Masa'ud da juwairiyya sai dariya suke mata har suka shiga had'adiyar unguwar nan ta masu kudin Lagos _Victoria island_ tafiya mai nisan gaske sukayi daga bisani suka nufi wani had'ad'e gida _gate_ d'in gidan kadai abin kallo ne _horn_ masa'ud yadanna bayan kamar _5 minutes_ gate d'in ya bude yadanna hancin motarsa yana shiga _securities_ suka taso saida sukayi _checking_ d'in motar masa'ud daga bisani suka barsu shiga gate na biyu saida bai kai tsaruwa na farko ba Haleesa sai zarar ido take tacigaba da kallon inda masa'ud yadosa wani karamin _parkin space_ yanufa yayi parking cikin zuciya Haleesa tace wannan shine na ba'ki a hankali ta mayarda idanu ta wurin k'aton _parking space_ mai d'auke da tsalatsala motoci lullube cikin _tenfold_ Haleesa bata sha kallo ba saida suka shiga cikin _main parlour_ gidan wata munmuna mata suka fara cikin karo da ita tana sanye da _black colour mini skeet da farar Riga gashi kanta lullube da attachment da sauri ta nufo waje su ta kar6i warmer d'in hannu masa'ud tanufi cikin wani karamin parlour yayinda su Haleesa suka Mara mata baya_
Kujera ta nuna musu masa'ud ne kadai ya zauna Haleesa da juwairiyya sukayi tsaye suna jiran matar tadawo ta kar6i Warmer's d'in hannu su........
[28/08 9:55 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```29```

Bayan matar mai kirar katti tazo ta kar6i Warmer's d'in sannan su Haleesa suka zauna bayan tadawo tace da su madam na zuwa tajuya ta koma inda tafito, a hankali madam Heendu take taka matakala bene fuskarta tadauke da murmushin da ke baiyanar da farin cikinta nagani bak'inta{visitor's} 'kamshin turare ta yadaki hanci Haleesa da sauri tad'aga kai ta dube ta kyakyawar fara mace kamar kata6a fatarta jini yafito kamanu matar kadai ya Haleesa ta kalla tagano cewa balarabiya ce tana sanye da tsadadiyar _combination shahada da material d'inki Senegal wuyanta yasha gold kirar Dubai_
Tana k'arasa shigowa _parlour_ masa'ud da juwairiyya suka mik'e tsaye gani Haleesa tak'i

mik'ewa tsaye yasa juwairiyya ta galla mata harara dole Haleesa ta tashi tsaye madam Heendu ta rungume juwairiyya ta sunbace kumatu ta hagu da dama tajuya wurin Haleesa ta rungumo ta ta sunbace ta kamar yadda ta yiwa juwairiyya a zuciya Haleesa tace kutt yau kuma ga wata sabuwa bidi'a cikin girmamawa masa'ud da juwairiyya suka kwashe gaisuwa dole Haleesa tayi yadda ta ga sunyi daga bisani madam Hindu ta zauna sannan suma suka zauna a zuciyar Haleesa tace kai jama'a duniya ina za ki damu _kudin bala'i ne ita wannan ba matar President ba ba kuma matar governor ba amma don tsabar girmamawa sai ta zauna mutane suke zaunawa_ ta dube Haleesa tana murmuahin ras-ras gaban Haleesa yafadi domin tayi mata kama da wata halitta da ta6a gani kafin ta lala6o inda ta ta6a gani mai irin kamanu madam Hindu sai ta ji sautin murya madam Hindu tana cewa juwairiyya amma wannan sister ki ne" koh"?
Juwairiyya tace eh madam Hindu tace saidai tafi ki kyau 'yan mata ya sunan ki Haleesa ta hadiye yawu da kyar tace......

```DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S ```

Jeddah Aliyu🌹
[29/08 8:09 pm] Jeeddah Aliyu🌹: [29/08 12:13 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```30```

"Sunana Haleesa, _madam Hindu_ tace sunanki mai dad'i har yaso yafi na Juwairiyya dad'i tak'arasa magana cikin dariya Juwairiyya tayi murmushin tace _Allah mommy nima sunana yana dad'i_
Nima bance sunanki bai dad'i ba Juwairiyya amma na Haleesa yafi dad'i saidai matsala Haleesa bata magana.
Juwairiyya da masa'ud suka kyalkyale da dariya, Janet ta shigo hannuta rike da _tray_ da kwalaye _juice a sama had'e da glass cups ta ajiye bisa stool ta tsiyayawa su juwairiyya Haleesa ta kar6i cup d'in_ tana jujuya shi yayinda suka cigaba da firar su Haleesa kanta na sunkuye tana saurare firar tasu, tsawon _2 hour's_ suka share suna fira daga bisani masa'ud ya mik'e tsaye yace madam bara mu barki ki huta sai gobe insha Allah zan shigo mu yi magana akan wance _Issue_
_alright_ masa'ud ba matsala sai ka zo Amma Haleesa nan za Ku barta ta tayani fira ko bara ki zauna ba Haleesa"?
```

Madam Hindu tak'asara magana had'e da duba fuskar Haleesa a tsorace Haleesa tad'ago tana kallon madam Hindu karaf Juwairiyya tace za ta zauna mana, Haleesa ta sada kai k'asa jin takeyi kamar tafasa ihu akan wane dalilin aunty Juwairiyya za ta yanke wannan hukunci akaita, gani yadda Haleesa tayi shiru yasa madam Hindu tace anyya Juwairiyya Haleesa za ta zauna kuwa saboda naga ta sada kai k'asa"?
Da sauri Haleesa tad'ago murya ta na rawa tace zan zauna _Mommy_
Juwairiyya tasaki ajiyar zuciya saboda tasan halin Haleesa sarai za ta iya cewa ba za ta zauna ba, madam Hindu tana dariya tace shikenan juwairiyya Haleesa ta 'kwace miki fada a wurina, a wannan karon masa'ud ne yabata amsa ta hanyar cewa madam in dai Haleesa ce ba ki kama kowa ba saboda za ki yini guda cur da ita batare da kin ji muryar ta.
Madam Hindu tayi murmushi mai sauti tace "wai haka ne Haleesa"?
Girgiza kai Haleesa tayi  madam Hindu tayi dariya had'e da cewa masa'ud Haleesa ta karyata zance ka don haka ja matarka Ku tafi gaba d'aya su suka kyalkyale da dariya daga bisani madam Hindu tace ina zuwa ta haura bene{upstairs} Da sauri Haleesa ta dube juwairiyya da masa'ud da alamar fad'uwar gaba a tattare da ita cikin sar'kewa halshe tace aunty Juwairiyya kuna nufi a gidanan za Ku barni"?
Kafin su bata amsa su ka ji tak'on takalmi madam Hindu hannuta ri'ke da katuwa Leda fara ta mik'awa Juwairiyya, yayinda juwairiyya ta du'ka tayi godiya Haleesa na kallonsu suka fice daga falon.
Cikin zuciyar Haleesa tace wannan wane irin d'aye hukunci ne"? ni bansan wannan matar ba kuma mutane nan sun tafi sun barni tare da Ita in muguwa ce fa"?
A tsorace Haleesa tad'ago tana duba madam Hindu da ke zaune a two Star hankalinta na wajen tv Haleesa taji wani matsananci faduwar gaba, saurtin murya madam Hindu ce tadawo da Haleesa daga natsuwarta sakamako kwadawa Janet kira da tayi da cikin tafiyar sauri Janet ta'karaso d'auke da _Warmers d'in abinci da Juwairiyya ta zo da shi ta ajiye tayi saving  madam tasauko k'asa ta zauna bisa center carpet_
Ta dube Haleesa tace Haleesa zo mu ci abinci cikin sanyi murya Haleesa tace na koshi mommy"
"Madam Hindu tayi murmushi tace ina matuk'ar jin dad'i abincin Juwairiyya ta iya girki sosai ina fatar kema kin iya domin kwarewa da iya girki shine mace"?
Haleesa tayi murmushi had'e da cewa nima ina d'an k'ok'artawa
 To ki k'ara bada himma domin iya girki yakansa mace tasami babban matsayi a zuciyar mijinta kinga ni nan lokacin da maigidana yana raye muna da _chef_ kuma kwarare ne sosai a fagge sarafa abinci amma Sam bana bari sa ya girkawa maigidana abinci ni nake girka masa da kaina, wasu lokuta a wurin _chef_ d'in nake koyo wasu girke-girke.
Har madam Hindu ta dasa aya a zanceta Haleesa tana kallonta daga bisani Haleesa tayi murmushi had'e da cewa _Allah yajikansa ya gafarta masa_
Ameen madam Hindu tafad'a had'e da ture _plate_ d'in gabanta
A zuciyar Haleesa tace ikon Allah matar nan nada saukin kai kalli yadda take bani labari abunda bai shafeni ba  haka madam Hindu tacigaba da Jan Haleesa da fira sai ga Haleesa tasaki jikinta har da su tintsira dariya.......
[29/08 5:30 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```31```

```DARE```

Zuwa wannan lokacin Haleesa ta zama 'yar gida yadda tasake da madam Hindu tamkar ta shekara da sanita, sai misali 'karfe 10:00pm madam Hindu ta kai Haleesa _bedroom_ d'in da za ta kwanta madam Hindu ta dube Haleesa fuskarta d'auke da murmushi tace Haleesa ga d'akin Hannah ki kwanta saboda nasan za ki fi sakewa anan fiye da nawa d'akin ki bud'e _wardrobe_ akwai _sleeping dress_ na Hannah kiyi amfani da su in kina bu'katar wani abu sai ki sanarda ni. Haleesa tayi murmushi tace na gode mommy
"Madam Hindu tafad'd'a murmshinta tace miye kuma abin godiya Haleesa"?
Ni fa na d'auke ki tamkar 'yar da na Haifa ki kwata ki yi bacci don naga alama agajiye kike sai da safe ta'karasa magana had'e da juyowa Haleesa k'ofa, Haleesa tajuya wurin k'ofa ta Murza _key_ a hankali takarewa d'akin kallo tasauke ajiyar zuciya mai k'arfi gaske, ta bud'e _wardrobe_ta tsurawa Jarin kayan da ke ciki ido cikin zuciyarta tace mai kudi yaji dad'insa yanzu duk  tuli tufafi nan na mutum d'aya ne _infact_ yarinya bata ma gida tana school amma ta tara wannan uban kaya, tabe baki tayi daga bisani tajuya _side d'in da jarin sleeping dress suke tad'auki wata cotton night gown_ tasanya tasauka mata har k'asa da alama mai rigar tafita tsayi nesa ba kusa ba, Haleesa ta yatsine fuska a zuciyarta tace in banda kar mommy ta ga nak'i bin umurni ta da ba abunda zai kai ni saka kayan wani, ta kashe wuta ta haye gado bayan tayi addu'a ta janyo _blanket_ ta lullube rabin jikinta sanyi Ac ya ratsata, ta lumshe idanuta ta tsunduma tunani yaya Habeeb yayinda hawaye suka ziraro mata ta gefe da gefe idonta suka sauka bisa wuyanta tsawon lokacin tadauka tana kuka had'e da tunani rayuwata da yaya Habeeb daga har bacci ya kwashe ta.

```WASHE GARI ```

Sai misali k'arfe 7:15am Haleesa ta falka da sauri tafad'a _bathroom_ tayi tsaye tana kallon tsarinsa daga bisani ta karanta rubutu da ke jikin kan famfo ta bud'e  na ruwan sanyi tayi alwala tana gama sallah tsawon lokacin tadauka tana yi ma yaya Habeeb addu'a tana shafawa tak'ara komawa bisa gado, tacigaba da baccinta sai _around 11:20am_ tafalka batare da 6ata ba tashiga bathroom tayi wanka tana fitowa ta mayarda kayanta ta D'an Shafa _lotion_ had'e da goga 'yar _powder a face nata_ tadauki _body spray_ mai sanyaye k'amshi tafashe jikinta,ta bud'e k'ofa tafice madam Hindu ta tsinkaya zaune bisa katafare _dining table mai d'auke da 8 chair's_
Tana _breakfast_ Haleesa tak'arasa waje ta madam Hindu nagani ta tasake mata murmushi.......

```DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S```

Jeeddah Aliyu🌹
[29/08 8:10 pm] Jeeddah Aliyu🌹: [29/08 6:56 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```® NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```32```

Haleesa ta duk'a ta gaisheta ta hanyar cewa ina kwana mommy"?
Madam Hindu ta mik'e tsaye ta rik'o Haleesa had'e da rungumeta tace lafiya qalau Haleesa ya bak'unci"?
Murmushi Haleesa tayi tace mommy ae na zama 'yar gida
Saida mommy tayi dariya sannan tace da kyau Haleesa 'yar gidana mommy haka nakeso oya zauna ki yi _breakfast_ Janet da ke tsaye a gefen kamar _bodyguard_ da sauri ta ja ma Haleesa kujera ta, zauna daga bisani tayi _saving nata_ ta ajiye mata plate d'in gabanta Haleesa ta dube plate mai d'auke da _chips da fried plantain with source_
A hankali Haleesa take ci abincin nata, tana korawa da _tea mai kauri gaske yaji Ovaltine_
Madam Hindu tariga ta k'arewa don haka ta mik'e tsaye tace Haleesa in kin gama ki same ni a 'karamin _parlour_
Kai kawai Haleesa tad'aga mata saboda ta cika bakinta da _fried plantain_ saida Haleesa ta ji tayi katt tayi gatsi had'e da hamdallah rabonta da taci abinci ta ji ta 'koshi irin haka tun kafin yaya Habeeb yarasu ta mik'e tanufi _parlour_ tararda madam Hindu a zaune hannuta ri'ke da _magazine_ tana dubawa Haleesa tanemi _one star_ ta zauna madam Hindu tad'ago ta dubeta tace har kin gama Haleesa"?
Haleesa tad'aga kai"
Baki da buk'atar komai"?
Haleesa tak'ara d'aga kai murmushi madam Hindu tayi tace har yanzu da raguwar bak'unta a tare da ke, Haleesa ta sada kai k'asa tana dariya _driven madam Hindu ne yashigo ya rusuna ya kwashe gaisuwa_
Madam ta amsa tana murmushi tace Aderwale ya akayi ne"?
Madam kudin _fuel_ na zo kar6i mota batada _enough fuel_
Madam Hindu tajuya wurin Haleesa tace Haleesa tashi ki je _upstairs bedroom d'ina ki bud'e brown colour handbag a gefen bed akwai kudi ki dauko min bundled d'aya_
Haleesa ta mik'e ta haura _stairs_ a hankali kaitsaye tanufi d'akin "with full confidence ta
```

murd'a handle" kutt! k'ofar ta bud'e 'kamshin turare "intense man da yahadu da sanyi Ac yad'aki hancinta ta lumshe idanuta tsawon 20 second's ta dauka idanuta na rufe daga bisani ta bud'e su ta shak'i k'amshin yaratsa _brain nata_ tasauke ajiyar zuciya sannu a hankali tafara taka 'kafarta idanuta suka hasko mata _brown hangbag colour_ ajiye a gefen _bed_ har ta mik'a hannuta ta zuge zip d'in karaf idanuta suka hango mata shi yana kwance yayi "pillow da hannaye shi yana sharar bacci abinsa, da kallon yanayi baccinsa kasan yana cikin kwanciyar hankali, Haleesa ta murza eye's nata ta kuma rintsi su ta bude tak'ara kallon bed still yana nan yadda tafara ganishi numfashinta ya yi sama yadawo k'asa tadafe k'irjinta a zuciyarta tace tabbas idanu na ba 'karya suke ba babu shakka wannan Handsome ne ya akayi yasan nazo Lagos har yabiyoni"?
Wayagaya masa ina gidanan"?
Ya akayi naganshi akan bed d'in mommy yana bacci"?
anyya kuwa "Handsome ba aljani bane"?
Saboda in banda aljani ba Wanda zai aikata wadanan abubuwan....
[29/08 8:09 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```33```

Wani mashahuri tsoro ya lullube ta jikinta na rawa ta fara ja da baya garin baya-baya 'duwawu ta suka bige _dressing mirror_ kwalba turare yafado ta daki tile's tafashe a razane ya tashi zaune yajuyo ya tsurawa Haleesa _sexy eye's d'insa_ masu matuk'ar tsoratarda mai kallonsu, Haleesa ta'kara firgita ta zare ido kallon-kallon suke yi wa junansu _eye's ball's_ d'inshi masu kama da na magge sukayi masifar firgita Haleesa tsanani tsoronshi ya mamaye ta, tanaso tajuya ta arce na kare amma takasa cikin firgici had'e da gigita Haleesa ta bud'e bakinta ta dagargaje iya k'arfinta ta kwatsama ihu _wayyo Allah aljani wayyo mommy aljani mai idon magge a d'akinki_
Gaba d'aya gidan yadauki amo sautin muryarta tamkar da "microphone takeyi sa da sauri yasaka yatsu zara-zara yatsunshi, doshe kunnenshi, kamar daga sama madam Hindu taji Murya Haleesa tana ihu had'e da kwada mata kira a razane ta take haura _stairs_ idanuta a rufe tashigo d'akin da k'arfi tajuyo da Haleesa tana, facing d'inta har zuwa lokacin Haleesa ihu take tana kira wayyo mommy aljani mai ido magge, girgiza ta mommy tayi da kyar Haleesa tayi shiru yayinda Madam Hindu tace menene Haleesa me kike yi wa ihu"?
Wallahi mommy shine aljani mai ido magge ga shinan zaune akan, bed d'inki, dube idanu shi mommy Allah na magge ne.
Sai lokacin mommy ta kai dubanta bisa bed yana zaune ya langwashe k'afafu shi hannaye doshe a kunnenshi, madam Hindu tayi murmushin mai sauti gaske tace Haleesa kalle shi ki gani ba aljani bane mutum ne.

Ihu Haleesa ta'kara kurmawa cikin zafin rai da tafarfasa zuciya yasauko ya tunk'aro waje Haleesa wance ke ta faman zunduma ihu yadaka mata rikitaciya tsawa _hey! Shut up just shut up!_
Yadda ya yi ihu yahdassawa jijiyoyi Kansa da na wuyanshi tashi fuskarsa tayi jajir alama tsanani bacin rai nan take Haleesa ta hadiye raguwar ihunta, talafe a jikin mommy had'e da chuikuikuye ta
"Madam Hindu ta dinga bubuga bayanta tace Haleesa wannan ba aljani bane d'ana ne sunanshi Habeeeeb......

```DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S ```

Jeeddah Aliyu🌹
[31/08 7:48 pm] Jeeddah Aliyu🌹: [30/08 12:29 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```34```

Numashin Haleesa ya tsaya "chak ta d'auki tsawon 4-5 minutes tana nazari daga bisani ta zare jikinta daga jikin madam Hindu, tajuya ta dube gefenta "still yana tsaye hannaye shi zube cikin aljihu wando "Jean's d'in da yake sanye da shi karaf sukayi 4 eye's yadankara mata harara Haleesa ta'kara d'imaucewa ta runtsi idanuta gam madam Hindu tarik'o hannaye ta ta girgiza ta cikin sigar rarrashi tace _come on Haleesa open ur's eye's look at me_
Da kyar Haleesa ta bud'e eye's nata ta tsurawa madam Hindu idanu.
Haleesa kidaina tsoro shi mutum ne _He is my son Habeeb, u can call him yaya Habeeb Co's He is urs brother_
Haleesa ta'kara rud'ewa ta rikice iya rikicewa "she can't believe abunda madam Hindu take fad'a sai kawai tafashe da matsananci kuka cikin murya kuka tafara magana _No mommy dis is not my yaya Habeeb, yaya Habeeb is gone He is death_ ta'karasa magana had'e da sakin matsananci kuka mai ratsa zuciyar mai karatu, madam Hindu ta firgita da gani wannan hali da Haleesa tashiga ajiyar zuciya tasaki yayinda goga naku yana gefe yana aikawa Haleesa kallo mai cike da tsana wani wawa tsoki yaja yafisgi handle ya bud'e k'ofa yafice daga d'akin zuciyarsa na tafarfasa kamar, ruwan zafi a "kettle.
madam Hindu ta duk'a gaban Haleesa wance take dur'kushe a k'asa tana kuka kamar ranta zai fita, ta rungume ta Haleesa tace mommy yaya Habeeb ya mutu yatafi ya barni, narasa farin
```

cikina banida saura jin dad'i a rayuwa mommy yaya Habeeb shine bugun numfashina banida Wanda zai so ni yabani farin cikin da yaya Habeeb yabani"?
Saboda haka mommy kidaina kiran wannan mai ido magge da sunan yaya Habeeb shi ba yaya Habeeb bane madam Hindu tarasa mafita sakamako yadda kalamai Haleesa suke sauka a kunnenta saida ta jajirce ta hanyar kawarda tsantsa rud'ani da take ciki tace kidaina kuka Haleesa kuka baya magani komai saida yak'ara jefa D'an Adam cikin wani hali, kiyi tawakalli a yanayi da kika riske kanki a ciki kowane tsanani yana tare da sauki matuk'ar kika jinginar da al'amura ki a wurin Allah{s,w,t} sai ki ga yayi miki sauyi da abunda baki ta6a tunani za ki samu a rayuwa bansan labari rayuwarki ba Haleesa amma da gani yanayi da kika shiga a yanzu na tabbata akwai, 6oyayye al'amari mai matuk'ar ban tausayi a tare da ke.
Haka madam Hindu tacigaba da rarrashin Haleesa da kalamai masu dad'i har tayi nasara shawon kanta tadaina kuka, saidai kuma zazza6i mai zafin gaske yarufe ta sai rawar sanyi take madam Hindu ta tashe ta tsaye a gefen bed ta zaunarda ita _panadol extra dauko tabata tasha daga bisani tace kwanta kiyi bacci Haleesa da kin falka za ki ji ki normal_
Haleesa ta bi umurni Madam Hindu ta kwanta domin ita kanta tana buk'atar kwanciya musanmman yadda kanta yake sarawa kamar zai rabu gida biyu, madam Hindu ta lullube ta da blanket ta kashe mata Ac had'e da ja mata k'ofa tafice, Haleesa ta lumshe idanuta kamar mai bacci tasoma backwards d'in kalamai mommy a firgici ta mik'e zaune sai yanzu ta fahimce inda kalamai mommy suka dosa tanufi mai idon magge d'anta ne sunanshi Habeeb, tadafe goshi cike da zullumi ta koma ta kwanta tana tunani makomar rayuwa ta anan gaba da haka har bacci ya sace ta.........
[31/08 7:48 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```35```

Direct 'karamin parlour madam Hindu tanufa zuciyarta cike da tausayi Haleesa, kwance yake akan _3 star_ ya hard'e k'afafushi a wuri d'aya madam Hindu ta tsaye tana kallonshi daga bisani tayi murmushi tadauke kanshi ta aza bisa ciyoyinta, a hankali take shafar sumar kanshi tace son yaushe ka shigo gidanan"?
Idanushi na lumshe cikin muryarshi mai matuk'ar dad'i yace _around 8:00 o'clock_
Madam Hindu ta tabe baki tace kai dai har abada ba za ka daina halinka"
Ya gyarar kwance shi ya kuma bud'e idanushi cikin shagwa6a irin ta sagartatu 'ya'ya yafara magana "please sweetheart bacci zan yi wance mahaukaciya 'yar aiki taki ta hanani bacci ke kuma mommy kinfara 'korafi akaina Allah za Ku haddasa min "headache
"Humm ba headache ba anything zai iya kama ka saboda ka k'i aure da kanada iyali ba Wanda zai dinga hanaka bacci please son ka manta da rayuwarka ta baya tsawon shekaru biyar da rasuwa salma ka kasa mantawa da ita ka daure kanemo life partner kai ma za ka fi jin dad'i.

I told you hundreds time's mom ki nemo duk wance tayi miki ki aura min Co's I don't have choice koda Janet kika ce na aure zan amince saboda banida za6i da yawuce naki yak'arasa magana had'e da Jan karan hancinta.
Madam Hindu ta buge mishi hannu tace  "God forbid me za kayi da Janet"?
In har mom d'ina za ta sonta nima zan so ta kinsan duk abunda kike so nima ina sonshi.
"Look son I'm tired da wadannan kalamai naka kullum nayi maka zance aure sai ka buge da yi mini dad'in baki na tabbata da mahaifinka yana, raye da ba zai fad'a ka k'i ji farin cikina shine kayi aure Habeeb ka manta da kata6a rayuwa da salma.
"Mom please stop saying dat koda ace Dad yana raye ko ba ya raye I'm ready to follow urs instructions saboda ke mahaifiyata ce I'll do anything just to make you happy"
Madam Hindu tayi murmushi jin dad'i tace I know Son za ka iya yi komai akaina, baka ta6a sa6awa umurni na shiyasa nake alfahari da haihuwarka.
Habeeb yasaki tsad'ad'e murmushinsa kumatushi  da k'asan geme shi suka lotsa yad'ago ya sumbace kumatu mommy yace "I love you mom
Madam Hindu tana murmushi ta mayar masa da cewa "I love too son.
 Habeeb yak'ara shigewa jikinta tamkar k'aramin yaro
madam Hindu tace son!
A sanyaye yace"Humm!
Haleesa ta yi matuk'ar bani tausayi 'I think akwai wani babban al'amari a tare da ita har madam Hindu ta dasa aya idanushi na lumshe batare da ya bud'e su ba yace wacece da wannan sunan"?
Ita ce yarinya da na baro a bedroom"
"Humm mom karki d'auki damuwa 'yar aiki kisaka a ranki saboda nasan halinki da mayarda damuwa wani naki'
Saida madam Hindu tasaki ajiyar zuciya daga bisani tace Habeeb Haleesa ba 'yar aiki bace k'anwar juwairiyya matar masa'ud manager ce nan take, madam ta kwararo masa labari dalilin zaman Haleesa a gidanta tacigaba da cewa inaso nasan labari rayuwar Haleesa musanmman a yadda naji tana kiran sunan yaya Habeeb zan so nasan waye Habeeb a wurinta.
Habeeb ya yatsine fuska kamar ya ga kashi yace ki tambaye ta mana ni miye nawa a ciki"?
Cike da jin haushi madam Hindu ta shafi fuskarsa tace babu dama kai damuwa wani ba zai ta6a zama naka ba.
Habeeb ya yi murmushi had'e cewa tun da kinsan haka mom ki kyale ni nayi bacci,
Shikenan son na kyaleka kayi baccinka Habeeb ya lumshe idanu bai dogon lokacin ba yayi bacci yayinda madam Hindu tasoma tunani rayuwarta da ta gudan jininta Habeeb......

```DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S ```

Jeeddah Aliyu🌹
[04/09 3:34 pm] Jeeddah Aliyu🌹: [02/09 10:23 am] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣
```

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```36```

```WANENE HABEEB???```

Late Alhaji Majeed lamido haifafe garin Adamawa jahar Yobe, ne sanane mai kudin da yayi tashe tun duniya tana zaune qalau, marigayi Alhaji majeed lamido ya mutu yabar tarin dukiya da 'ya'ya bila adadin rankatakan family majeed lamido babu talaka domin sun gaji dukiya mai tarin yawa daga gurin mahaifinsu Muhammad lamido yana d'aya daga cikin 'ya'ya marigayi majeed lamido mahaidiyarshi su biyu kacal ta haifa tarasu, a lokacin da majeed lamido ya mutu aka rabawa 'ya'ya shi tarin dukiyar da yabar musu a matsayin gado tun lokacin da aka raba musu gado muhammad yaduk'ufa wurin juya dukiyar shi ba abunda yasaka a gaba sai neman kudin Wanda a cikin d'an k'an'kani lokacin ya gawurta yayi fice ya yiwa sauran 'yan uwanshi zarar, Muhammad lamido ya mallaki "companies dama arewa da kudanci Nigeria yana da gidanje sayarda man fetur bila adadin shine mamallaki Majeed Lamido Airlines yana da hannu jari da dama a companies na k'asashe waje yana da gida a Abuja da Lagos tsanani neman kudin Muhammad yasa yad'auki dogon lokacin batare da ya aje iyalin ba, burin Muhammad shine ya aure mace mai matuk'ar kyau garin neman duniyarshi ya hadu da Hindu a Egypt tun daga lokacin da daura idanushi akanta yadauki son duniya yadaura mata kasancewarta kyakyawa Hindu ita ce 'ya ta farko wurin iyayyeta sai k'annanta biyu maza Ahub da Ansar da farko da ta gabatarda Muhammad a wurin iyayyeta k'in amincewa sukayi da shi acewarsu bak'ar fata ne saida takai ruwa rana da su sannan suka barta ta aure Muhammad, saida Hindu tayi shekara bakwai da aure sannan tasami cikin Habeeb cikin Hindu na da wata tara chin ta haifi Habeeb daga ita har Muhammad suna matuk'ar son Habeeb tamkar numfashinsu suna nuna masa gata shiyasa Habeeb yatashi a sagarce babban matsala Habeeb rashin magana da farko iyayye shi sun dauka ko kurma ne sai daga baya suka fahimce cewa, tsabar miskilanci ne yayi masa yawa, Habeeb bashida, aboki koda yaushe za ka tararda shi manne da mommy shi ba, abunda Habeeb yasani daga Daddy shi sai mommy shi duk wannan gata da Habeeb yasamu Muhammad da Hindu basuyi sake da karatunshi Habeeb yanada 10yrs a duniya Hindu tak'ara haihuwa tasami 'ya mace mai suna Hannah.

Habeeb na gama primary school Muhammad yatura shi Egypt wurin iyayyen Hindu yayi karatun secondary school d'inshi a lokacin da ya gama secondary school yadawo Nigeria D'an zaman da yayi a Adamawa kafin yatafi university shak'uwa mai 'karfi tashiga tsakaninshi da salma 'yar k'ani Alhaji Muhammad da suke uba d'aya, salma ta girmewa Habeeb da kusan 3-4yrs duk lokacin da salma taga Habeeb sai tayi ta tsokanarshi ta hanyar kira shi da suna kurma ko mai idon magge tun Habeeb baya kulata har yadawo bashida friend in ba salma ba tsanani sha'kuwar da Habeeb yayin da salma ta karanci halaye Habeeb shiyasa k'awance su yadaure, a lokacin da Alhaji Yusuf majeed lamido zai tura salma da''yan uwanta karatu a London salma na bawa Habeeb labari shima yayi tsalle yadira yace sai _Oxford university London_ zai yi karatun degree d'inshi kaitsaye Alhji Muhammad ya amince Habeeb da salma da kuma saura
```

'yan uwata suka d'aga London.
 watani suka wuce shekaru suka shud'e cikin nasara Habeeb da salma suka kamalla karatun degree d'insu suka dawo gida Nigeria.
Yayinda Muhammad ya mik'a ragamar alhakin kula da dukiyarshi a hannu Habeeb, tun daga lokacin Habeeb yadawo tamkar ya shi baisan komai ba sai neman.
Kwatsan Alhaji Muhammad yatashi da rashin lafiya kwanasa biyu a hospital yarasu Hindu da Habeeb sun shiga tashin hankali, saida basuda yadda za suyi illah suyi hank'uri gani yadda aiyuka suka yiwa Habeeb yawa yasa Hindu take tayasa, kula da wasu _companies_ nasu gudun kada su duk'ushe  sunan madam yasamu asali ne a duk lokacin takai ziyara a company sai kaji _worker's_ suna kiranta da madam shikenan sunan yabita.
Madam Hindu mace ce mai sauki kai ga ri'kon Addini, tanada matuk'ar tausayi tana tsanani son 'ya'yanta musanmman d'an gaban goshi Habeeb akanshi za ta iya 6atawa da kowa shima Habeeb abin haka yake a wurinshi yana matuk'ar girmama mommy shi yana so duk abunda takeso yana taka tsan-tsan da duk wani abunda zai 6ata mata rai.....
[02/09 6:59 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

          ```37```

Habeeb farin ne tass skin d'inshi har wani ja-ja takeda yanada tsawo sosai har wani d'an rangwafawa yayi fuskarshi, na dauke da dogon hanci yanada manya idanu eye's ball d'inshi kamar na magge sumar kanshi bak'a wulik yanada saje a gefen kumatu shi sai wani d'an siriri geme kamar na _2face_ duk lokacin da yayi murmushi kumatushi da k'asan geme shi na lotsawa{dimple} Habeeb bashida fa'ara ko kad'an koda yaushe fuskarshi a murtuk'e take da kyar ka ga Habeeb ya yi dariya, shiyasa mutane da dama suke masa kallon a matsayin mai girman kai.
Matsala ta farko da salma tafara fuskanta tun dawowarta _Nigeria_ shine rashin takameme mijin aure mutum d'aya ke so ta da aure shine salis saida matsalar salis shaye-shaye  ba abunda baya sha a dangin kayan maye, duk da kasancewa salma kamila zama London bai chanza mata, kyawawa dabi'u ta ba salma akwai addini Sam bata wasa da lukutan sallah salma fara ce irin farin Fulani Adamawa gajeriya ce batada tsawo ko k'adan akwai hips da manya boobs tanada k'iba sosai wance mutane da dama suke tsanmani ko salma bazawara ce batada hayaniya akwai hank'uri ta iya zama da mutane, duk da wad'annan kyawawan halaye na salma amma tarasa dalilin da yasa mijin aure yagagareta.
A dalilin wannan matsala ta salma yajanyo mata matsananci bak'in jini a wurin iyayyeta daga haj khareema har Alh Yusuf kullum cikin yi mata gorin suke shiyasa k'annanta suka rena ta.
Salma kwance a room d'inta abin duniya yataru ya yi mata yawa ita kanta a yanzu tana buk'ace da abokin rayuwa a halin yanzu takai mataki da ba za ta iya kare kanta dalilin da yasa wata

rana ta kira Habeeb domin yabata shawara cikin shasshekar kuka ta kwashe irin wulaqanci da take fuskanta, daga wurin haj khareema da k'annanta tafad'awa Habeeb, har ta dasa aya Habeeb na kallonta daga bisani yasauke ajiyar zuciya cikin sigar rarrashi yafara magana, hank'uri za ki yi aunty salma komai ya yi farko yanada 'karshe da ina da magani magance wannan matsala taki da tuni na nemo shi duk da haka zan cigaba da tayaki addu'a har Allah ya kawo miki k'arshe wannan matsala salma tace na gode Habeeb, dama na kira ne domin na sanarda kai zan amince na aure salees saboda nima a yanzu ina da bu'katar aure salma ta'kasara magana had'e da rushewa da kuka da sauri Habeeb yarik'o hannuta, yace please aunty salma karki amince da aure salees saboda hakan zai iya haifar miki da matsala Sam bai dace da ke ba.
To Habeeb ya zan yi"?
Hank'uri za ki yi salma"
Ba zan iya ba Habeeb hank'uri na ya'kare banaso na jefa kaina a halaka, a kullum shekaru na 'Kara yawa suke in kuma kana gani salees bai dace da ni ba to kanemo min mijin aure.
Habeeb yasauke gwaron numfashi tsanani tausayi salma ya kanainaye shi, cikin rashin mafita yace shikenan aunty salma ki bani _time_ zan kawo miki Wanda yafi dacewa da ke, salma tayi murmushi had'e da cewa shikenan Habeeb na gode da wannan taimko naka agareni.
Dare ya yi Habeeb yakasa bacci sai faman juyi yake tsanani tausayi salma yahana shi bacci, ya kuma rasa Wanda zai nemo ya aure salma, tsawon lokacin yadauka yana nemawa salma Mafita daga karshe yasaki murmushi.
Washe gari kaitsaye Habeeb yanufi gidan su salma yana shiga gidan ya hadu da ita a compound za ta fita, bayan sun gaisa yace aunty salma na nemo miki miji amma bansan ko za ki amince da za6i na salma tayi murmushi tace Habeeb kenan ae ni na gaya maka banida za6i......

````DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S ```

Jeeddah Aliyu🌹
[04/09 3:34 pm] Jeeddah Aliyu🌹: [04/09 8:20 am] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```38```

yadda za'ayi muje ka rakani a hanya sai mu yi magana, Habeeb ya yatsine fuska yace ni fa banaso yawo, salma tayi dariya had'e da cewa kadai shiga mota mu tafi tun lokacin da suka
```

d'auki hanya Habeeb yake ta faman kame-kame ta wace hanya zai bi ya baiynawa salma mijin da yanemo mata daga bisani ya yi 'kundubala had'e da k'unar bak'in wake ta hanyar cewa aunty salma ina son ki saka fahimta a cikin wannan magana da nazo miki da ita ki gano cewa komai muk'addari ne daga Allah na zauna nayi nazari, ni nafi chanchanta da na zama aboki rayuwarki na har abada na amince zan aure ki aunty sal.....
Wawa birki da salma taka ne ya yi sanadi da Habeeb ya hadiye saura kalamai shi ta gangara gefen titi ta yi _parking_
Cikin yanayi mai d'auke da tsoro da mamaki take kallon Habeeb Sam bata amince da wad'annan kalamai da suke fitowa daga bakin Habeeb Lamido wai ita salma zai aura, da kyar salma tace Habeeb kasan abunda kake fad'a kuwa"?
Kwarai kuwa aunty salma kawai yanzu amincewar ki nake neman nan da d'an k'ank'ani lokacin matsalolinki sun zama tarihi.
Karka yaudare kanka Habeeb nima ka jefa ni a wasiwasi ni ba tsara aure ka bace I'm not your type Habeeb kada tausayi na, ya rinjaye zuciyarka daga baya ka dawo kana danasani marar amfani.
Auren ki ba zai ta6a jefani a danasani ba aunty salma ina tausayi ki ina da burin taimaka miki basan Inda zan je na nemo miki mijin aure ba, shiyasa na kawo miki kaina.
Dan Allah Habeeb kadaina fadar wannan magana, infact na girme maka ni ba tsarar aure ka bace in ka aure ni Habeeb ya za kayi"?
Kai yaro ne Habeeb ba lallai bane ka hango abunda nake hangowa cikin wannan al'amari salma ta'karasa magana had'e da share hawaye.
"I don't care all dis aunty salma don addini bai haramta ba kin girme ni so what's asalima ni sunnah zan yi domin kuwa Annabi{s,a,w} ya aure Nana khadeejat kuma ta girme shi karki kawo zance tazarar shekaru aunty salma kina kallona a matsayin yaro ba laifi, amma inason Kisani a yadda nake haka ba ke ba aunty salma kowace tafi ki shekaru zan iya sarafa ta.
Salma tazara ido tana duban Habeeb anyya kuwa, Habeeb bai zare ba iya sanita Habeeb baya shaye-shaye ballatana tayi tunani ko ya shawo shegiyar ne.
Tsawon _5 minute's_ salma tadauka tana k'arewa Habeeb kallo daga bisani, ta ya'ke zuciyarta ta hanyar furta ba zan ta6a amincewa na aure ka Habeeb domin nasan zan cutarda kai ne kawai nafi kowa sanin halinka nasan kalar mace da kakeso mallaka a matsayin matar aurenka _I'm not d one of them_ don haka mu yi closing wannan chapter banaso mu 'Kara tada wannan zance zan iya jure k'are rayuwata ba aure amma ba zan ta6a iya jure cutarda kai ba Habeeb.....
[04/09 8:20 am] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```39```

Haba! Aunty salma in har kika ce ba za ki amince ki aure ni ba, kin butulcewa ni'ema da Allah

yabaki ba addu'a da kike yi ne ba dare ba rana Allah ya tausayi miki yakawo miki ni a matsayin Wanda zai share miki hawaye ki amince da ni aunty salma nan da d'an 'kan'kani lokacin ki zama mallaki na.
Salma ta runtse idanu hawaye suka wanke mata fuska, wannan wane irin tausayi ta ne Habeeb yake ji"?
Cikin zafin rai salma tace Habeeb na 'Kare magana nace ba zan aure ka ba kuma kayi gagawa kafita min daga mota, Habeeb ya yi murmushi yace wai me kika d'auki kanki ne"?
Bansaniba fice min kawai daga mota Habeeb ya bud'e k'ofa yafita ya lek'a cikin motar yace na fita daga motarki aunty salma amma Kisani ba zan ta6a fita daga rayuwarki ba da k'arfi Salma taja mota ta tafi Habeeb ya bi motar da kallo tsanani tausayi salma na 'kara ratsa shi, salma batayi wani nisa ba tayi reverse tadawo wurin shi Habeeb yasaki murmushi domin yasan ba za ta iya tafiya tabar shi cikin bacin rai idanu ta sunyi jajir tace shigo mu tafi, Habeeb ya tabe baki cikin gadara yace ki tafi kawai"
Banaso iskanci Habeeb za ka shigo mu tafi ko kuwa"?
Kallon 'kasan ido Habeeb ya aika mata da sauri ta kauda fuskarta, ya bud'e k'ofa ya shiga ta'kara Jan mota suka d'auki hanyar gida Habeeb yace naga kin dauki hanyar gida kinfasa zuwa inda za ki je ne"?
Na fasa tafad'a kaitsaye har suka isa gida ba Wanda yak'ara magana suna k'arasawa salma ta balle k'ofa tafice da sauri tashiga gida, Habeeb ya shafi sumar kanshi, yasoma tunani 'kalubali da yake tunk'ara tabbas tun nayi niyar magance miki matsalarki ba abunda zai sanya na sauya ra'ayi na.

```BAYAN SATI D'AYA ```

Tsawon wad'annan kwananki Habeeb bai k'ara neman salma ba sai kawai salma tayi tunani sabul da baka ne ya yi domin tasan ba abunda zai yi da ita,
Kasancewar duk 'karshen wata {month} "family majeed Lamido kwai su da kwarkwata suna had'uwa a family house domin gudanar da family meeting kallo d'aya Habeeb ya yi wa salma ya kauda fuska, bayan  an gama meeting d'in Habeeb yace yana da magana nan take yafara kwararo zance ina son nayi amfani da wannan damar domin in sanarda ku abunda yake faruwa tsakanina da salma gaba d'aya nutane da ke wurin suka d'ago suna masa kallon mamaki yayinda Habeeb yacigaba da cewa ni da salma mu kasance muna tsanani son juna saidai Salma tace ba zata aure ni ba saboda tafi ni yawan shekaru, gaba d'aya parlour yadauki surutu mutane da kyar sukayi shiru salma ta sada kai k'asa tana sharar hawaye domin tasan Habeeb yana yunkuri d'aukar Dala ba ganwo, bayan dogon sarhi da kace-nace da yabiyo baya, daga bisani babban d'a marigayi majeed Lamido da ke matsayin kamar uba a garesu kuma duk abunda yafurta ya zaunu yace, aje anemo masa dabino nan take yadaura auren Habeeb da salma ya kuma biyawa Habeeb sadaki, shi kanshi Habeeb ya girgiza da wannan hukunci na Alhaji Bello lamido, domin so ya yi sai ya sanarda madam Hindu yanzu me zai ce da ita saidai kash aikin gama yariga ya gama bakin al'k'alami ya bushe tun lokacin da aka watse meeting salma tanufi gida, tashige room d'inta tana aikin kuka domin tasan Habeeb ba sonta yake ba kawai dai tausayinta yakeji, batasan yadda za tayi da k'anwarta Maryam da ke masifar son Habeeb tana cikin wannan tunani Hajiya khareema da Maryam suka shigo kowane su fuska a
```

had'e Maryam ce tafara magana cikin muryar kuka kin cucu ni aunty salma kin rabani da yaya Habeeb wane boka ne kika samu da ya yi miki asirin da kika mallaki zuciyar yaya Habeeb"?
Salma tad'ago idanu ta taf da kwalla tace boka kuma ni me yahadani da boka"?
Ke! Hajiya khareema tadaka mata tsawa kin shiga uku salma dama tsawon wannan lokacin da kika dauka k'unshe a d'aki ashe kina nan kina sak'a burin da yafi 'karfinki ke banda abin kunya ina kuda balle rumo sa ina ke ina Habeeb"?
Salma ta'kara fashewa da kuka Hajiya khareema ta ri'ko hannun Maryam tace zo mu tafi Maryam duk tsutsu da yakira ruwa shi ruwa kan doka.
Tabangare Habeeb kuma da kyar yasamu madam Hindu ta amince da salma acewarta sam salma bata dace da shi ba amma tunda yaji yagani shikenan, bayan kwana biyu da daura aurensu Salma ta tare gidan Habeeb, saidai wani abin mamaki da salma taci karo da shi.....

```DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S ```

Jeeddah Aliyu🌹
[04/09 3:34 pm] Jeeddah Aliyu🌹: [04/09 11:57 am] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```40```

Habeeb gudunta yakeyi tsawon sati ta d'aya da tarewa a gidanshi amma bata saka shi a idanu ta ba, gani wannan ba zai zame mata mafita, a wani dare takasa ta tsare Habeeb na shigowa cikin sand'a kamar barawo yashige da'kinshi tana la6e tana kallonshi, saida ta tabbatar da yashiga bedroom d'inshi ta Mara masa baya tana shiga yana fitowa daga wanka kallon-kallon suke yiwa junansu tsanani kunya tarufe Habeeb wai shine ya aure auntyshi salma tsawon lokacin suka dauka a tsaye daga bisani salma takawo karshen shiru ta hanyar furta zo zauna Habeeb mu yi magana Habeeb ya langwa6e kai yace aunty sal...
Dakata Habeeb! Karka k'ara kirana da suna aunty tuni na tashi daga wannan matsayin a yanzu Kaine gaba da ni.
Habeeb yak'arasa ya zauna a gefen bed ita ma ta zauna kusa da shi, tafara magana cikin rauni murya Habeeb wannan tsari da kafito da shi zaman mu ba zai yi armashi saboda ka aure ni ne don kana ji tausayina to bai kamata kana guduna.
Habeeb yayi k'asa da murya yace aunty salma kunyarki nakeji salma tarik'o hannunshi tace Habeeb ka ajiye zance kunya a gefen domin yanzu babu kunya a tsakaninmu tunda igiyar aure tashiga tsakani mu, a dare ranan Habeeb ya nunawa salma cewa shi d'in ba 'karamin yaro bane kamar yadda take kallonshi, ya sanyata farin ciki da bata ta6a mafalki samu a rayuwarta tun
```

daga lokacin salma take ririta shi tana bashi girma a matsayin shi na mijinta tana matuk'ar son Habeeb tamkar numfashinta duk lokacin da Habeeb yake a gari bai yi tafiya ba salma na manne da shi tana nuna masa salon so, sannu a hankali son salma yasami muhalli a zuciyar Habeeb yabata babban matsayi a zuciyarshi yadda salma take ririta Habeeb da shagwa6a shi yasa tayi nassara mallake shi saboda akwai son girma Sam bayaso reni, yana matuk'ar son rayuwar Hutu gaba d'aya tsarin rayuwarshi ta turawa ce in har yana gida bayaso salma tayi nisa da shi hatta da baccin a k'irjin salma yakeyi ana cikin haka tasamu ciki Habeeb tamkar zai yi hauka don farin ciki har cikin salma yashiga wata tara bata fasa farantawa Habeeb ba ga girman ciki ga girman jiki amma a haka salma take zage dantsi ta taraiyi Habeeb, wata rana na zaune a downstairs parlour yana duba wasu file's salma tanufi wurinshi jin tak'o tafiyarta yasa Habeeb yad'ago suna had'a ido yasake mata murmushi, ita ma ta mayar masa da martani garin taka stairs k'afarta ta zame  ta dinga mulmula akan stairs har ta sauko k'asa Habeeb ya watsarda file's d'in hannushi da gudu yanufi wurinta, tuni jini ya ballewa salma Habeeb ya dinga girgiza ta saidai ko motsi batayi duk iya 'ko'kari Habeeb yadauki salma ya k'asa saboda tayi mishi nauyi da gudu yanufi _main gate_ ya nemo taimako bala driver suka saka salma a mota sai hospital, yayinda salma keta faman bleeding nan take doctor's suka yanke shawara yi mata cs saboda kada baby da yake cikinta mutu Habeeb ya yi sign aka shiga _operation theatre_  da ita likitoci sukayi nasara Ciro mata baby girl mai Kama da ita sak saidai sun k'asa tsayarda bleeding d'in takeyi har salma tafarfado jini na zubar mata, cikin yanayi na jigata tace a kira mata gani yanayi da take ciki yasa likitoci suka amince Habeeb ya shiga d'akin salma na gani shi tarik'o shi da kyar take iya magana tace.......
[04/09 1:53 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```41```

Habeeb kayafe min yadda nakeji jikin nan nawa bana tunani zan tashi, da sauri Habeeb yarufe mata baki yana girgiza, yace za ki tashi salma in kika tafi wa zai kula miki da ni da babynmu"? Allah zai kula da Ku Habeeb dama chan shi yake kula da dukani halittu sa.
Habeeb share hawaye da suka zubo masa yace "please salma stay with me don't leave us we really need you me & my baby
Habeeb inaji rad'ad'i da zafin ciwo kayi min addu'a da sauri Habeeb yadinga karanto  addu'a yana tofa mata tayi murmushi k'arfin hali tace Habeeb me na Haifa"?
Baby girl mai kama da ke kinaso ki gannta salma tadaga kai bara naje na kawo miki ita kinji salma naa"?
Ya sunbace goshi had'e da lips nata yafice yayinda salma tabishi da kallo, idanuta na tsiyaya hawaye, Habeeb yana karasowa rik'e da baby ya ga an turo salma lullube da farin kyale bayan fitar shi Allah ya kar6i ran salma Habeeb yayi matuk'ar tsorata saura kiris ya jefarda baby da

sauri wata nurse ta kar6i baby gawar salma yanufa yadinga girgiza ta saida likitoci{doctor's} suka rik'e Habeeb kuka yakeyi kamar k'arami yaro, daga bisani aka wuce da gawar salma gida akayi mata sutura kamar yadda addini musulunci ya tanarda, ranarda sadaka bakwai aka rad'awa baby sunan salma Habeeb yana kiranta da iman kasancewar madam Hindu bata lokacin kula da baby iman dole Habeeb yabarta hannu Hajiya khareema ita kuma ta bud'e babi tatsar Habeeb da kuma cusa masa Maryam ita ala dole so take Maryam ta maye gurbin salma, a haka rayuwa iman tacigaba da kasancewa a k'arkashin kulawa Hajiya khareema har salma tayi shekara biyar da rasuwa Habeeb bai k'ara tunani yin aure ba farko haduwar shi da Haleesa ya je gani iman yatararda 'yar aiki Hajiya khareema tafi da iman unguwarsu shine yabiyota har driven shi ya watsawa Haleesa ruwan kwatami a karo na biyu ma yaje gani iman still Hajiya khareema tace tana gidansu lami mai aikinta shine haduwar shi ta biyu da Haleesa haduwar shi ta uku da Haleesa nan ma yaje ganin iman akace tabi lami gidansu ashe tsakani unguwar su lami mai aikin Hajiya kareema da Unguwar su Haleesa ba nisa kusan unguwa d'aya ce titi ne kawai yaraba su.

```cigaban labari ```
Madam Hindu tasauke ajiyar zuciya tashafi sumar kan Habeeb, zuciyarta cike da tausayi d'a nata Ko yaushe mafalkinta zai cika nagani Habeeb yak'ara aure"?
A hankali ya bud'e kwayar idonshi yarik'o hannu madam Hindu cikin sanyayar muryar shi mai matuk'ar dad'i yace mom tunani me kike yi"?
Madam Hindu tayi murmushi tace no thing son Habeeb ya mik'e zaune yace mom banaso ko kad'an naganki ciki damuwa please karki d'auki damuwar crazy girl kisaka a ranki'
Murmushi madam Hindu tayi daga bisani tace wacece crazy girl"?
Yana yatsina fuska yanuna bedroom d'in mommy da yatsashi yace wance take ciki madam Hindu ta girgiza kai tace _stop calling her crazy infact she is your sister_
She is not yafada had'e da mik'ewa tsaya yayi mik'a yace mom zan shiga ciki nayi wanka madam Hindu tayi murmushi had'e daga masa kai yayinda Habeeb yahaura stairs d'in zai sada shi da room d'inshi madam Hindu ta bishi da kallo daga bisani ta mik'e tanufi bedroom d'inta wurin Haleesa.......

```DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S ```

Jeeddah Aliyu🌹
[05/09 9:57 pm] Jeeddah Aliyu🌹: [05/09 4:07 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```43```

Zaune take ta rakka d'a uban tagumi sallamar Madam Hindu ce tadawo da ita natsuwarta, da sauri tanufi wurinta, sannu Haleesa kintashi ya jikin naki"?
Murmushi Haleesa tayi tace I'm okay mom ba abunda yake min ciwo
"Alhamdulillah hankalina ya yi matuk'ar tashi Haleesa da naganki cikin wannan hali har naji a raina lallai ya Zame mini dole na tambaye ki waye yaya Habeeb"?
Tuni idanu Haleesa sun ciko da kwala ta sada kai k'asa cike da tausayi madam Hindu tarik'o hannuta karki kiyi kuka Haleesa in har wannan tambaya nawa zai haifar miki da tashi hankali to kiyi han'kuri karki fad'a kinji"?
Haleesa ta share hawaye had'e da majina tad'ago jajaye idanuta cikin sark'ewar halshe, tafara bawa madam Hindu labarin rayuwarta da yaya Habeeb tana dasa aya ta rushe da kuka mai matuk'ar sautin gaske, madam Hindu ta rungume ta tana sharar hawaye domin ita kanta labari Haleesa ya matukar bata tausayi, cikin tausasa halshe tafara rarrashin Haleesa ta hanyar furta mata kalamai masu dad'i Haleesa ta share hawayeta tace mommy narasa yaya Habeeb yatafi yabarni da soyayyarshi a zuciya a kullum tunani nakeyi anyya zan samu Wanda zai so ni kamar yaya Habeeb"?
Za ki samu Haleesa in har kika saka hank'uri da tawakalli Allah zai kawo miki wanda yafi yaya Habeeb Murmushi kawai Haleesa tayi domin tasan abunda madam Hindu take fad'a ba zai ta6a kasancewa gaskiya ta lafe a jikin mommy tana sauke ajiyar zuciya.

```3:00pm```

Madam Hindu da Haleesa na zaune a _dining table_ Janet na gefen su tsaye yayinda Haleesa ke ta fama jujuya spoon d'in hannuta zuciyarta cike da zullumi yadda za ta ci abinci da ke gabanta.
A hankali yake taka stairs hannaye shi na cikin aljihu "black Jean's d'in da yake sanye da shi jikinsa na fitarda k'amshin turare intense man fuskarshi a had'e tamkar tsohon soja kallon d'aya Haleesa ta yi masa ta kauda fuska, yayinda shi kuma ko kallo bata isheshi ba da sauri Janet taja masa kujera ya zauna wani wulaqantace kallo ya watsawa Janet ya doshe hancinshi yana yatsinar fuska tuni Janet ta nisanta da shi saboda ta fahimce da ita yake madam Hindu ta dube shi tana murmushi tace son me ke faruwa naga ka doshe hancinka"?
"Very slowly yafara magana mom bakyaji yadda parlour nan ya gume da odour"?
Humm! Habeeb rigima sarki 'yan kyayami ni ba abunda naji tajuya wurin Haleesa tace Haleesa ko ke kinji wari a parlour"?
Girgiza kai Haleesa tayi cikin rawar murya tace nima  mommy ba abunda naji.
Cike da jin haushin Haleesa Yaja tsoki sanin halinshi da mommy tayi yasa da kanta tayi mishi "serving yatsine yake cin abinci sai wani ya6ata fuska yakeyi, sai lokacin madam Hindu ta lura da Haleesa bata cin abincinta Haleesa ki ci abinci ki mana
Haleesa tad'ago ta dube mommy tace toh! Ta tsurawa abincin idanu fried rice with pepper chicken da had'e com slow a sama sai d'an uban Bama cream da Janet ta yaya6a mata duk duniya ba abunda Haleesa ta tsana irin Bama cream masifar wari shi takeji, tun ranar farko zuwanta Lagos yaya masa'ud ya yi musu take away na jallof rice aka saka shi tanaci saida tayi Amai kunya takeji tace da mommy bataci Bama cream kada wannan Mr arrogant yadauke ta a
```

matsayi _villager_ Haleesa ta sauke numfashi ta ciko spoon ta kai bakinta runtsi idanuta tayi ta hadiye abinci yasoma ratsa throat nata duk iya k'ok'ari Haleesa nagani abincin yashiga hanjinta abun yagagara sakamako wani amai da yataso mata da sauri ta furzar da na bakinta tasoma kakari a firgici madam Hindu tarik'o ta "what's worry Haleesa"?
Haleesa takasa magana sai faman yun'kuri amai takeyi madam Hindu tajuya wurin Habeeb da ke cika yana batsawa jin yakeyi tamkar ya shak'o Wuyan Haleesa ya gagaura mata dirty Slave's tace "please son halp me with glass of water
Cikin zafin rai Habeeb ya mik'e yature kujera yafice daga dining area a zuciyarshi yace in har sai na bata ruwa ta mutu madam Hindu ta mik'e da kanta tadauko robar ruwan faro ta mi'kawa Haleesa da sauri ta k'ar6a tasha tad'ago idanunta da sukayi jajir madam Hindu tace sannu Haleesa murmushi mai cike da jin kunya Haleesa tayi tace yauwa mommy"
Yakamata na kira doctor Elizabeth ta duba ki.
Haleesa ta girgiza kai had'e da cewa no need mom dama banaci wannan abin duk lokacin da naci shi sai nayi amai ta'karsa magana had'e da nuna Bama cream da yatsanta dariya mommy tayi sosai Haleesa na tayata daga bisani ta tsagaita dariyar nata ta dungurewa Haleesa kai tace next time in har zuciyarki bayaso abun karki kara ci kinji"?
Haleesa tad'aga kai madam Hindu tasake yi mata serving d'in wani abinci, hankali kwance Haleesa take ci abincinta
Kinga kin kore mana wannan sarkin kyakyami abun kad'an ya haddasawa Habeeb tashin zuciya shi mutum ne matuk'ar tsafta gaske tsaftarshi har ta zarce ta masu hankali har madam Hindu ta dasa aya a zanceta Haleesa tana kallonta......
[05/09 9:48 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```44```

Murmushi Haleesa tayi tace mommy yana da gaskiya tsafta cikon addini, madam Hindu ta tabe baki tace Tsaftar Habeeb ta fitar hankali ce'
A wannan karo Haleesa rasa abun fad'a tayi sai kawai tasaki murmushi madam Hindu ce tafara kamalla cin abinci ta mik'e tsaye tace Haleesa in kin gama ina downstairs parlour Haleesa tad'aga kai tana gani madam Hindu tafice ta ajiye spoon tadafe goshinta tafara zance zuci "how long zan dauka a gidanan"?
Miyasa duk lokacin da naga Handsome nake rasa peace of mind"?
hawaye suka cika mata ido a baiyane tace I miss you yaya Habeeb da kana tare da ni da duk banshiga wannan halin ba I really miss you yaya Habeeb no matter where I'm I'll never ever forget your memories"
Bayan hannuta tasaka ta goge hawaye fuskarta, ta mik'e tanufi downstairs parlour madam Hindu na zaune a two star yayinda Habeeb yake zaune a k'asa ya jingina kansa jikin kujera yayi

"crossing leg's nashi ya lumshe, idanu kamar mai bacci Haleesa tayi chak tana tunani ta yadda za'ayi ta'karasa parlourn madam Hindu na d'agowa ta hango ta tsaye tace Haleesa ki 'karaso mana Haleesa tamkar za ta fasa kuka tasoma tafiya zuciyarta cike da tsoron Habeeb jikinta na shacking tashiga parlour Sam bata lura da 'kafafu Habeeb ba jin tayi kamar ta taki wani abu tana sauke idanu ta k'asa taci Karo da k'afarta akan k'afafu Habeeb saura kiris tasaki fitsari a tsorace ta dube shi still idanushi a rufe da sauri ta sauke 'kafarta tajuya wurin madam Hindu taga hankalinta na waje TV tasaki ajiyar zuciya ta zagaye k'afafushi tanufi kusa da k'afafu madam Hindu ta zauna a k'asa madam Hindu tace tashi ki zauna akan kujera girgiza kai Haleesa tayi cikin sar'kewa halshe tace "No mommy nan ya isa  nima nafi jin dad'i zama a k'asa madam Hindu tayi murmushi tacigaba da kallonta cikin zuciyar Haleesa tace thank god da guy nan ya ji lokacin da na take shi "He' gonna kill me a karo na biyu ta'kara kallonshi idanu shi a rufe ta tsurawa lips d'inshi ido ta tabe baki had'e da fara zance zuci kalli lips nashi very pink da su maybe yana using lipstick yana matsayin namiji yana Shafa lipstick wannan ae abin kunya ne mtss d'an daudu kawai da sauri ta kauda fuskarta da bari kallonshi.
Duk abunda takeyi Habeeb yana kallonta ta 'kasan ido a zuciyarshi yace _what's hell dis crazy girl looking at my face"?_ ta taka min 'kafa but she staring me just like plasma tv mtss I hate dis girl for d first time my eye's saw on her.
Mtss Haleesa ta'kara
Jan tsoki a zuciyata tacigaba da zance zuci ta _I don't known why anytime my eye's Shaw dis arrogant man  I feel like crazy_ wata zuciya tace da ita ke Haleesa ina ruwanki da shi ki yi abunda yake gabanki shi d'in He doe's Care about you lokacin da ya ganki Sam bai nuna yata6a saninki "so forget about him tak'ara satar kallonshi ta yatsine fuska watakila bacci yakeyi naga tun lokacin da nashigo parlour nan idanu shi a rufe kin ji ki da wani zance banza Haleesa da ba bacci yakeyi ba da you're d first person da za ki sani Co's da yanzu ya falla miki mari ko kin manta kin taka 'kafarshi Haleesa tasaki ajiyar zuciya mtss nagaji da wannan zance zuci zuciyata ki barni na huta ta sada kai k'asa.
A zuciya Habeeb yace oh! God mommy akwai kwashe-kwashe ko zama me wannan crazy girl takeyi a gidanan oho"?
Gaskiya nagaji da gani ugly face nata I'll pack my luggage to leaves dis House be for I loose my temper nayi mata rashin mutunci har wani sunan ta rad'a min wai aljani mai idon magge ni ban kirata da suna aljana ba sai ita ce za ta kirani da aljani k'aramar yarinya kawai.
Madam Hindu ce tayi nassara katsi masa zance zuci da yakeyi ta hanyar kiran sunanshi Habeeb bai dai bacci  kake yi a zaune ba"?
Ya bud'e idanushi yace idanu na biyu mommy ba bacci nakeyi ba
Cikin tsanani tsoro Haleesa tad'ago dama guy nan idanu rufe su kawai ya yi ba bacci yakeyi ba na shiga uku ni Haleesa tuni jikinta ya jik'e da gumi Bala driver ne yayi sallama yashigo falon yana kyalla ido ya ga Haleesa yadaka wani uban tsalle yana murza idanu shi yace boss yakasa furta abunda yakeso fada sai faman maimaita sunan Boss yakeyi madam Hindu tadaka mishi tsawa kai! Bala wannan wane irin sakarci ne"?
Ina matuk'ar yabawa k'o'kari Habeeb da yake iya zama da kai wani abin mamaki duk inda ya jefa k'afa yana tare da kai.
Bala driver yacire fencing cap yasoma fifita da ita yace madam wallahi aljana nagani a parlour nan, mtsss Habeeb yaja dogon tsoki ya mik'e cikin zafin rai da sauri Bala yanufi wurinshi yace

Boss dubi chan ka gani aljanarka ce a zaune dama ni nasan za ta biyo ka kasan aljannu sun fi so kyawawa irinku ka shiga uku boss aure ka za tayi cikin tafarfasa zuciya Habeeb ya wanka masa mari shut up Bala I think you are insane yature Bala ya haura sama da gudu a tsorace madam Hindu tajuya wurin Bala tace aljana kuma Bala ina aljanar take"?
Bala yanuna Haleesa da yatsa yace gatanan zaune kusa da ke madam sau uku muna haduwa da ita a Yobe kuma kowane haduwa da mu kayi da ita sai yadauki dogon lokacin kafin mu sake ganita
Madam ta kyalkyale da dariya tace Bala wannan Haleesa ce ba aljana ba amma zo ka bani labari yadda haduwarku ta kasance nan take Bala ya kwararo wa madam Hindu labari haduwarsu da Haleesa madam Hindu tace Haleesa abunda Bala yafad'a gaskiya ne"?
 Haleesa tad'aga kai miyasa baki sanarda ni kinta6a haduwa da Habeeb ba"?
Mommy gani nayi haduwar batada mahimanci, tafad'a cikin rawar murya madam Hindu tayi shiru alamar tunani nan take zuciyarta tafara sak'a mata wani abu......

```DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S```

Jeeddah Aliyu🌹
[15/09 12:28 pm] Jeeddah Aliyu🌹: [07/09 8:03 am] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```45```

Note:- _Masoyan Ni da yaya Habeeb Ku yi hank'uri 2 day's kudaina gani post hakan yafaru ne a dalilin matsananci ciwon baya da nake fama da shi_

Tsawon lokacin madam Hindu tadauka tana sak'e-sak'e daga bisani tad'ago ta dube Haleesa, wance ta sada kai k'asa kamar mai d'aukar karatu tausayi ta ya kamata har taji a zuciyarta lallai ita ce za ta kawo karshen matsalar Haleesa muryar Bala driver ce tadawo da hankalin madam Hindu tajuya waje Bala da ke dur'kushe a gabanta madam ki taimake ni kada narasa aiki na domin yadda naga Boss ya harzuk'a kwano tuwo na zai iya yak'arewa a gidanan, madam Hindu tayi dariya tace Bala kai da Habeeb ba'a shiga tsakaninku matsayin biyu kake takawa a wurin shi kaine driven shi kuma kaine P.A{personal assistance} gaskiya Bala kai d'an gata Habeeb ne.
"Bala driver tamkar zai rusa ihu yace wallahi madam a wasu lukuta Boss Sam baya la'akari da matsayin mutum kaitsaye yake tsula maka tsiya, cikin salon tafiyarshi ta k'asaita yake taka stairs hannushi d'aya na cikin aljihu wando shi batare da ya kalli Wanda suke parlour ba yanufi k'ofar fita tak'o tafiyarshi kadai Haleesa ta ji amma saida gabanta yafad'i da sauri Mommy ta
```

dakatar da shi Habeeb fita za ka yi ne"?
Ya wani 6ata fuska kamar zai yi kuka yace "Eh!
Amma kuma za ka fita ne batare da Bala driver ko kana nufi kai za ka yi driving da kanka"?
Whatever! yafada kaitsaye
Look son I known you can't drive musanmman yadda ababe hawa suke cikoso a gari Lagos kayi han'kuri kutafi da Bala.
Dafe goshi ya yi da alama yafara gajiya da surutu mommy nashi mom bana bukatar Bala I can managed with myself amma ke za ki iya d'aukar shi aiki "Co's I don't need him anymore madam Hindu tayi murmushi tace banaso fitarka kai kadai Habeeb ka yi hankuri kutafi tare da sauri Bala ya zube gabanshi yace am sorry Boss nasan nayi laifi amma ba zan 'kara ba Haleesa ta ja tsoki a zuciyarta tace dube yadda ake rarrahinshi sai kace Wanda aka yi wa wani laifi, d'an reni wayo kawai wallahi na tsini mutum mai girman kai muryarshi ta katsiwa Haleesa zance zuci ta baza kunnenta domin taji abunda zai fada mom na tsani mutum mai surutu a rayuwata sai kuma gashi shine halaya Bala duk abunda idanushi suka gane mishi, sai yafallasa yak'arasa magana had'e da gallawa Bala harara madam Hindu tace duk abunda bakaso daga yau zai kiyaye Habeeb ya mik'e kafad'a had'e da cewa mom I have to go!
Yajuya yafice daga parlour madam Hindu tajuya wurin Bala tace tashi kutafi Bala da sauri Bala ya mik'e yabi bayanshi, Haleesa ta tabe baki tacigaba da zance zuci ta kai amma wannan guy ya kware da wulaqaci sunanshi Sam bai dace da shi ba saboda yaya Habeeb d'ina is very simple man da kyar ka ga yaya Habeeb d'ina yayi fushi amma wannan He is always angry fuska a muturk'e so arrogant.
Haleesa! Da sauri Haleesa tad'ago tace Na'am mommy!
Da alama kema zaman gidanan yafara isarki koh"?
Murmushi Haleesa tayi batare da tace komai ba madam Hindu ta mik'e tsaye had'e da cewa ina zuwa tanufi upstairs yayinda Haleesa tasaki ajiyar zuciya tace Allah yasa mayarda ni gidan aunty juwairiyya za tayi saboda jin kai na nakeyi tamkar prisoner ga zuciyata ta hanani sukuni na zama _heart restless_ musanmman duk lokacin da idanuna sukayi tozali da Habeeb, nakan tsince kaina cikin matsananci fad'uwar gaba.
Har madam Hindu tafito Haleesa bata sani ba saida tadafa ta a tsorace Haleesa tajuya, cikin tausayawa  madam Hindu tace Haleesa kidaina yawan tunani Kada ya shafi lafiyarki murmushi Haleesa tayi madam Hindu tacigaba da fad'ar mu je ki rakani unguwa saboda na fahimce cewa kin gaji da zama guri d'aya tana gaba Haleesa na biye da ita har suka isa parking space da gudu "Driven madam Hindu yak'araso ya bud'e masu mota kirar _BMW 6 series_   Haleesa da madam Hindu suka parke a owner's corner yawo sukayi sosai Haleesa ta ga gari Lagos sai d'an banza go slow tsiya madam Hindu ta yi wa Haleesa shopping nagani nafad'a "ready made da jallabiya's masu matuk'ar kyau da tsada sai around 10:30pm suka dawo gida Aderwale ya yi parking ya bud'ewa madam k'ofa yayinda Haleesa ta bud'ewa kanta Aderwale yataya ta kwashe bag's had'e da ledoji da suka yo shopping a parlour suka zube kayan madam Hindu tace Haleesa ki k'arasa da kayanan ciki duka naki ne, Haleesa ta duk'a k'asa tayi wa madam godiya da sauri madam ta d'agata haba! Haleesa miye haka"?
Duk abunda nayi miki bana buk'atar godiya saboda na dauke ki tamkar Hannah Haleesa tayi murmushi tace duk da haka na gode mommy Allah yasaka miki da alkhairi.
Ameen Haleesa ki je ki kwanta madam nak'arasa magana ta nufi bedroom d'inta Haleesa ta

kwashe kayan tanufi bedroom d'in Hannah, tsanani gajiya da ta de6o ga kuma bacci fal idonta yasa ta haura wrong stairs a maimako ta haura left wanda zai sadata da room d'in Hannah sai ta haura right na part d'in Habeeb kaitsaye ta murd'a handle tashiga...
[10/09 9:37 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```46```

Bedroom d'in Hàbeeb tana shiga ta jefarda kayan hannuta da yake d'akin akwai duhu Sam bata lura da, Habeeb da ke kwance wani juyi tayi tacire mayafinta had'e d'an kwalinta ta jefa bisa bed suka fad'a akan fuskarshi daga bisani tanufi switch ta kunna wuta haske yagauraye d'akin karaf idanuta suka sauka akan bed Habeeb na kwance ya yi matashi{pillow} da hannaye shi fuskarshi na lullube da mayafinta da jefa akan bed Haleesa ta zaro ido jikinta yadauki rawa tasoma ja da baya a hankali yacire mayafinta da ke kan fuskarshi ya jefa mata batare da bud'e idanushi yafara magana, d'aya bayan d'aya sai kace mai koyon magana _hey what's are you doing in my room at dis time"?_
Cikin sark'ewa halshe Haleesa tace I'm so..rry I made a mistake am  looking Hannah's room but I'm so sorry.
_hey shut up I don't wants any apologies from you just pack your things  & leave my room right now_
A tsorace Haleesa ta tattara kayanta jikinta na rawa ta bud'e k'ofa tafice tsanani rud'ewa yasa Haleesa takasa gane inda za ta dosa dole ta koma downstairs parlour anan tayi tsaye daga bisani ta haura stairs d'in zai sadata da room d'in Hannah tana shiga d'akin ta jefarda kayan hannuta, tafad'a kan gado tasoma zanci zuci wai gari yaya naje room d'in yaya Habeeb"?
Gaskiya nagaji da gidanan gaba d'aya naji garin Lagos yafita min a rai, tun zuwa na banyi waya da Ammi ba gashi na baro phone d'ina gidan aunty juwairiyya ballatana na kira yaya salman ya had'a ni da Ammi, mtss gidanan ban had'a komai da su ba yakamata zuwa yanzu ace nasan lokacin da zan dauka a gidanan, domin ba zan iya cigaba da zamansa, banaji ko 1week zan iya k'arawa a garinan.
Ta b'angare Habeeb kuma Haleesa nafita ya ja tsoki ko uban me yarinya nan ta zo yi a d'akina oho"?
Na tsani yarinya nan Sam banaso ganita duk lokacin da idanu sukayi arba da ita sai naji tsanarta na 'kara yad'uwa a zuciyata.

```washe gari ```

Tun misali 'karfe 10:44am Haleesa ta falka tayi wanka ta shirya cikin d'aya daga cikin jallabiya's d'in da madam Hindu ta siya mata rigar _black colour ce anyi mata ado da blue colour stone's_
```

tayi rolling da mayafin rigar duk da batayi make up ba she look very beautifully ta nemi gefen bed tayi zaune ta zabga d'an uban tagumi, zuciyarta cike da tunani yadda za'ayi tafita saboda tana masifar tsoron had'uwa da Habeeb idanuta suka cika da kwalla jin karar bud'e k'ofa yasa tayi maza ta goge hawaye fuskarta madam Hindu ce tashigo jikinta sanye da atamfar Sheraton tayi matuk'ar k'ar6a fatarta Haleesa me kikeyi a d'aki da har yanzu baki fito kiyi breakfast"?
Haleesa tayi murmushin yak'e tace mommy yanzu nakeso fitowa sai kuma ga ki'
To tashi mu tafi Haleesa na kamalla breakfast ta nufi 'karamin parlour ta zauna k'asa kamar yadda tasa6a, hankali madam Hindu tajuya wurinta, Cikin murmushi tace Haleesa har yanzu kin k'i kisaki jikinki sai wani d'ari-d'ari kikeyi Haleesa tayi murmushi had'e da sada kai k'asa 'kamshin turare intense man yacika parlour da sauri Haleesa d'ago idanuta suka sauka akan fuskarshi yana sanye da coat red colour da black colour trouser hannushi na cikin aljihu yayinda d'ayan hannun rik'e da file's fuskarshi a had'e Sam ba alama fara'a a tare da shi kaitsaye yanufi kusa da madam Hindu ya zauna kamar mai rad'a yace _Good morning mom_
Morning son da fatar katashi lafiya"?
_lafiya qalau mom_
Batare da Haleesa tad'ago tace ina kwana yaya Habeeb"?
Yayi ignoring nata tamkar wani kurma, yacigaba da maganarshi mom ga wad'anan documents za ki yi sign nasu zan wuce da su Abuja.
Madam Hindu ta bata fuska tace Habeeb bakaji Haleesa tana gaidaka"?
Ya yatsine fuska a wulaqance yace lafiya  sani halinshi da mom tayi yasa batayi masa complain akan yadda ya amsa gaisuwan da Haleesa tayi masa sai kawai tayi ignoring nashi had'e da k'ar6a documents d'in tayi signing phone d'inshi yayi ringing ya mik'e cikin yanayi tafiyarshi ta k'asaita yafice, yayinda a fakace Haleesa tabishi da kallo, cikin zuciyarta tace banza d'an girman kai shi wannan da Allah yayi shi gidan sarauta da bansan iya adadi iskanci da zai dinga tsulawa mutane, madam Hindu ta katsita ta hanyar kiran sunanta Haleesa kar6i file's d'inan ki kai ma Habeeb nasan halinshi da mantuwa zai iya tafiya ya manta da su daga baya yadinga yi min k'orafi cikin sanyi sanyi jikin Haleesa ta kar6i file's d'in tafice tana fita ta hango shi a parking space Bala driver ya bud'e mishi mota zai shiga tazara da ke tsakaninsu zai iya tafiya kafin tak'arasa sai kawai tayi decided ta kwala masa kira yaya Habeeb tafad'a da k'arfi batare da yajuya ba ya tsaya chak gani haka yasa Haleesa ta kwasa da gudu Habeeb da ke tsaye zuciyarshi tamkar za ta kama da wuta jin sautin gudunta, yak'ara harzu'ka ya tsani ya ga mace na gudu da sauri yashige mota Haleesa ta'karaso tana sauke numfashin gudu da tayi, tadafa k'ofar mota tace yaya Habeeb gashi mommy tace nakawo maka,
Da k'arfi yafisge file's d'in har yana had'awa da yatsun Haleesa garin fisgar file's  zobenta na azurfa yasa6ulle sakamako ramar da tayi zobe yadaina tsayuwa a yatsanta Haleesa ta matsa daga jikin motar tana yarfe hannu cikin k'unar zuciya yace da Bala kai! tsayuwar me kake yi ne"?
Jiki na rawa Bala ya bud'e k'ofa ya zauna a sit d'in gaba yayinda Aderwale driven madam Hindu yaja mota yanufi gate Haleesa tabisu da kallo daga bisani tanufi cikin gida zuciyarta cike, da d'ibin tsanar halaya Habeeb airport  Aderwale ya ajiye su fitowar da Habeeb zai yi daga cikin mota zobe yafad'o daga jikinsa ya duk'a yadauki zoben yana jujuya shi ras-ras gabanshi yafad'i sakamako ganin sunan da ke rubuce a jikin zoben ```NI DA YAYA HABEEB ``` Yafad'a a baiyane me wannan sunan yake nufi"?

Meyasa gabana yafadi anyya kuwa yarinya nan ba bibiyana takeyi ba"? nan take, yatuna da haduwarsu da kuma ganin da yayi mata a gidansu......

```DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S ```

Jeeddah Aliyu🌹
[15/09 12:29 pm] Jeeddah Aliyu🌹: [14/09 10:56 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```47```

Haleesa na Shiga cikin gida ta koma mazaunita ta zauna, madam Hindu ta dubeta cikin kulawa tace kin bashi file's d'in Haleesa"?
Haleesa tad'aga kai madam Hindu tacigaba da kallon tv yayinda Haleesa ta sada kai k'asa tasoma aikin nata{tunani} madam tajuya ta tsurawa Haleesa ido gani yadda ta zurfafa a tunani tausayinta yakamata nan take ta k'udiri anniya sai takawo karshen matsalar Haleesa saboda yarinya ta shiga ranta matuk'a.

```ABUJA```

Misali 'karfe _12:15pm_ flight d'in yadauko passengers daga Lagos yasauka a airport na Abuja, a hankali Habeeb Lamido yake saukowa daga stair's na jirgi Bala driver yana biye da shi a baya driven madam Hindu na Abuja ne ya yi picking nasu kaitsaye gidan Habeeb Lamido da ke Garki driven yadosa yayinda Habeeb Lamido ke ta fama da zance zuci na hadu da 'yan mata kala daban-daban ban ta6a haduwa da very smart girl irin Haleesa, zuciyata tana bani cewa Haleesa ta zo d'aukar famsa abunda na ta6a yi mata ko kuma ta fad'a a tarko sona shiyasa take bibiyana in kuwa d'aya daga ciki ya kasance gaskiya lallai sai na wulaqanta ta Co's ban ta6a haduwa da yarinya da naji farat d'aya na tsaneta irinta, kamar daga sama ya ji sautin muryar Bala driver yana fad'ar Boss mu iso gida Habeeb yasauke ajiyar zuciya had'e da yafito daga cikin mota.

```BAYAN KWANA BIYU ```

Haleesa na kitchen tana wanke plate's da cups d'in da sukayi amfani da su kasancewa yau Sunday Janet tana church, madam Hindu kuma tafita ba yadda batayi da Haleesa su fita tare Haleesa ta k'i a cewarta bataji dad'i cikin sanyi jiki take wanke plate's d'in K'amshin turare
```

intense man da tashak'a ya haddasa mata fad'uwa gaba, Habeeb Lamido ne tsaye a k'ofar kitchen yana aika mata kallo mai cike da tsana Cikin tsanani tsoro Haleesa tajuya karaf suka had'a ido, da sauri ta sada kai k'asa Habeeb ya ja tsoki yak'arasa shiga kitchen d'in cikin muryarshi mai matuk'ar dad'i yafara magana kamar mai rad'a ke! Uban me kike jira a gidanan da har yanzu baki tattara komaitsa ki kibar mana gida"?
Wani irin shock yaja Haleesa jikinta yafara sharking, takasa furta uffan yadaka mata tsawa ke! Ba magana nakeyi da ke ba"?
Yak'arasa magana cikin k'unar zuciya muryarta na rawa tace Dan Allah kayi han'kuri ba laifina bane mommy ce har yanzu bata bani izzini tafiya gida.
_You're very stupid kina nufi mom ce mai laifi ashe bakida mutunci"?_
A lokacin d'aya mamaki had'e da tsoro sukayi nassara lullu6e Haleesa ko kwakwara motsi takasa yayinda haushinta yak'ara turnuk'e Habeeb a harzuk'e yafisgo hannuta yace wai ke me kike tak'ama da shi waye ubanki duk fad'in African da har zanyi miki magana kiyi ignoring nawa"?
Hawaye suka wanke fuskar Haleesa tsanar Habeeb ta kanainaye zuciyarta, da k'arfi ta fincike hannuta saidai kash takasa kwace hannu nata ranta a 6aci tace dallah malam kasake min hannu, kallon uku saura kwa6o ya watsa mata ya yatsine fuska cikin sigar wulaqanci yace ki kwace hannunki mana Haleesa ta girgiza kai tace kai kanka kasan da zan iya kwace hannun nawa ba bazan tsaya ina rok'a mutume da baisan daraja da k'imar d'an Adam irinka.......
[14/09 11:02 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```48```

Da k'arfi Habeeb ya murde mata hannu yace kin tafka babban kuskure na shigowa rayuwata tuni nagano cewa kina bibiyana, kuma sai na tabbata miki da cewa bansan daraja da k'ima mace banza 'yar iska irinki mai bin d'an namiji har gidansu da wannan Neman gindi zama da kike yi a wurin mom da fitowa kika yi kika fad'a mata gaskiyar dalili zuwanki gidanan.
Haleesa ta zaro manya idanuta masu cike da tsoro ta hadiye miyau masu masifar d'aci ta rushe da matsananci kuka tace karka jefeni da mummuna kalma yaya Habeeb don ina zaune a gidanku bashi zai baka damar ka fad'a mini magana son ranka, ka tambaye mahaifiyarka za ta fad'a maka dalilin zama na a gidanku. Habeeb ya galla mata harara had'e da cewa ke! Munafuka ni fa nagano cewa abu biyu ne yakawo ki a gidanan  kodai kin zo daukar famsa wulaqanci da nayi miki a baya ko kuma kin zo neman soyayyata jin wannan furuci na Habeeb yak'ara rud'a Haleesa ta runtse idanuta tana kuka kamar ranta zai fita saboda zafi biyu Habeeb Lamido yahad'a mata ga zafin murd'e mata hannu da yayi ga kuma na magaganu da yake ta faman gasa mata, yayinda Habeeb yacigaba da cewa bara na fad'a miki ko a k'afa aka daura min ke zan kwance na yar Co's nafi k'arfinki  infact ban ta6a jin na tsani wata 'ya mace sai

akanki don haka kidaina yaudara mom ta hanyar ihun da kike yi kina cewa yaya Habeeb ya mutu ba zai ta6a dawowa gareki wai ke ga ki 'yar duniya Haleesa ta bud'e idanuta tasoma watsawa Habeeb kallon mamaki daga bisani tace tir da wannan duk'usashiya kwakwalwa taka da har ta tasanya maka tunani cewa ni Haleesa ina sonka me zanyi da kai bana d'aya daga cikin shashashu 'yan mata da kudinka da kyakyawa surarka za su rud'a kuma yau d'inan zan bar maka gidanku bara ka k'ara ganina ba har abada Habeeb Lamido ya ja tsoki wulgar da hannunta da k'arfi ya juya cikin tafiyarshi ta k'asaita yafita daga kitchen d'in Haleesa ta dur'kushe 'kasan tile's tafashe da kuka tasoma danasani zuwa garin Lagos da kyar ta mik'e tsaye ta nufi room d'in Hannah tafad'a kan bed tafara zance zuci ashe Habeeb Lamido mahaukaci ne in banda hauka don kawai ya ganni a gidansu zai ce ina sonshi mtss shashasha kawai mai k'aramar kwakwalwa nan take tafara tunina rayuwarta da yaya Habeeb da yaya Habeeb yana raye me zanzo yi a garin Lagos da har wannan arrogant zai same damar wulaqantani, Haleesa tacigaba da shashekar kuka madam Hindu ta murd'a handle tashigo d'aki ta hango Haleesa kwance tana kuka da sauri tanufe ta Haleesa lafiya me kike yi ma kuka"? Cikin muryar kuka Haleesa tace mommy gida zan tafi, inaso gani Ammi naa nagaji da garinan tak'arasa magana had'e da rushewa da kuka madam Hindu ta rungume ta tace haba Haleesa don kinaso zuwa gida shine za ki dinga kuka"?
Yi maza ki share hawayenki ki tashi mu tafi na ajiye ki gidan Juwairiyya gobe masa'ud yasaka ki a flight ki koma Yobe da sauri Haleesa ta k'ank'ame mommy tace na gode mommy Allah yasaka miki da alkhairi, madam Hindu tad'ago ta tana murmushi tace Ameen Haleesa 'yar gidan mommy jiki na rawa Haleesa ta had'a kayanta madam Hindu sai faman dariya take yi mata had'e da tsokanarta a haka suka fice daga gidan zuciyar Haleesa cike da farin ciki tabar ma Habeeb gidansu, suna isa gidan Juwairiyya tun kafin Aderwale yabude mata k'ofa ta bud'e da kanta tafito Aderwale yabud'ewa madam Hindu k'ofa tafito tana dariya tace Haleesa sai murna kike yi za ki tafi kibar mommy koh"?
Haleesa ta rufe fuskarta da tafin hannuta Juwairiyya nagani su tafara washe hak'ora saboda kullum sai yaya salman ya kira waya ya tambayi Haleesa, madam Hindu ta zauna a parlour yayinda Haleesa tanufi d'akinta juice da ruwa masu sanyi Juwairiyya takawowa madam Hindu ta tsiyaya mata, a glass cup ta mik'a mata kur6a d'aya zuwa biyu madam tayi ta ajiye cup d'in bisa stool tajuyo tana facing Juwairiyya, tace Juwairiyya akwai magana mai matuk'ar mahimmanci da nakeso zanyi da ke akan Haleesa.....

```DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S ```

Jeeddah Aliyu🌹
[15/09 8:00 pm] Jeeddah Aliyu🌹: [15/09 4:50 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```49```

Tun daga lokacin da nadaura idanuna akanta naji tashiga raina matuk'a, nayi matuk'ar tausayawa Haleesa a dalilin labari rayuwarta da yaya Habeeb da tabani gani halin da take ciki da Kuma yabawa da ingantaciya tarbiya da takeda ita yasa na yi wa d'ana Habeeb sha'arwata ko ba komai tarasa Habeeb ga kuma wani Habeeb yadawo watakila ko don sunan Habeeb kadai zai iya saka tarage tunani marigayi Habeeb bansaniba ko iyayyenku za su amince su ba wa Habeeb aureta har madam Hindu ta dasa aya Juwairiyya tana mata kallon mamaki daga bisani tace mommy karki ce na katsi miki hanzari sai naga kamar Haleesa bata dace da Habeeb ba saboda mu talakawa ne duk zuri'armu ba mai kud'i Juwairiyya tak'arasa magana had'e da sada kai k'asa, madam Hindu tayi murmushi tace Juwairiyya Yakamata ki bada kyakyawa sheda akaina da zuri'arta bana d'aya daga cikin masu kud'in da ke kyamar talaka a wurina mai kud'i da talaka duk d'aya ne shawara na zo neman a wurinki ya kamata ki k'arfafa min guiwa domin na cima aikin alkhairi da nayi niyya karki manta shekaru biyar a baya da suka wuce Habeeb yarasa matarshi a waje haihuwa, dalilin haka yakasa k'ara aure Juwairiyya ina buk'atar Habeeb ya yi aure saidai duk lokacin da na tuntube shi da zance aure sai yace na nemo mishi matar aure, ni kuma narasa yarinya da zan nemo masa wance za ta soshi tsakani da Allah ba don kud'inshi ko kyakyawa sura da Allah yabashi sai gashi kwatsan Allah yakawo min Haleesa har gida, kuma ta cika duk wasu sharudd'a da nakeso matar Habeeb ta kasance da su Juwairiyya tasauke ajiyar zuciya tace shikenan mommy sai kifara sanarda Habeeb in ya amince da Haleesa a za6inki daga bisani sai a sanarda iyayyenmu domin su ne kadai a halin da Haleesa take ciki za su iya tankwarata ta amince da zance aure.
Habeeb bashida matsala Juwairiyya duk abunda nakeso shima yanasonshi bamu ta6a samu sa6ani ra'ayi, Haleesa ta d'aga hankalinta tana buk'atar ganin Ammi karki hanata tafiya ni kuma zanyi amfani da wannan damar naje Yobe na nemawa Habeeb aureta.
Ba matsala mommy duk yadda kika ce haka za'ayi'
"Madam tayi murmushin farin ciki tace kira min Haleesa mu yi sallama, Juwairiyya ta mik'e tsaye tana washe hak'ora kamar mai talla toothpaste Haleesa na kwance Abba na bisa cikinta yana wasa doki, Juwairiyya tana dariya tace wannan k'aton yaro za ki aza bisa ciki yana doki sai yafasa miki ciki, Haleesa ta mik'e zaune tace Abba naa ba k'ato bane, Juwairiyya ta tabe baki had'e da cewa ki taso Ku yi sallama da "mommy za ta wuce Haleesa ta mik'e tsaye suka fice tare Madam nagani Haleesa ta'kara fad'ad'a murmushinta tace Haleesa ni zan wuce ki gaida Ammi kafin nazo mu gaisa.
"To mommy zai taji na gode sosai da d'ibin alkhairi ki agareni madam ta zuge zip handbag d'inta tafito da bundle na dubu d'ari ta mik'awa Haleesa gashi Haleesa ki yi wa su Ammi tsaraba Haleesa ta girgiza kai had'e da cewa hidima da kike yi da ni mommy tayi yawa ba zan kar6i kud'inki ba.
Madam ta mik'e tsaye ta mik'awa Juwairiyya kud'in Juwairiyya takasa k'ar6a kad'a kai "madam tayi batare da tace komai ba ta ajiye kud'in bisa hannu kujera, tajuya tafice cikin sanyi jiki Haleesa da Juwairiyya suka Mara mata baya da sauri Aderwale yafito ya bud'ewa madam mota, tashiga Haleesa ta dafa k'ofa tace mommy narasa da wance kalma zaiyi amfani da ita wurin
```

gode miki, banida abunda zan saka miki da shi mommy saidai, zan cigaba da yi miki addu'ar fatan alkhairi ke da zuri'arki.
Madam tayi murmushi da ke nuna taji dad'i kalamai Haleesa daga bisani tace ba komai Haleesa ni na d'auke ki tamkar Hannah, Haleesa da Juwairiyya suna tsaye har motar madam tafice daga gate d'in gidan sannan suka juya zuwa cikin gida, Haleesa tafad'a bisa kujera ta ja wata doguwar ajiyar zuciya Juwairiyya ta zauna kusa da ita cikin sanyi murya tace Haleesa meyasa kike so komawa Yobe alhali da bakinki kika ce sai kinyi _3 week's_ za ki koma gashi _1 week_ kawai kika yi kince za ki koma ko anyi miki wani laifi ne"?
"Ba abunda akayi min kawai dai nagaji da garinan
Shikenan bara na shirya na rakaki kasuwa gobe sai ki bi morning flight"
Murmushi Haleesa ta yi, cikin zuciyarta tace hakan shi zai saka Habeeb Lamido yagano kwakwalwa da zuciyarshi sun cuce shi da suka haska masa cewa na zo Lagos ne saboda shi, ta yatsine fuska a baiyane tace _disgusting_ Juwairiyya ta zaro idanu tace lafiya kike Kuwa Haleesa"?
"Yes am absolutely fine
Murmushi Juwairiyya tayi ta mik'e tsaye had'e da cewa ki je ki d'auko mayafinki mu tafi batare da ta jira amsar da Haleesa za ta bata tashige bedroom d'inta.
Yinin ranar sun k'arace shi ne a yawon siye banza siye wofi ba su ne suka dawo gida ba sai ana kiran sallah magariba, don haka a gajiye suka shiga cikin gida kaitsaye kowane su yanufi bedroom d'inshi Haleesa ta jefarda mayafinta bisa bed tanufi bathroom tayi alwala bayan ta gama sallah ta zabga tagumi tasoma tunani Habeeb Lamido zuciyarta cike da mamaki shi wai ina bibbiya shi to me zan tsinta a wurinshi mtss mahaukaci kawai marar tunani, da kyar ta samu ta rinjaye zuciyarta tabarta ta gabatarda sallah isha dawowar masa'ud yasa tafito parlour ba rarrashin da banyi mata akan tayi zamanta koda  _1 week_ ne ta'kara musu amma Haleesa ta k'ek'ashe k'asa tace ita dai tafiya za tayi dole masa'ud ya kyaleta......
[15/09 8:00 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```50```

```WASHE GARI ```

Da wuri Haleesa ta tashi ta yi wanka tana jiran fitowar Masa'ud yakaita airport, saida yagama ja mata rai sannan yace tafito su tafi koda tafito _10:30am_ ta buga gashi flight d'in da zata bi zai tashi k'arfe _11:30am_ sai faman complaints take mishi ya6ata mata lokacin Juwairiyya sai faman dariya take yi gani yadda Halee take zumud'i tafiya saida suka ga tashin jirgin su Haleesa sannan Masa'ud da Juwairiyya suka nufi gida.
```

```YOBE```

Jirgi na sauka bayan Haleesa tafito batare da 6ata lokacin ba, taja trolley d'inta taxi tashiga tana gani driven taxi d'in yashiga unguwarsu tasaki sanyaya ajiyar zuciya tasaki iska ta furzar tace _Home, sweet Home_ har k'ofar gidansu taxi d'in tayi parking cikin zumud'i ta balle k'ofa tafito, dai-dai lokacin da Hasheem 'kanin marigayi yaya Habeeb yafito daga cikin gida Haleesa ta tsura masa ido da sauri-sauri numfashinta yake fita saboda sai yau ta'kara tabbatar da tsanani kama da Hasheem yakeyi da Yaya Habeeb banbanci su kawai yaya Habeeb yafi shi, tsayi gani yadda take kallonshi yasa yasake mata murmushi yak'araso daf da ita cikin tsokana yace babylove ya akayi ne naga kin wani tsare ni da ido sai kace yau kika fara ganina ke da kika je Lagos a maimako ki waye sai kika k'ara kwaso k'auyanci.
"Ko kwakwara motsi Haleesa ta kasa yi da k'arfi Hasheem ya kira sunanta Haleesa!
Haleesa ta dube shi tayi ajiyar zuciya, kafin ta yi magana mai taxi yace malama sallame ni na tafi Hasheem yace nawa ne kud'inka"?
D'ari uku ne yallabai Hasheem yafito da _N 500_ ya mik'a masa shi kuma ya bashi chaji yadauki trolley d'inta ya wuce gaba tana biye da shi sai tambayoyi yake zuba mata yayinda Haleesa takasa bashi amsar ko d'aya daga ciki da sallama yashiga cikin gidan had'e cewa Ammi fito ga bak'in Lagos da rana tsaka da sauri Ammi tafito daga d'aki tana gyara d'auri d'an kwalinta tana had'a ido da Haleesa mamaki ya baiyana akan fuskarta da gudu Haleesa ta'karasa wurinta ta rungume ta tasa kuka Ammi ta bubbuga bayanta, haba! Haleesa meye kuma abun kuka"?
Cikin muryar kuka mai cike da shagwaba tace Ammi nayi kewarki'
Hasheem da ke gefe ya kyalkyale da dariya yace lallai yarinya nan dad'i ya yi miki yawa ki ce kukan dad'i kikeyi to ni zan tafi anjima zan dawo na kar6i tsaraba na yak'arasa magana had'e da yaficewa.

```3 hour's later```

Haleesa na zaune a d'akin Ammi sai labari madam Hindu take ba wa Ammi, kwarai Ammi ta yaba da kirkin "madam Hindu
Tace duk lokacin da tashigo Yobe zata zo Ku gaisa.
Murmushi Ammi tayi tace Allah yakawo ta lafiya
"Ameen Ammi bara na je na gaida inna mairo ta zari hijab d'inta had'e da ficewa, tana Shiga gidan zainab ta shek'o suka rungume juna sai da aka fara kiran sallah magariba Haleesa ta koma gida bayan ta gama sallah tafito tsakiyar gida tasha iska yaya salman ya yi sallama yashigo, Haleesa ta amsa mishi, ya zauna kusa da ita tana bashi labari Lagos Salman ya kyalkyale da dariya yace Haleesa manya ke da kika yi _1 week_ kacal a Lagos har wani labari za ki bayar
Haleesa ta turo baki tace Allah yaya salman nayi yawo saidai ba sosai ba kuma baka ga gidan da na zauna Allah gidan yahad'u kamar a abroad ae kuwa Salman da kamal suka dinga yi mata dariya Haleesa ta gallawa kamal harara tace gwara ni na je lagos nayi kauyanci kai kuma kamal baka ta6a zuwa ba tak'arasa magana had'e da yi masa gwalo har baffa yashigo gida suna

zaune tsakiyar gida suna fira shima ya zauna akayi firar da shi kowane su zuciyarshi cike da tsan-tsan farin ciki sakamako gani yadda Haleesa take annashuwa da nishad'i sai misali k'arfe _11:44pm_ kowane su yanufi d'akinshi Haleesa tasuya kaya zuwa wata 'yar k'aramar vest ta daura zani bisa ta kwanta tana daura kanta bisa pillow ta lumshe idanu  nan take  face d'in Habeeb Lamido yafara yi mata shawagi a eye's nata da sauri ta bud'e idanuta _"why Habeeb why don't leaves my heart to be in peace"?_
Ba gidanku kadai ba har garin Lagos na baro maka _but you still following me_
Hawaye suka ziraro mata a gefen idanu suka sauka bisa wuyanta, kuka Haleesa tayi sosai daga bisani bacci ya yi awo gaba da ita anan ma bata tsira ba saboda mafalki shi tadinga yi Habeeb ya zamewa rayuwarta karan tsaye.

```BAYAN SATI D'AYA ```

Haleesa da zainab sun dawo daga islamiyya yamma suna tafiya suna fira, tun daga nesa Haleesa ta hango mota kirar _KIA cerato_ a Parke a k'ofar gidansu wani matsananci fad'uwar gaba taji saboda ta ta6a gani Habeeb Lamido cikin irin wannan motar, zainab tace Haleesa bak'i masu kud'i mu ka yi ne na hango had'ad'iyar mota a k'ofar gidanmu"?
Haleesa tad'ago ta dube ta tasauke ajiyar zuciya tace oho! Tafad'a kaitsaye suna k'arasawa k'ofar gida idanu Haleesa suka sauka bisa number motar _Habeeb Lamido 5_  abunda idanuta suka hasko mata kenan tsanani tsoro had'e da tashin hankali suka chukuikuye mata zuciya Wanda hakan ya haddasa mata zaro idanu tanemi yawu bakinta tarasa, a zuciyarta tace na shiga uku me wannan shu'umi ya zo yi a gidanmu..."?

```DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S ```

Jeeddah Aliyu🌹
[17/09 3:01 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```51```

Meke faruwa ne Haleesa na ga kina zarar ido"?
Muryar Zainab ce tadawo da ita daga natsuwarta taja gwaron numfashi daga bisani, tace ba komai zainab ta yi murmushi rashin yarda da amsar da Haleesa tabata Haleesa kenan nasan abunda kike yi wa zarar ido duk bai wuce sunan Habeeb da kika gani a jikin number motar nan

ta'karasa magana had'e da nuna number motar da yatsanta tadafa kafad'ar  Haleesa tacigaba da cewa yakamata ace zuwa yanzu kin manta da rayuwarki da Yaya Habeeb Co's He will never comeback to us yaya Habeeb ya mutu Haleesa ba zai ta6a dawowa so ki manta da shi ko Ke ma za ki ji dad'i rayuwarki, hawaye suka cikawa Haleesa idanu saboda a yanzu batada wata matsala da ta wuce Habeeb Lamido tarasa dalilin da yasa take yawan tunani shi, cikin sanyi murya tace zainab bara na shiga gida batare da ta jira amsa da zainab za ta bata tashige zaure gidansu, tana jefa k'afarta tsakiyar gida ta yi turus Ammi da madam Hindu sai wata kyakyawar budurwa mai kama da Habeeb Lamido ta hango zaune, suna fira nan take tagano cewa wannan budurwa ita ce Hannah, ajiyar zuciyar Haleesa ta yi cikin tsanani jin dad'i gani bak'i{visitor's} nasu tayi sallama a lokacin d'aya suka amsa mata madam Hindu tace idonki kenan Haleesa kin manta da mommy koh"?
Cikin yanayi naji kunya ta durk'usa tace ina wuni mommy"?
"Lafiya qalau Haleesa zo ki zauna anan ta nuna mata kusa da ita Haleesa ta zauna tajuya wurin Hannah da ke ta faman zabga murmushi, tace Mommy ko ban tambaya ba wannan ita ce Hannah madam ta yi murmushi tace kin chanka dai-dai Hannah da Haleesa sukayi dariya fira sukeyi Haleesa sai kyalkyale dariya takeyi madam tace ashe Haleesa kina dariya"?
Haleesa ta sada kai k'asa tana dariya k'asa-k'asa Ammi ta yi 'yar gajeriya dariya daga bisani tace tun daga lokacin da Haleesa tadawo daga Lagos take wannan fara'a narasa me Ku ka bata da yasauya ta a d'an k'ank'ani lokacin Ammi ta'karasa magana had'e da dariya madam da Hannah suka kwashe da dariya sallama baffa da baba Audu ce ta katsi musu dariyar da suke yi bayan sun gaisa a tsakaninsu madam tajuya wurin su Haleesa tace Haleesa da Hannah Ku ba mu guri za mu yi magana Haleesa ta mik'e had'e da rik'o hannu Hannah tace zo mu je gidan su zainab Ku gaisa.
"Madam ta gyara zama tafara magana malam Usman wata alfamar nazo nema a wurinka shine dalilin da yasa nace inaso magana da kai, bansaniba ko za ka amince da buk'atana"?
"Malam Usman yajuyo ya dube d'an uwanshi daga bisani yace fad'i Alfarma taki Hajiya kuma Allah yasa zan iya.
Malam usman dama alfarma da na zo nema alkhairi ne bansaniba, ko ta ya za Ku d'auki wannan al-amari azahiri gaskiya tun daga ranar da naga Haleesa na yaba da hankali da tarbiyyarta musanman da naji tarihi rayuwarta da marigayi Habeeb Wanda hakan ne yajanyo na yi wa d'ana Habeeb sha'arwata a tunani na Haleesa tarasa Habeeb ga kuma wani Habeeb yadawo ina matuk'ar tausayi rayuwa Haleesa 'yarku na buk'atar abokin rayuwa Wanda zai sota yabata kulawa wance za ta sa ta manta da rayuwa da tayi da marigayi Habeeb yanayi da Haleesa ta tsince kanta a ciki yadda ta mayarda kuka da tunani abokai rayuwarta, hakan zai iya shafar lafiyarta kun ga kenan za'ayi biyu babu an6ata d'aya biyu bata gyaru ba amma kuma a matsayinku na iyayyeta menene ra'ayinku"?
A lokacin d'aya baffa, baba da kuma Ammi suka sauke ajiyar zuciya domin abu ya zo musu a bazata basu ta6a tunani jin wannan, furucin daga bakin madam Hindu baba Audu ya numfasa, yace tabbas Hajiya kin zo mana da abu mafi girma, da farko inaso kisani mu talakawa ne ba mu da komai akullum fafutukar Neman nasawa a bikin salati mu ke ni aganina, sai naga kamar d'anki baidace da 'yarmu wutsiyar ragumi tayi nesa ga k'asa.
Ka ga malam Audu kada Ku fassara ni baibai, ni mutumce kamarku don kawai Allah ya yi min arziki sai Ku banbanta kanku da ni to kusani duk d'aya mu ke a wurin Allah sai Wanda yafi wani

tsoronshi, ban zo nan don na cutarda 'yarku kafi nazo nan saida nasa akayi min bincike akanku nima na baku damar Ku yi bincike akaina da kuma d'ana Habeeb.
A wannan karo malam Usman ne yabata amsa ta hanyar cewa shikenan Hajiya, mu amince da buk'atarki domin bamusan abunda Allah yake nufi a cikin wannan al-amari Haleesa tarasa Habeebu a lokacin da tafitarda rai da tak'ara samu farin ciki sai kuma ga wani Habeebu yashigo rayuwarta Allahu Akbar Allah mai iko, mu amince Hajiya amma a bisa sharad'i d'aya sharad'i kuwa shine har sai Haleesa ta furta da bakinta ta amince da d'anki domin mu ba za mu yi mata dole ba.
Murmushi madam Hindu tayi da ke baiyanar da farin cikinta tace nima bana goyo bayan ayi mata dole, Ku barni da ita agabnku zan yi magana da ita insha Allahu za ta amince ae Haleesa yarinya ce mai biyayya......
[17/09 5:07 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣the sweetest love_❣

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```52```

Tun lokacin da su Haleesa suka shiga gidan su zainab fira ta barke a tsakaninsu, _ringing_ d'in wayar Hannah ce ta katsi musu firar tasu gani "mommy ce ta kira yasa Hannah bata yi picking ba ta mik'e tsaye had'e da cewa Haleesa tashi mu tafi mommy ce ta kirani watakila wuce wa za mu yi Haleesa ta mik'e zainab ta Mara musu baya da sallama suka shiga gidan madam tace zo zauna Haleesa za mu yi wata magana da fatar za ki bani had'in kai"?
Haleesa tad'aga kai madam ta rik'o hannuta cikin k'ask'antar da kai tafara magana Haleesa burin kowace uwa tagari d'anta ko 'yarta su sami abokin rayuwa nagari shiyasa na za6e ki a matsayin matar da nakeso Habeeb ya aura"
A firgice Haleesa tad'ago dara-dara idanuta tasauke su bisa fuskar madam kallo d'aya za ka yi mata gano tsintsa tashin hankali da take cikin, yayinda madam tacigaba da fad'ar amincewarki kadai nake nema Haleesa saboda iyayye ki sun amince, shin Haleesa kin amince da Habeeb ya maye gurbi marigayi Habeeb a wurinki"?
Wannan tambayar ta "madam Hindu ta yi matuk'ar gigita Haleesa had'e da haddasa mata shiga tashin hankali maras misaltuwa, ta zazzare ido tamkar ta ga wani abin tsoro yayinda zuciyarta ke bugawa kamar ana buga ganga nan take tafara shid'ewa numfashinta yafara k'ok'ari k'auracewa gangar jikinta tsanani tashin hankali da rashin mafita suka lullu6e ta sai faman zazzare ido take mayuwaci abu ne ta kalli tsabar idon madam Hindu tace batason d'anta babban tashin hankalinta bai wuce yadda za ta rayuwa da Habeeb Lamido mutumin da yakira ta da suna 'yar iska mai bibbiya d'an namiji kenan furucin sa zai tabbata na cewa ina sonshi.
Da k'arfi madam ta girgiza Haleesa tadawo haiyyacinta kin yi shiru ba ki ce komai ba Haleesa ko bakyaso Habeeb ne"?
Karki dame kanki Haleesa ba za mu yi miki dole ba har. madam ta dasa aya Haleesa tana kallonta ta sauke numfashi yafi a kirga daga bisani ta tattaro k'uzari had'e da jarumtaka ta cikin sar'kewa halshe tace, mommy ko za'a daura min bakin bindiga banida bakin furta kalma banaso
```

jininki akwai 'yan mata da yawa a gari Wanda suka fi ni baki yi la'akari da kasancewa ta 'yar talaka kika tsalleke su kika za6e ni a matsayin wance ta dace da d'anki ta ya ya zan bad'a miki k'asa a ido nace banaso jininki"?
"Tun lokacin da narasa yaya Habeeb nasan cewa nayi bankwana da farin ciki na har abada, don haka "mommy na amince da yaya Habeeb ko ba komai yana d'auke da suna mutumin da yake mahad'in rayuwa ta na gode da wannan karamawa ta ki tana k'arasa magana ta mik'e da gudu tashige d'akin Ammi tafad'a sama gado tafashe da kuka mai k'arfin gaske.
"Malam Usman yace Hajiya ko za'a hank'ura da wannan al-amari saboda naga har yanzu Haleesa bata fitarda marigayi Habeebu a ranta kada aje gyara gira arasa ido ta je takasa zaman lafiya da d'anki kin ga anyi ba'ayi ba d'aukar makaho photo.
Karka damu malam Usman kayi 'ko'kari ka yak'i wannan tunani daga zuciyarka karka manta har yanzu Haleesa tana fagge na jinyar mik'i da ke zuciyarta na rashin marigayi Habeeb a cikin wannan yanayi Habeeb za'ayi amfani da wannan damar yakafa sanssani yak'i neman za6e zuciyar Haleesa Wanda a sannu za ya maye gurbi Marigayi Habeeb har ta manta ta ta6a rayuwa da wani Habeeb addu'arku kawai nake nema a cikin wannan tafiyar.
"Shikenan Hajiya Allah yasanya alkhairi yasa abunda za'a ci amfaninsa ne Allah yahad'a Kansu ya kad'e fitina a tsakaninsu.
_Ameen malam Audu_
Yayin da madam Hindu tacigaba da cewa sai magana tagaba Habeeb zai zo yagana da Haleesa su fahimce juna daga bisani zan yi magana da d'angin mahaifinsa su kawo kud'in gaisuwa a kuma sanya, lokacin banaso auren yadauki dogon lokacin.
A wannan karo baffa ne yayi magana yace ba damuwa Hajiya duk yadda kika tsara haka za'ayi Allah yasanya alheri _Ameen_ daga haka su baffa suka mik'e had'e da ficewa daga gidan Hannah da zainab suka shiga d'akin Ammi cikin tattausa lafazi suka soma rarrashi Haleesa da kyar suka samu tadaina kuka da take yi Hannah tace Haleesa kidaina kuka domin yaya Habeeb mutumin kirki ne bashida matsala za ki ji dad'i zama da shi wani d'agowa Haleesa ta yi ta watsawa Hannah mugun kallo mai cike da tambayar kinada hankali kuwa daga bisani tace.....

```DEDICATED TO SHEHU ALIYU FAMILY'S ```

Jeeddah Aliyu🌹
[17/09 7:38 pm] Jeeddah Aliyu🌹: [17/09 3:01 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣the sweetest love_❣

```®NWA```

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```51```

Meke faruwa ne Haleesa na ga kina zarar ido"?
```

Muryar Zainab ce tadawo da ita daga natsuwarta taja gwaron numfashi daga bisani, tace ba komai zainab ta yi murmushi rashin yarda da amsar da Haleesa tabata Haleesa kenan nasan abunda kike yi wa zarar ido duk bai wuce sunan Habeeb da kika gani a jikin number motar nan ta'karasa magana had'e da nuna number motar da yatsanta tadafa kafad'ar  Haleesa tacigaba da cewa yakamata ace zuwa yanzu kin manta da rayuwarki da Yaya Habeeb Co's He will never comeback to us yaya Habeeb ya mutu Haleesa ba zai ta6a dawowa so ki manta da shi ko Ke ma za ki ji dad'i rayuwarki, hawaye suka cikawa Haleesa idanu saboda a yanzu batada wata matsala da ta wuce Habeeb Lamido tarasa dalilin da yasa take yawan tunani shi, cikin sanyi murya tace zainab bara na shiga gida batare da ta jira amsa da zainab za ta bata tashige zaure gidansu, tana jefa k'afarta tsakiyar gida ta yi turus Ammi da madam Hindu sai wata kyakyawar budurwa mai kama da Habeeb Lamido ta hango zaune, suna fira nan take tagano cewa wannan budurwa ita ce Hannah, ajiyar zuciyar Haleesa ta yi cikin tsanani jin dad'i gani bak'i{visitor's} nasu tayi sallama a lokacin d'aya suka amsa mata madam Hindu tace idonki kenan Haleesa kin manta da mommy koh"?
Cikin yanayi naji kunya ta durk'usa tace ina wuni mommy"?
"Lafiya qalau Haleesa zo ki zauna anan ta nuna mata kusa da ita Haleesa ta zauna tajuya wurin Hannah da ke ta faman zabga murmushi, tace Mommy ko ban tambaya ba wannan ita ce Hannah madam ta yi murmushi tace kin chanka dai-dai Hannah da Haleesa sukayi dariya fira sukeyi Haleesa sai kyalkyale dariya takeyi madam tace ashe Haleesa kina dariya"?
Haleesa ta sada kai k'asa tana dariya k'asa-k'asa Ammi ta yi 'yar gajeriya dariya daga bisani tace tun daga lokacin da Haleesa tadawo daga Lagos take wannan fara'a narasa me Ku ka bata da yasauya ta a d'an k'ank'ani lokacin Ammi ta'karasa magana had'e da dariya madam da Hannah suka kwashe da dariya sallama baffa da baba Audu ce ta katsi musu dariyar da suke yi bayan sun gaisa a tsakaninsu madam tajuya wurin su Haleesa tace Haleesa da Hannah Ku ba mu guri za mu yi magana Haleesa ta mik'e had'e da rik'o hannu Hannah tace zo mu je gidan su zainab Ku gaisa.
"Madam ta gyara zama tafara magana malam Usman wata alfamar nazo nema a wurinka shine dalilin da yasa nace inaso magana da kai, bansaniba ko za ka amince da buk'atana"?
"Malam Usman yajuyo ya dube d'an uwanshi daga bisani yace fad'i Alfarma taki Hajiya kuma Allah yasa zan iya.
Malam usman dama alfarma da na zo nema alkhairi ne bansaniba, ko ta ya za Ku d'auki wannan al-amari azahiri gaskiya tun daga ranar da naga Haleesa na yaba da hankali da tarbiyyarta musanman da naji tarihi rayuwarta da marigayi Habeeb Wanda hakan ne yajanyo na yi wa d'ana Habeeb sha'arwata a tunani na Haleesa tarasa Habeeb ga kuma wani Habeeb yadawo ina matuk'ar tausayi rayuwa Haleesa 'yarku na buk'atar abokin rayuwa Wanda zai sota yabata kulawa wance za ta sa ta manta da rayuwa da tayi da marigayi Habeeb yanayi da Haleesa ta tsince kanta a ciki yadda ta mayarda kuka da tunani abokai rayuwarta, hakan zai iya shafar lafiyarta kun ga kenan za'ayi biyu babu an6ata d'aya biyu bata gyaru ba amma kuma a matsayinku na iyayyeta menene ra'ayinku"?
A lokacin d'aya baffa, baba da kuma Ammi suka sauke ajiyar zuciya domin abu ya zo musu a bazata basu ta6a tunani jin wannan, furucin daga bakin madam Hindu baba Audu ya numfasa, yace tabbas Hajiya kin zo mana da abu mafi girma, da farko inaso kisani mu talakawa ne ba mu da komai akullum fafutukar Neman nasawa a bikin salati mu ke ni aganina, sai naga kamar

d'anki baidace da 'yarmu wutsiyar ragumi tayi nesa ga k'asa.
Ka ga malam Audu kada Ku fassara ni baibai, ni mutumce kamarku don kawai Allah ya yi min arziki sai Ku banbanta kanku da ni to kusani duk d'aya mu ke a wurin Allah sai Wanda yafi wani tsoronshi, ban zo nan don na cutarda 'yarku kafi nazo nan saida nasa akayi min bincike akanku nima na baku damar Ku yi bincike akaina da kuma d'ana Habeeb.
A wannan karo malam Usman ne yabata amsa ta hanyar cewa shikenan Hajiya, mu amince da buk'atarki domin bamusan abunda Allah yake nufi a cikin wannan al-amari Haleesa tarasa Habeebu a lokacin da tafitarda rai da tak'ara samu farin ciki sai kuma ga wani Habeebu yashigo rayuwarta Allahu Akbar Allah mai iko, mu amince Hajiya amma a bisa sharad'i d'aya sharad'i kuwa shine har sai Haleesa ta furta da bakinta ta amince da d'anki domin mu ba za mu yi mata dole ba.
Murmushi madam Hindu tayi da ke baiyanar da farin cikinta tace nima bana goyo bayan ayi mata dole, Ku barni da ita agabnku zan yi magana da ita insha Allahu za ta amince ae Haleesa yarinya ce mai biyayya......
[17/09 5:07 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```52```

Tun lokacin da su Haleesa suka shiga gidan su zainab fira ta barke a tsakaninsu, _ringing_ d'in wayar Hannah ce ta katsi musu firar tasu gani "mommy ce ta kira yasa Hannah bata yi picking ba ta mik'e tsaye had'e da cewa Haleesa tashi mu tafi mommy ce ta kirani watakila wuce wa za mu yi Haleesa ta mik'e zainab ta Mara musu baya da sallama suka shiga gidan madam tace zo zauna Haleesa za mu yi wata magana da fatar za ki bani had'in kai"?
Haleesa tad'aga kai madam ta rik'o hannuta cikin k'ask'antar da kai tafara magana Haleesa burin kowace uwa tagari d'anta ko 'yarta su sami abokin rayuwa nagari shiyasa na za6e ki a matsayin matar da nakeso Habeeb ya aura"
A firgice Haleesa tad'ago dara-dara idanuta tasauke su bisa fuskar madam kallo d'aya za ka yi mata gano tsintsa tashin hankali da take cikin, yayinda madam tacigaba da fad'ar amincewarki kadai nake nema Haleesa saboda iyayye ki sun amince, shin Haleesa kin amince da Habeeb ya maye gurbi marigayi Habeeb a wurinki"?
Wannan tambayar ta "madam Hindu ta yi matuk'ar gigita Haleesa had'e da haddasa mata shiga tashin hankali maras misaltuwa, ta zazzare ido tamkar ta ga wani abin tsoro yayinda zuciyarta ke bugawa kamar ana buga ganga nan take tafara shid'ewa numfashinta yafara k'ok'ari k'auracewa gangar jikinta tsanani tashin hankali da rashin mafita suka lullu6e ta sai faman zazzare ido take mayuwaci abu ne ta kalli tsabar idon madam Hindu tace batason d'anta babban tashin hankalinta bai wuce yadda za ta rayuwa da Habeeb Lamido mutumin da yakira ta da suna 'yar iska mai bibbiya d'an namiji kenan furucin sa zai tabbata na cewa ina sonshi.
Da k'arfi madam ta girgiza Haleesa tadawo haiyyacinta kin yi shiru ba ki ce komai ba Haleesa ko bakyaso Habeeb ne"?
```

Karki dame kanki Haleesa ba za mu yi miki dole ba har. madam ta dasa aya Haleesa tana kallonta ta sauke numfashi yafi a kirga daga bisani ta tattaro k'uzari had'e da jarumtaka ta cikin sar'kewa halshe tace, mommy ko za'a daura min bakin bindiga banida bakin furta kalma banaso jininki akwai 'yan mata da yawa a gari Wanda suka fi ni baki yi la'akari da kasancewa ta 'yar talaka kika tsalleke su kika za6e ni a matsayin wance ta dace da d'anki ta ya ya zan bad'a miki k'asa a ido nace banaso jininki"?
 "Tun lokacin da narasa yaya Habeeb nasan cewa nayi bankwana da farin ciki na har abada, don haka "mommy na amince da yaya Habeeb ko ba komai yana d'auke da suna mutumin da yake mahad'in rayuwa ta na gode da wannan karamawa ta ki tana k'arasa magana ta mik'e da gudu tashige d'akin Ammi tafad'a sama gado tafashe da kuka mai k'arfin gaske.
Aunty Juwairiyya da Zainab zaune a d'akin Ammi sun tusa lefen Haleesa gaba suna kallon sai faman santi da yaba kayan suke yi sa6ani Haleesa da ke kwance rub da ciki akan gadon Ammi ita ba kuka take yi ba amma a yadda takeji Zuciyarta na tarfafasa gwara ta yi kuka ko za ta same sausauci k'unci da take ciki babban bak'i cikinta bai wuce yadda Mutane Unguwa har ma da na cikin gidansu suke zuzuta kayan lefe ta basu San cewa a wurinta atamfar super prints ta fiye mata tarin kayanan Zainab tace Haleesa bara ki sauko ki taya mu ganin wannan abun arziki ko kunya kike ji kada Ammi tace bakida kunya tak'arasa magana cikin tsokana
"Cikin zafin rai Haleesa ta diro k'asa ta tsalleke kayan tafice Zainab da Aunty Juwairiyya suka bi ta da kallon, girgiza kai Aunty Juwairiyya tayi tana mamaki tauri kai da kafiya irinta Haleesa.

```1 WEEK LATER ```

Tuni gidaje biyu sun fara gudanar da tsare- tsare yadda bikin aure 'ya'ya su zai gudana tsawon wannan lokacin Habeeb da Haleesa ba su k'ara gani Junansu.
Haleesa na zaune bisa kujera 'yar tsuguno a tsikiyar gida tana yanka alayahu almajiri ya yi sallama Haleesa ta amsa masa yace wani mai mota yana sallama da Haleesa a k'ofar gida, ras gaban Haleesa yafad'i nan take annuri da ke kan fuskar ta ya gushe tace je kace batanan Ammi ta lek'o daga cikin kitchen ta ce je ki kace gatanan zuwa tajuya wurin da Haleesa take zaune ta galla mata harara had'e da cewa me kike Jira ne da bara ki tashi ba da sauri Haleesa ta mik'e ta jefar da wuk'a hannunta Ta Shiga D'aki tasaka Hijab tafito fuskarta ahad'e tanufi k'ofar gida dafe k'irji Haleesa ta yi sakamako motar Habeeb Lamido da ta ganin nan take Numfashinta yafara kai da kawo ta runtsi idanuta...

Jeeddah Aliyu🌹
[10/24, 11:44 AM] +234 813 417 9191: [11/10 6:25 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```®NWA```

°°°°```In Dedication```°°°
*To Shehu Aliyu family's*

```60```

Jiki a sa6ule tak'arasa fita Wannan karo ma Bala ne yafito daga cikin mota yak'araso wurinta "Barka da fitowa ranki yadad'e"
Yauwa Bala ya gida"?
Lafiya Qalau ya hidimomi biki"?
Shiru Haleesa ta yi had'e da sada kai k'asa gani yadda ta yi yasa Bala ya yi murmushi yace ba fa ni kadai bane tare nake da "Boss'
Wani fad'uwa gaba Haleesa tak'ara ji tsanani tsoro ya lullu6e ta tamkar mai ciwo hak'ora ta bud'e bakinta tace Bala kace da shi yak'araso ciki ranar ma da na tsaya da shi a k'ofar gida saida Baffa ya yi Fad'a "Bala yace okay ba matsala bara na yi masa magana Bala yanufi wurin mota ya bud'e k'ofar da Habeeb yake Zaune fuskarshi ahad'e ba bu annuri ko misk'arazairatil a tare da shi da alama zuwan sa na dole ne "Boss tace ka shigo daga ciki saboda Baffanta bayaso tsayuwa a k'ofar gida"
```

A harzuk'e Habeeb ya ke kallon Bala daga bisani yace banida buk'atar shiga gidansu don haka za ka iya bata dalilin zuwa na gidansu"
Ka yi hank'uri "Boss ka daure ka k'arasa daga ciki karka manta ko yanzu kafin mu zo gidanan irin Fad'a da Madam ta dinga yi ta nuna 6aci ranta k'arara a dalilin rashin waiwaye Haleesa da ka yi Yakamata ace ka danne duk wata k'iyayya da ka ke yi mata saboda saura d'a k'ank'ani lokacin ta zama mallaki ka in tashigo gidanka kana da iko yi mata duk abunda ka ga dama ba bai hanaka saboda ikonka ce.
Habeeb yadage gira sama yana duban Bala cike da gansuwa da kalaman Bala yasaki tsadade murmushinsa mai narkar da Zuciyar 'yan mata
Haleesa nagani Bala na musu-musu da baki da alama magiya ya ke yi wa Habeeb haushi ya turnuk'e ta ta juya cikin gida tana shigawo ta ci karo da Ammi sai kawai tace Ammi Key's d'in d'akin yaya Salman za ki bani batare da Ammi tace da ita komai ba tashiga d'aki tadauko mata Key's ta mik'a mata a sanyaye Haleesa tak'ara juyawa k'ofar gida tana fita taci karo da su a bakin k'ofar shigowa Zaure ba shiri ta taka birki had'e da sunkuyar da kai Kallo d'aya Habeeb Lamido ya yi mata ya d'auke kai tsawon "5-6 minutes suka dauka a tsaye daga bisani Haleesa tanufi d'akin yaya salman ta bud'e k'ofa tajuya batare da ta bari sun had'a ido tace "Bissimillah!
Banza Habeeb ya yi kamar bai ji abunda tafad'a "Bala yace Boss ka k'arasa daga ciki bara na je na fito da kayan da ke cikin mota Wani tsuke baki Habeeb ya yi kamar mai tsotsa "Sweet ko mai shiri d'aukar selfie ya yi kici-kici da fuska, yajuya ya kalle d'akin yaya Salman Wanda tuni Haleesa ta tsofa a ciki tana jiranshi ya ta6e baki yanufi d'akin batare da yacire "cover shoe d'in k'afarsa kawai yadanna kai Haleesa na Zaune akan kujerar roba kanta na sunkuye tana wasa da yatsu hannunta "Ba don sani daraja da sallama da ke ita a musulunci da ba yadda za'a yi ya yi mata sallama"
"Assalamu Alaikum" yafad'a chan k'asan mak'oshi"
"Batare da Haleesa tad'ago kanta ta amsa mai masa da cewa "Wa'alaikum sallam warahmatullahi wabarakatih..."
Habeeb ya kya6e baki a zuciyarshi yace ka ji su  Al-Sheikh za ki yabawa aya zak'i ta in kika shigo hannuna 'ya nema mai kai Kamar dunk'ule "cabbage' ya ja ya yi tsaye Haleesa bata ce da shi ga wurin zama hakan ne yasa yacigaba da zance zuci tana nufi bara tace na zauna ba amma bara naga iya gudun ruwanta kafin na wanke mata allonta saboda naga kanta na hayak'i.
A fakace Haleesa tad'ago ta sace kallonshi yana nan tsaye k'ikan hannaye shi zube cikin aljihu wandoshi da sauri ta d'auke kai a zuciyata tace tofah wata sabuwa inji 'yan caca shi wannan mai tsawo kamar fol waya yana nufi bai ga wurin zama bane ko kuma duk cikin, salon tsabar kwarewa da wulak'anci ne amma bara nace ya zauna a karo na biyu da tasake d'agowa amma bata dube shi ba tace "please have a seat"
Zaro ido ya yi daga bisani ya gyatsine fuska kamar ya ga "cockroach a zuciyarshi yace "Humm! I can't believe this Illiterate girl she known how to speak English"
Ya dube kujera da ta nuna masa da yatsanta akwai tazara tsakaninta da wance ta ke Zaune yafito da "handkerchief fari kal daga gaban aljihu "black colour coat d'in da yake sanye da ita ya shinfid'a akan kujerar sannan ya zauna ya yi crossing legs nashi yafito da "phone in shi yafara buga "game in crush candy"
Haleesa ta cika ta yi dam! Me wannan mutumin yake nufi me ye laifinshi Haleesa ke yakamata ki fara gaida shi abunda d'ayan 6angare Zuciyata yace da ita kenan......."ina Wuni yaya

Habeeb"? tafad'a cikin sark'ewa harafi"
"Ignoring nata ya yi saida d'auke almost 3-4 minutes sannan yace da ban Wuni ba kya gani saida ya furzar da zazzafa iska yacigaba da cewa ke! Wai me yasa a duk lokacin da na zo gidanku sai kin yi "Wasting time in na"?
Numfashi da Haleesa ta sauke yafi a kirga da kyar ta iya controlling in "temperature' ta Co's wannan karo guy nan yakawo ta k'ul tace am sorry Yaya Habeeb wallahi.....
"Shut up please don't give me that fucking excuse yak'arasa magana had'e da cigaba da buga game in shi girgiza kai Haleesa ta yi cike da takaici tafara zance zuci na Shiga uku ni Haleesa wannan wane irin aure ne zan yi"?
"Very slowly yafara magana Kin d'auki kanki Wata tsiya sai kace ana sonki sai wani jiji da kai kike ko kin manta kina gaban Habeeb Lamido ne Wanda ba ya gajiya da furta miki kalma ```Tsana``` amma da yake ke Heartless ce har Wani Jan aji kike yi na kuma San duk wannan abu da kike yi kina yi ne don ki burgeni ni mutum ne kaifi d'aya ban ta6a sauya ra'ayi na musanmman akan abunda nace banaso don karki yi tsanmani in na aure ki wata rana za ki same gur6i a zuciyata tun daga lokacin da kika shigo rayuwata na nemi farin cikina narasa bana sonki wallahi na tsane ki tsanar da bara ta6a gushewa daga Zuciyata yak'are magana had'e da Murmushi.
Tun lokacin da yafara magana kai Haleesa yana sunk'unye a k'asa hawaye na bi kumatu ta, Habeeb ya mik'e tsaye hannunshi guda yana ciki aljihu yanufi inda Haleesa take Zaune daf da ita ya tsaye yad'an rankwafa yace ke!
A firgice ta d'ago tasauke ganinta akan fuskarshi k'asa jure kallon tsanar da yakeyi mata ta yi ta sada kanta k'asa.
Murmushi jin dad'i Habeeb yasaki sakamako hawaye da yagani akan fuskar Haleesa yace you hears all what's am saying right"?
K'asa magana ta yi kawai tad'aga masa kai cikin isa da tak'ama yacigaba da cewa "Don't you think is too early ace kin fara zubar da hawaye ki"?
"Is better ki share hawaye ki saboda bai kamata kifara zubar da su tun yanzu domin ina da buk'ata su a gida na  Haleesa tacigaba da share hawaye ta masu masifar Zafi da k'ona Zuciya.
"Habeeb ya ja tsoki had'e da cewa kina da aiki yarinya ya yi dialling number Bala yak'ara a kunnenshi "Hello! Bala wai me kike yi ne da har Yanzu ba ka k'araso ba"?
"Boss ina k'ofar gida nufina na dan ba Ku wuri za ka fi jin dad'i sakewa Ku sha fira
Kai! Banaso shirme banza da Wofi na baka _3 minutes_ ka shigo ko nayi maka abunda ba kayi tunani ba yana k'are magana ya yi hanging up"
Haleesa ta sa gefen hijab d'inta ta goge hawaye ta "Bala yashigo had'e da sallama yadire wani k'aton kwali had'e da farar Leda Habeeb ya dube Bala yace na ba ka "5 minutes kayi Mata bayani abunda ke ciki ni ina k'ofar gida kuma karka sake ka wuce time d'in na ba ka yaficewar shi batare da ya dube inda Haleesa take Zaune.
Bala yace ranki yadad'e dama "invitation card's ne mu kawo miki ga kuma waya nan akwai sim card a ciki had'e da numbers in "boss duk abunda Ku ke buk'ata Ke da k'awaye ki a lokacin biki sai ki kira "boss gobe insha Allah Zan zo na fita da Ke  'kawayeki Ku kai wa 'yan uwa da abokai arziki katin gaiyyata
[11/10 7:01 pm] Jeeddah Aliyu🌹: Har Bala yadasa aya a zance shi Haleesa bata ce komai ba gani ta yi shiru yasa yace ranki yadad'e kin yi shiru ba ki ce komai ba"?

Saida tasauke Numfashi daga bisani tace Zai fi kyau kayi min Serving in number domin bana tunani zan iya "calling in wani"
"Bala d'an murmusa yafito da Biro daga gaban aljihu shi ya rubuta number shi akan kwalin da yashigo da shi ya yi mata sallama yafice.
Saida Haleesa ta share tsawon "10 minutes kafin tashiga cikin gida kaitsaye tashiga d'akin Ammi ta ajiye kwalin hannunta bata ce da Ammi komai ba ta nufi d'akinta.

```WASHE GARI ```

Tun misali k'arfe 10:30am Bala ya zo yadauki Haleesa da k'awaye ta suka tafi raba "invitation saida suka share kwana ki 3 suna raba invitation tun safe in suka fita sai da yamma lis suke dawowa.

```ON TUESDAY ```

Ita ce ranar da aka fara gudanar da shagalin biki kamu za'a yi a gidan Aunty Juwairiyya tun daga Lagos Madam Hindu ta yo "Booking d'in Aunty funke da yaranta suka k'awata gidan Aunty Juwairiyya da "Decoration yayinda Aunty funke za ta yi wa Amarya Haleesa Makeover tun lokacin da Haleesa tashiga "bathroom da suna wanka ta rufe k'ofa tun Aunty funke tana saka ranta fitowar ta har tagaji da jira tafito daga bedroom ta nufi parlour wurin Aunty Juwairiyya ta Fad'a mata abunda ke faruwa a harzuk'e Aunty Juwairiyya tanufi bedroom d'in tadinga knocking in k'ofar had'e da kiran sunan Haleesa shiru kamar ba mai rai a ciki Haleesa da ke Zaune dirshan a tiles d'in bathroom tasaka kanta tsakiyar cinyoyinta sai faman shashekar kuka take bata tunani akwai Wanda ya isa yasaka ta ta bud'e k'ofar nan har sai sun gama shirme su, jin yadda Aunty Juwairiyya take duka k'ofa yasa Haleesa tace Aunty ki daina wahalarda kanki bara ta6a bud'e k'ofar nan har sai kun gama shagalin bikinku.
Cikin 6aci rai Aunty Juwairiyya tace a gidan uban wa Haleesa kika ta6a gani anyi kamu ba Amarya"?
"Daga yau za'a fara a kaina Haleesa tafad'a had'e da murgud'a baki...

Jeeddah Aliyu🌹
[10/24, 11:44 AM] +234 813 417 9191: [15/10 4:53 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣the sweetest love_❣

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```®NWA```

°°°°```In Dedication```°°°
*To Shehu Aliyu family's*
```

```62```

Note:- _na yi kuskure a wurin fadar sunan garin a farko labari mai karatu zai ji nace yola a wani wurin kuma zai ji nace Yobe to yola ne ba Yobe da fatar za'a gafarce ni_

_10:30am_

"Habeeb na tsaye gaban "dressing mirror yana sharce suma shi da "Comb Mus'ab ya murda handle ya shigo ta mirror ya had'a ido da Habeeb ya kyalkyale da dariya da sauri Habeeb ya had'e rai ya d'auke kai yace banaso iskanci Mus'ab hali yanzu ka fara kaini bango tun dare jiya ka ke ta fama yi min dariya shin akwai uban da baya mafalki ne da za ka sakani a gaba kana dariya, Mus'ab yak'ara kyalkyalewa da dariya har yana dukan gefen bed abunda yak'ara harzuk'a Habeeb ya jefa masa comb in hannunshi ka ga Mus'ab na rok'e ka da ka had'a "luggage in ka ka bar min gidana Mus'ab ya tsagaita da dariyar da yake yi au abin har da su kora to ba ida zan tafi ina nan tare da kai har sai Amarya ta zo"
Amma kuma kaima kana da gida sai ka je gidanka ka tare ka jira zuwan Amarya ni kan bara iya cigaba da zama da mahaukaci"
Kyalkyalewa da dariya Mus'ab sake yi yace to ae ni narasa gane tsakanin ni da kai waye mahaukaci ko ka manta kuka ka ke yi wa mace a mafalki wannan ke nuna cewa kai d'in zarare ne Mus'ab bai jira me Habeeb zai ce ba ya juya yafi ce daga d'akin yana dariya shak'iyanci Habeeb ya bi shi da kallo daga bisani ya ja tsoki kai amma yarinya nan ta gama da ni me  ke shiri faruwa da ni da na ke mafalki na sadu da ita"?
Lallai sai na musgunawa yarinya nan sai ta yi danasani zuwa mini a mafalki cike da takaici ya murd'a handle yafi ce Mus'ab ya tarar akan dining table yana breakfast batare da ya dube ida yake zaune ba ya ja kujera ya zauna, chef Peter ya yi masa "saving har suka gama breakfast ba Wanda ya tankawa d'an uwanshi Habeeb ya dube ida yake zaune yadauke kai in ka ga dama katashi mu tafi Mus'ab ya yi murmushi had'e da cewa gaskiya tsarin gidanan ya burgeni matuk'a ba k'aramin more rayuwa za Ku yi kai da Amarya Haleesa wai... Ina nufi dream girl domin Haleesa bata kai matsayin da za'a more rayuwa da ita ko ba haka bane aboki na"?
Ran Habeeb yak'ara 6aci jin yake kamar ya zabgawa Mus'ab mari ya ja tsoki ya fice daga parlour Mus'ab ya Mara masa baya yana dariya har suka iso gidan Madam Hindu Mus'ab yana tsokanar Habeeb tun yana jin zafinshi har yagaji ya zuba masa na mujiya.

_8:00pm_

```HALEESA```

Duk lokacin da Haleesa ta tuna cewa saura kiris ta zama mallaki Habeeb Lamido sai ta zubar da hawaye ta yi nisa a tunani Aunty Juwairiyya tashigo Haleesa ki tashi ki je wanka Aunty funke na jiranki za ta yi miki makeover na tafiya _Dinner_ Haleesa ta kwa6e fuska wai ni Aunty dole ne sai na je dinner"?

"Dole ne Haleesa sai kin je don haka ki tashi ki je ki yi abunda na umurce ki Karki 6atawa mutane lokacin"
Haleesa ta shar6e hawaye na fahimce cewa Aunty Juwairiyya ko tausayi na bakyaji ta kare magana had'e da mik'ewa Aunty Juwairiyya ta tabe baki sai anan a gaba za ki gano alkhairi da ke cikin wannan aure"
Tun da zuciyata bataso
 Ya za'a yi na fahimce akwai alkhairi a wannan aure kawai zan yi biyayya da dukkan Umarni da ki ka bani domin banida mafita bata jira jin abunda Aunty Juwairiyya za ta fad'a ba tashige "bathroom.
"Aunty Funke tsantsarawa Haleesa kwalliya wance tafi ta jiya kyau da tsaruwa Amarya Haleesa ta yi matuk'ar kyau cikin wedding gown "golden colour" da head blue colour kafarta sanye da blue hill's hannaye da k'afafuta sun sha Zane k'umshi ja da baki Haleesa ta nemi gefen bed ta zauna ta zabga tagumi gani take wannan abun kamar almara hawaye suka wanke mata fuska da sauri Aunty Funke ta rik'o hannunta haba! Haleesa me yasa bakya gajiya da kuka"?
Haleesa ta sada kai k'asa had'e da ja majina da k'arfi tana k'ok'ari danne hawayeta  Aunty Juwairiyya tashigo d'akin ta yi turus ya akayi ne sarkin kuka"?
Ki sausautawa kanki Haleesa wannan kuka bara ya K'ara ki da komai ba kullum kuka abu yak'i ci yak'i cinyewa sai hawaye ki sun kare a wofi tashi mu tafi karki 6atawa mutane lokacin"
Da kyar Haleesa ta mik'e hawaye na ta ambaliya akan fuskarta Aunty Funke ta rik'e ta Haleesa ki daina kuka karki 6ata kwalliyarki kinji"?
Saida tak'ara Jan majina sannan tad'aga kai Aunty funke tayago tissue ta yi wiped in hawaye fuskarta ta k'ara Shafa mata powder sai ga fuskar Haleesa na kyalli kamar ba ita ne tagama kuka Aunty Juwairiyya ta wuce gaba Haleesa da Aunty Funke suna biye da ita har zuwa "Compound Aunty Funke ta bud'e mota kirar "Lexus 2016 model" ta zaunar da Haleesa cikin dusashiya murya Haleesa tace Aunty bara iya tafiya ni kadai ki kira Zainab da khadeejat mu tafi tare'
"Aunty Juwairiyya ta kya6e baki tace tuni Zainab da khadeejat suka tsofa a "Hotel in da za'a yi dinner in kin je kya had'u da su Aunty Funke ta rufe mata k'ofa driver ya ja mota yayinda Aunty Juwairiyya da Aunty Funke suka shiga ta su mota had'e da marawa motar da Haleesa take baya.

```HALL```

Motar su Haleesa ta yi parking har driver ya bud'e mata k'ofa ta zuro k'afarta d'aya Hannah ta dakatar da ita karki fito Haleesa koma ciki sai yaya Habeeb yak'araso za ki fito"
Yatsine fuska Haleesa ta yi batare da tace komai ba ta mayarda da k'afarta tsawon _6-7 minutes_ ta dauka zaune a mota tana jiran k'arasowa Habeeb sai gashi ya iso tare da Mus'ab"
Hannah ta bud'ewa Haleesa k'ofa tafito Haleesa na kyalla ido ta sai akan Habeeb Lamido yana sanye da suit "sky blue ya yi matuk'ar kyau yafito balarabe sak gabanta ya yanke yafad'i jikinta yafara "sharking kamar wance "electric shock ya ja da sauri ta d'auke kai a Zuciyarta tace shi wannan wai bashida kayan ne hatta da ranar Aurenshi suit zai saka "huh! Ta tabe baki jin ta yi an rik'e hannunta tad'ago da sauri Hannah ta gani damk'e da hannunta ta nufi wurin Habeeb Lamido da ita shima ta rik'o hannunshi ta had'e da na Haleesa ba yadda ya iya dole ya rik'e
```

hannunta a lokacin d'aya wani shock ya ja su Wanda ya yi sanadi dagowarsu suka had'a ido kallon k'asan ido yake mata yayinda Haleesa takasa jure kallon ta d'auke "eye's ball in ta k'awaye Haleesa da friends in Habeeb Lamido suka fara haska su da camera wayoyinsu hannaye su na sark'e suka fara tattak'i bisa lallausar blue carpet Habeeb ya lalla6o yatsu Haleesa ya matse su da k'arfi tsanani zafin ratsa ta wabi irin zufa ya karyo mata jin take kamar za ta saki fitsari ta bud'e baki da kyar cikin wahalaliya murya da ke nuna ba k'arami zafin take ji tace it's hurt yaya Habeeb Dan Allah kadaina ko kallonta bai yi ba sai ma 'kara matse ta da ya yi a haka har suka k'arasa akan high table da aka tanada domin su a tunani Haleesa in suka zauna Habeeb zai sake mata hannu sai taga sa6ani hakan cigaba ya yi da murza mata yatsu da k'arfi yake murza su
[15/10 7:14 pm] Jeeddah Aliyu🌹: Haleesa tad'ago idanu ta taf da hawaye ya kalle Habeeb fuskarshi a had'e ya dank'ara mata harara da sauri ta sunkuyar da kai, Mus'ab yak'araso yadafa kafadar Habeeb yakai bakinshi dai-dai kunnenshi ya yi mishi rad'a haba! Ango na Haleesa da leesa ka Saki ranka mana duk yawan jama'a da ke wurinan saboda Ku suka zo amma kai wani had'e fuska "Habeeb yatsine fuska ya k'akaro murmushi dole Mus'ab ya yi dariya maras sauti ya d'an daki kafadar Habeeb "Good job abokina ya juya wurin Haleesa yace Amaryamu ya haka naga kin wani had'e fuska Dan Allah ki saki ranki ki k'awata kyakyawa fuskar nan taki da sanyaye murmushi Haleesa tasaki murmushi yak'e mai kama da mai so yi kuka "Ma'aruf MC ya umurce ango da Amarya su fito su d'an taka rawa Jikin Haleesa yadauki rawa tsawon rayuwarta bata ta6a rawa ba Habeeb, ya mik'e yad'an rankwafa dai-dai kunnen Haleesa kamar zai rada mata abun arziki ke! Villager tashi mu je karki yarfa ni a gaban jama'a ace Habeeb Lamido ya auro 'yar Daji tad'ago dara-dara idanuta masu d'auke da kwalla tasauke su akan fuskarshi alama ya yi mata da girar idonshi tadaina kallonshi da sauri ta d'auke idanuta yana rik'e da hannuta suka nufi tsakiyar fili Haleesa kan tsaye ta yi k'ik'an yayinda Habeeb Lamido yake juyi da hannaye Haleesa tuni filin ya rikice sai ruwan naira ake musu Maryam ta ratso tsakiyar filin ta nufi wurin Habeeb ta 6alle pose in ta taciro bundle na N1000 tasoma yi masa lik'e ta fakaci idanu mutane ta bangaje Haleesa ta matsa daf da Habeeb kamar za ta shige k'irjinshi kallo d'aya Haleesa ta yi musu ta dauke kai nan take ta ji wani bak'o yanayi na shigarta Mus'ab ya ankara da waina da ake toyawa ya yi wa Habeeb rad'a wani shegen murmushi yasake yarik'o hannun Haleesa su ka koma wurin zamansu sai misali k'arfe _12:15am_ aka tashi daga dinner har izuwa lokacin  Habeeb na rik'e da hannun Haleesa yana Gana mata azaba ta hanyar matsi mata yatsu har wurin mota Habeeb yaraka Haleesa ya matsa daf da k'ofar mota ya yi k'asa da murya kamar mai rad'a Ina fatar za ki k'ara jajircewa ki zama jaruma domin zama da Habeeb Lamido sai jarumar mace ya wani dage girar sama oh! Kina mini kallon marigayi saurayinki koh"?
To ki yi gaggawa ki fitarda da hakan daga ranki na barki lafiya Amarya taa yak'arasa magana had'e da sakin tsadad'e murmushinsa yabar Haleesa sake da baki tana mamaki shu'umanci sa.

```ON FRIDAY ```
_2:30:pm_

Tun daga farko layin su Haleesa har zuwa karshe sa d'an mutum ne ba matsaka tsinke tarin jama'a 'yan dauri aure ne Habeeb Lamido na hango cikin farar shadda d'inki babbar Riga kanshi
```

d'auke da farar hula kum6e Mus'ab da khaleel sun saka shi tsakiya sai fama washe hak'ora dole yake k'arfe _2:40pm_ dai-dai dunbanni jama'a suka sheda daurin auren Habeeb Lamido da Haleesa Usman akan sadaki naira dubu d'ari ana Shafa fatiha gaban Habeeb yafad'i a zuciyarshi yace shikenan yarinya nan da tsana ta zama mallaki na ya yi murmushi had'e da Shafa gajerar gemun shi.

_5:00pm_

Aka gudanar da walima inda aka gaiyyato malama Hafsat Umar ta yi Nasiha akan zamantakewar Aure tafad'i irin azabobi da Allah tanardawa duk mace da bata biyayya ga sunnah ma'aiki s.a.w bayan gama wa'azi yaran Aunty funke su dinga raba katuwar jakka mai d'auke da pic d'in Amarya da ango in ka bud'e jakka za ka tararda 'yan uban kaya daga ciki har da atamfa mai kyau gaske tun lokacin da aka tashi daga walima Haleesa keta faman rusa kuka ta tsorata murtuk'a da Nasiha da malama Hafsat Umar ta yi nan take ta k'udiri anniya yi wa Habeeb Lamido biyayya koda ace zai dinga yanka naman jikinta bara ta ta6a tsalleke umurni sa.

_9:44pm_

Haleesa na durk'ushe a gaban iyayyeta suna kora mata Nasiha duk akan zaman aure yayinda Haleesa ke kuka kamar ranta zai fita Baffa yarik'o hannunta yanufi k'ofar gida yasanya ta cikin mota ya mik'a mata Al-qur'ani da pray mat had'e da casbaha yace Haleesa ki rik'e wannan domin shine magani kowace matsala ta d'an Adam Allah yabaku zaman lafiya yabaku zuri'a dayyaba Haleesa tak'ara fashewa da wani sabon kuka Baffa ya umurce driver yaja mota su tafi har aka fita daga unguwarsu tana kuka kamar ranta zai fita....

Jeeddah Aliyu🌹
[10/24, 11:44 AM] +234 813 417 9191: [13/10 6:02 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```®NWA```

°°°°```In Dedication```°°°
*To Shehu Aliyu family's*

```61```

Matuk'ar na kirga 3 ba ki fito ba wallahi zan kira Baffa a waya na Fad'a mishi abunda ki ke shirin

aikatawa nasan duk iya shegenki kina tsoro Baffa"
Sosai Haleesa ta tsorota da jin furucin Aunty Juwairiyya ba shiri da mik'e ta bud'e k'ofa suna had'a ido da Aunty Juwairiyya wance ta cika ta yi fam cike da takaici ta gallawa Haleesa uwar harara d'auke kai Haleesa ta yi kamar ba ta ga Aunty Juwairiyya na harara ta, ta ra6a gefen ta za ta wuce cikin Zafin nama Aunty Juwairiyya ta fisgota ta igizata cikin "bathroom koma ciki don gidanku ki yi Wanka ko kina nufi bara ki yi Wanka ba"?
Idanuta taf da kwalla tace to ni Wanka me zan yi"?
"Bansaniba Aunty Juwairiyya tafad'a a zafafe tacigaba da magana ta hanyar nuna tsanani 6acin ranta wallahi Haleesa ki kiyaye ni sai na yi mummuna sa6a miki idan ki ka sake kwatata irin Wannan shashanci so ki ke mutane duniya su zage mu ace mu yi miki Aure dole.
"Haleesa ta shar6e hawaye had'e da k'argame k'ofa kuka takeyi sosai har ta gama Wanka tana kuka, idanuta sun yi luhu-luhu tana fitowa Aunty Funke tafara aikin nata na tsatsara mata Make-up ta kece raini ta yi matuk'ar kyau Aunty Funke ta fito da "Wedding gown ash& black colour ta mik'awa Haleesa tace ga wannan ki saka Yatsine fuska Haleesa ta yi ta Wani turo baki da ya masifar K'ara mata kyau tace me zan yi da Wannan abar"?
Galala Aunty Funke ta yi da baki tana duban Haleesa "OMG! Ni kan banta6a gani "Bride da irin wannan hali ke da yakamata ki yi farin ciki wannan fa ranar ki ce "Humm Haleesa tafad'a had'e da kyabe baki bata k'ara bin ta kan Aunty Funke ta juya tasanya inner wear's daga bisani tasanya gown d'in Aunty Funke ta rufe mata zip ta daura mata "black colour head sai ga Haleesa ta yi dass da ita tubarakallah masha Allah" Zainab da wasu school mate d'inta suka take mata baya har Zuwa "compound d'in da za'a yi kamu gidan yacika taf ba masaka tsinke yayinda 'yan "police bands su ka k'awata wurin da kid'ansu mai matuk'ar dad'i da ratsa Zuciya Hannah tayi "Parking motar ta ta fito ita da k'awaye ta ta nufi "high table wurin Amarya Haleesa ta d'a yi hugging in ta Haleesa tasaki Murmushi yak'e Hannah tace "Wow! Ki yi matuk'ar kyau matar yaya Habeeb bara na d'auke ki "Pic's na turawa yaya Habeeb nasan dole yarud'e ya nemi natsuwa da kwaciyar hankali shi yarasa tana magana had'e da haska Haleesa da camera wayarta yayinda Fad'uwar gaban Haleesa ta yawaita Jin takeyi kamar za ta kurma ihu har Hannah ta gama budirinta Haleesa na bin ta da ido, "2 minutes matar yaya Habeeb Hannah tafad'a had'e da juyawa tana dannar wayarta tabar Haleesa cikin halin k'unci da tsoron yadda zata rayuwa da Wani d'a namiji ba yaya Habeeb d'in ta ba.
Cikin Salon tafiyar k'asaita da son nuna ita d'in 'yar wani ce ta tunk'aro "high table wurin Haleesa yayinda muk'arabanta suka take Mata baya a yadda tashigo da kuma yanayi tsarin Make-up in ta za ka yi tsanmani ita ce Amarya tun kafin tak'araso Haleesa ta gane ta a zuciyarta tace me kuma wannan 'yar iska ta zo yi anan"?
Maryam da Zeely suka k'arasa wurin Haleesa sauran muk'arabanta suka nemawa Kansu matsugunni daf da kunne Haleesa ta kai bakinta kamar za ta Fad'a mata abun arziki duk da Haleesa ta tsorata amma sai ta dake ba na zo nan ne don na tayaki murna nassara auren d'an masu kud'in da ki ka yi na zo ne na yi miki albishir da mummuna tanadi da na tanada miki zan bi kowace hanya domin gani na nisanta ki da duk Wani farin ciki da kike kwad'ayi samu a gidan Yaya Habeeb nayi alk'awali sai na mayarda rayuwarki, tamkar ta kare da ke yawo akan bola yana neman mushe sai kin yi danasani aure abunda na ke ```SO``` tak'arasa magana had'e da Murmushi ta wani kwanto a jikin Haleesa tace Zeely haska mu da camera Zeely ta saita camera wayarta dauke su photo Maryam ta shafi checks d'in Haleesa da d'an yatsata tajuya tana

Murmushi Wanda da Haleesa za ta k'ura mata ido kaitsaye za ta gano na yak'e ne ga kuma zafafa hawaye shinfid'e a eye's ball in ta Zeely ta Mara mata baya suka fice daga gidan dama ba kamu suka zo yi ba sun zo ne don su aiwatar wa da Haleesa gargad'i mai cike da barazana Haleesa ta bi Mutane da ke Wurin da kallo tasauke ajiyar Zuciya mamaki da tsoro suka lullu6e ta k'irjinta na duka uku-uku kamar zai tsage gida biyu tafara zance zuci to ita wannan mai kama da "snooker stick me ta ke nufi da ni ne humm"?
Ba shakka wannan mugun nufi ta kala d'aya ne da na Habeeb Lamido a duk lokacin da ya yi nassara lullu6e Zuciyata da zazafa kalamai daga karshe sai ya wanke ni da Murmushi mugunta ita ma Wannan girl friend in shi haka ta yi min Wannan ke nuna tafiyar su d'aya lallai kuwa akwai kwaram tsakanina da ita in har shi Habeeb Lamido ina tsoronshi ae ita bana tsoronta zan nuna mata cewa ni ma ba kanwa lasa bace, sai na tabbatar mata kalamanta duk burgace da rashin samu nassara Haleesa ta yi kyaci cike da buri k'ara aragama da Maryam.
Sai daf da sallah magariba aka watsi daga kamu Hannah na manne da Haleesa sai faman zuba mata surutu take cike da gajiya da surutu Hannah Haleesa tace ni kuwa Hannah in tambaye ki mana"?
Hannah ta washe hak'ora had'e da daga kai"
Haleesa ta gyara zamanta ta yi k'asa da murya Hannah wacece doguwar yarinya nan mai sanye "dark blue lace wance na hango ki tsaye da ita ina nufi Ku na da alak'a da ita"?
Murmushi Hannah ta yi tace ta yi miki Wani laifi ne"?
A'a kawai na tambaya ne saboda na ga tana da kirki da son mutane kuma ga ta da saurin sabo Haleesa tak'arasa magana tana kyabe baki kafin Hannah tafara magana saida tasauke ajiyar Zuciya tace k'anwar marigayiya Salma ce matar yaya Habeeb wance tarasu.
Shiru Haleesa ta yi tana nazari kalman Hannah daga bisani tace amma ba wata alak'a tsakaninta da yaya Habeeb"?
Hannah ta tsorata da wannan tambaya da Haleesa ta yi mata nazari take yi irin amsa da za ta bata shigowar Aunty Juwairiyya ce ta yi sanadi katsiwa Hannah nazari da sauri Hannah ta mik'e tsaye Matar yaya Habeeb zan wuce gida me ye sak'onki a wurin yaya Habeeb"?
"Haleesa ta ja 'yar siririya tsoka karaf ta had'a ido da Aunty Juwairiyya gani irin mugun kallon da ta watsa mata batasan lokacin da tace "My regear to him"
Bata fuska Hannah ta yi haba! Haleesa gaskiya gaisuwa ta yi kad'an ki d'an k'ara da wata kalma wance za ta hana shi bacci ta k'are magana tana 'yarfe hannu  shiru Haleesa ta yi tarasa abunda za ta furta ga Aunty Juwairiyya ta kafe ta da ido jira take ta ji abunda za ta Fad'a chan dabara tafad'o mata ta rok'o hannun Hannah zo mu je na rakaki a hanya na gaya miki abunda za ki fada masa suna fitowa Haleesa ta mitsine mata hannu ashe bakida kunya Hannah a gaban Aunty Juwairiyya kike irin wannan Zance"?
Hannah ta kyalkyale da dariya tace cab! Lallai kuwa Haleesa kinada aiki domin yaya Habeeb mutum ne mai son rayuwa jin dad'i gaba d'aya tsarin rayuwarshi ta turawa ce gwara tun wurin ki koyi yadda ake tarairaya miji a gaban kowa ki yi fatali da wannan kunyar taki cike da takaici Haleesa ta ja tsoki "You know what"?
Hannah ta girgiza kai "Bana son yayanki Hannah babban wulak'anci da zan yi wa kaina na yi sake Zuciyata ta kamu da sonshi ballatana ina da yak'ini cewa Zuciyata bara ta6a son wani d'a namiji a dalilin na mallakawa marigayi Yaya Habeeb ita zan aure yayanki ne saboda Mahaifyarku ba wai don ina sonshi ba kamar yadda shima banida muhalli a zuciyarshi tana

k'are magana ta juya cikin zafin rai da tafarfasa zuciya Hannah tasha gabanta karki biyewa Zuciyarki Haleesa tasa ki aikata abunda zai sanya mutane su gano cewa ba aure soyayya Ku ka yi ke da yaya Habeeb hakan wata dama ce da za ta ba wa mak'iyaki nasara akanki" Yatsine fuska Haleesa ta yi daga bisani tace " I don't care what's they people say oll I know banaso Habeeb Lamido kamar yadda shima baya sona na tsane shi kamar yadda ya tsaneni that's oll tana kare magana ta ra6a ta gefen Hannah tashige cikin gida Hannah ba ta yi mamaki jin wad'annan zafafa kalamai daga bakin Haleesa, domin tasan za'a yi haka ta yaya mutane da ke jinyar Zuciyoyinsu ace za'a had'a su aure da wannan zance zuci ta ja motarta ta nufi gida saukin ta d'aya tuni ta sallame k'awayeta da yanzu a gabansu Haleesa za ta furta wad'annan kalamai masu zafin gaske.

```HABEEB LAMIDO ```

Habeeb da Mus'ab na Zaune a parlour madam Hindu da ke upstairs ga kuma tarin invitation card's na dauri aure zube a gabansu, Habeeb ya ja tsoki Mus'ab yad'ago ya galla masa harara wannan wane irin iskanci ne tun d'azu ka ke ta fama yi wa mutane tsoki aure nan fa ba dole bane ko yanzu za ka iya tunk'ara Mom ka fad'a mata ba ka yi har Mus'ab ya dasa aya Habeeb yana kallonshi ya tabe baki had'e da Shafa sumar kanshi kaitsaye Hannah tashigo ta nufi kujera da Mus'ab yake Zaune shima yana ganinta yafara zabga Murmushi Yaya Mus'ab dama kana gidanan ba ka tafi ba"?
Ke ji ki da wani Zance Hannah ina zan tafi in bar wannan shashasha, yak'arasa magana yana nuna Habeeb da yatsa Hannah ta rufe bakinta tana dariya tasan  Mus'ab ne mutum na biyu da ke tilasawa Habeeb ya yi abunda bashida ra'ayi akai tana dariya tafito da wayarta ta yi "scrolling pic's in da ta yi wa Haleesa tace yaya Habeeb "take a look ta mik'a masa phone in  yana daura idanushi akan screen d'in wayar yaci Karo da fuskar da yatsana wawa tsoki ya ja had'e da cillawa Hannah wayarta saura kiris tafad'i Hannah ta chafe ya mik'e cikin angry face yace "how dare you show me dis nonsense" wannan ya kasance shine na farko na kuma karshe da za ki k'ara nuna mini fuskar wannan mummuna yarinya tashi ki bar parlour nan
Jiki na rawa Hannah ta tashi saboda ta tsorata da yadda Habeeb yataso mata kamar zai cinye ta Mus'ab ya tabe baki Habeeb yakoma mazauni shi zuciyarshi sai fama tafarfasa ta ke.

```2:45am```
Da gudu Haleesa tafito daga bedroom tana rik'e da k'asan wedding gown d'in da take sanye da ita tanufi parlour Habeeb na zaune akan 3 Star yana duba magazine kaitsaye tafad'a K'irjinshi ba bu shiri ya jefar da "Magazine  hannunshi yasaka ya matse ta gam har ya bud'e bakinshi zai yi magana  Ta had'e bakinta da nashi tana tsotsa tsawon lokacin tadauka tana rikita mishi "brain da salonta daga bisani ta kamo hannye shi tadaura a bayanta "very slowly take magana yaya Habeeb ka zuge min zip yana bud'e mata zip d'in ta cire gown in ta yi flinging da ita ta rage daga ita sai inners wear's tak'ara shigewa jikinshi idanu ta na lumshe take 6alle masa bottoms har ta yi nasara raba shi da rigar jikinshi Cikin zumudi manna bakinshi cikin nata daga nan Komai yacigaba da wakana Haleesa ta yi matuk'ar gigitashi ta rikita masa lissafi bayan komai ya kamalla yana k'ank'ame da ita kuka yake yi tamkar k'aramin yaro _"I love you leesa you are the only woman I loved "Tell me leesa you love me_ yafad'a yana lek'e fuskarta yatsine fuska ta

yi yak'ara marairaice murya  "please leesa say it's you love me....kai! Habeeb wawa dukan da Mus'ab ya narka masa ya falkar da shi daga baccin sa mai cike da mafalki Haleesa  Habeeb ya mik'e zaune ya shafi fuskarshi  a tsorace yabi tafin hannnunshi da kallon " Habeeb Wacece leesa"?
Tambayar da Mus'ab yajefa masa kenan kallon mamaki Habeeb yake masa a kasalance yace "I don't know"
"Look malam karka rena mini hankali ya kana mafalki yarinya har da saduwa da ita a mafalki kana mata kuka gaba d'aya ni ka hanani bacci   ita ya akayi tayi winning heart in ka har kana mata kuka wannan ke nuna you are already in love with her c'mon dude tell me who is this lucky girl"?
Habeeb ya share zufa had'e da hawaye a zafafe yace "I don't know anything About whats you are saying yana kare magana yadiro daga bisa bed yanufi "bathroom yabar Mus'ab sake da baki dama akwai wance Habeeb yakeso shine tsawon wannan lokacin bai ta6a Fad'a mini ba"?
"Huh! Habeeb shu'umi ne ko me yasa ya amince da za6in Mommy bayan akwai wata a zuciyarshi"?
Wacece Leesa me yasa Habeeb ya sadaukar da soyayya da yake mata ya amince zai aure Haleesa"?
Amma kuma a mafalki shi naji yana rok'o ta tace   Sonshi "which means bata sonshi shi kadai ke hauka shi Mus'ab ya kyalkyale da dariya Habeeb ya bud'e k'ofar bathroom yafito ya yi tsaye yana kallon yadda Mus'ab ke kwasa dariya a tsakiyar dare ya girgiza kai yanufi wardrobe yasanya jallabiya ya haye bed ya yi kwanciyarshi tun yanaji dariyar Mus'ab har bacci ya yi awo gaba da shi....

 Jeeddah Aliyu🌹
[10/24, 11:45 AM] +234 813 417 9191: [20/10 11:06 am] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```®NWA```

°°°°```In Dedication```°°°
*To Shehu Aliyu family's*

Note:- _Ina ba Masoya ni da yaya Habeeb hankuri a dalilin rashin post da ba nayi akai-akai har wasu na k'orafi na cika Jan rai yakamta ku yi min uziri ni ma ba'a son raina hakan take faruwa_

```63```

"Har suka k'araso unguwar Haleesa bata saniba domin kanta na tsakiyar cinyoyita tana

shassheka kuka, katsaye direban yanufi had'ad'e gate d'in gidan Habeeb Lamido ya yi tsaye ayarin motacin da ke bayan shi suka bi sahunshi saida suka share tsawon _10 minutes_ a tsaye saida security camera in da ke manna a gida suka gama "screening in motaci daga bisani gate d'in ya bud'e kanshi tafiya mai d'an nisa sukayi kafin su tararda k'aramin gate anan "gate man yake zaune yataso ya bud'e musu gate bayan driver ya gama parking yafito ya bud'ewa Haleesa k'ofa inna mairo ta rik'o ta gaba d'aya jikin Haleesa lullu6e yake cikin white colour lafayya ko fuskarta ba'a gani inna Mairo ta rad'a mata ki yi addu'a kafin mu Shiga ciki sannan kuma ki shiga da k'afar dama Aunty Mami ce ta jagorance su inna mairo zuwa bedroom d'in Haleesa inna mairo ta zaunar da ita a gefen bed tak'ara yi mata nasiha gani yadda Haleesa take ta rusar kuka ta yi matuk'ar ba inna mairo tausayi take ta tuna da d'ata Marigayi Habeeb da yanzu gidanshi za'a kai Haleesa ta kuma tabbata cewa da ace gidanshi za'a kai Haleesa da ba abunda za ta yi wa kuka idanu inna mairo suka ciko da hawaye da sauri ta fice Zainab da khadeeja suka saka Haleesa a tsakiya suna lallashi kamar suna k'ara zugata ne domin wani sabon babi ta bud'e na kuka k'arfi _10:20pm_ dai-dai Su Zainab suka ce za su wuce yayin da Haleesa ta k'ank'ame Zainab tana kuka "Zainab karki tafi ki barni ba zan iya rayuwa da Habeeb Lamido saboda Zuciyata har yanzu yaya Habeeb takes....da sauri Zainab tarufe mata baki haba! Haleesa me yasa bakyaji magana"?
Ko kin manta cewa a yanzu kina matsayi matar wani Dan Allah ki yak'i zuciyarki ta daina ambato yaya Habeeb gudun daukawa kanki zunubi Haleesa ta zare jikinta daga na Zainab tafad'a bisa bed ta cigaba da shasshek'ar kuka har Zainab ta yi yunkuri nufar wurinta Khadeejat ta dakatar da ita ki kyalleta kawai domin na tabbata kowace kalma za ki furta mata halin da take ciki bara su yi tasiri akanta ae ita ba jahila bace tanada ilimi tasan abunda yadace ta kuma San abunda bai dace ba tana k'arasa magana tarik'o hannun Zainab suka fice gidan ya yi tsit gaba d'aya 'yan rakiya amarya sun kama gabansu.

_11:15pm_

```HABEEB LAMIDO ```

Bala yadanno hanci mota a farfajiya gidan ya nufi parking space ya yi "parking ya za gaya ya bud'ewa Habeeb k'ofa yafito yana sanye da "black colour Jeans da blue colour long sleeve shirt yasha stocking cikin yanayi da ke nuna ya kwaso gajiya yanufi cikin gida a main parlour ya tsaya ya yi switch off in light ko kallon bedroom d'in Haleesa bai yi ba ya hura upstairs yanufi dak'inshi bayan ya yi wanka ya sanya pajamas ya haye bed Sam ya manta da wata aba Haleesa tsanani gajiya da ya kwaso yasa bai d'auki dogon lokacin bacci ya yi awo gaba da shi.

```HALEESA```

Tun tana kuka da hawaye har tadawo kukan zuci ko kayan jikinta kasa cirewa ta yi sai fama juyi take zance ta rufe k'ofa bai ma taso ba saboda tasan ko kare hauka ya cije Habeeb Lamido ba yadda za'a yi ya shigo d'akinta sai kawai ta cigaba da zance Zuci sai kusan asuba bacci ya yi nassara kwasheta.

```WASHE GARI ```
_10:08pm_

Haleesa ta falka daga bacci a gauggauce ta gyara "bedsheet ta jona "burned a "socket ta zuba turare wuta d'akin ya gume da sanyaye k'amshi daga bisani tashiga wanka bata d'auki dogon lokacin ba tafito ta shirya cikin atamfar "Super Sheraton blue da touch in pink ta yi matuk'ar kyau tafito amarya sak batare da ta daura Dan kwali ba ta yane kanta da d'an siriri "veil pink colour tanemi gefen bed ta zauna ta rakka d'an uban tagumi k'ugi da cikinta yake yi yasa babu shiri ta mik'e ta murde handle ta bud'e k'ofa kad'an ta lek'a wayam ta hangon parlour ba kowa a hankali take sand'a kamar barauniya ta dafe da kwakwaso tana kallon tsarin parlour ya yi matuk'ar yi mata kyau "everything's da ke parlour red & yellow colour ne tasauke numfashi a baiyane tace "amazing that's my favourite colour" daga bisani tanemi d'aya daga cikin "Royal chairs d'in da suka k'awata parlour ta zauna tunani take ina za ta nemo abinci za ta sakawa hanjinta tun, kafin yunwa da takeji ta yi mata illah 'kamshi turare "intense men da ta shak'a ya haddasa mata fad'uwa gaba karar "footsteps da taji ana saukowa daga upstairs yak'ara jefata cikin matsananci tsoro cikin d'an k'ank'ani lokacin zuciyarta ta motsa yayin da hankalinta yatashi tasoma fargaba had'uwa da Habeeb Lamido ko wace irin tarba zai yi mata sanye yake ciki "three quarter red colour da white armless shirt k'afarsa rufe cikin white combat boot hannaye shi na zube cikin aljihu wandon fuskarshi a had'e yak'araso cikin parlour a wulaqance ya dube inda Haleesa take zaune ya Ja 'yar siririya tsoka yanemi nesa da ita ya zauna tsawon "4-5 minutes da zaman shi ya d'ago ya kalleta har yanzu kanta na k'asa tana wasa da yatsuta ranshi ya yi mugun b'aci wannan 'yar k'auye tana nufi bara ta gaishe ni ba yafad'a a cikin zuciyarshi Cike da izza yace ke! A rud'e Haleesa tad'ago idanuta suka firfito alama tsoro ke! Ba da ke nake magana ba"?
"Na"am ta Fad'a tsoro shinfid'e a fuskarta kina nufi bara ki zo bane"?
Jiki na rawa ta mik'e tanufi gabanshi tayi tsaye had'e da sada kai k'asa ta k'asan ido yake kallonta kamar Mai rad'a ya furta ba ki iya gaisuwa ba koh"?
Sam Haleesa ba tayi zato jin wannan kalma daga bakinshi ba ta hadiye yawu da kyar tace na iya mana"
Yad'ago eye's in shi yana tsotsa bakinshi kamar mai tsotsa sweet daga bisani ya ja iska kamar Wanda ya ci yaji da sauri Haleesa tadauke kanta da bari kallonshi "tsabar iskanci ne da yacika miki ciki yasa kika kasa gaida ni koh"?
Girgiza kai Haleesa ta yi
"A fusace Habeeb yace you are not dump or deaf so open your bloody mouth & talk to me"
Cikin sarkewa halshe tace dan..Allah.. Yaya Habeeb ka yi hankuri ni banaso fitina
Ya galla mata harara kina nufi ki ce ni ne fitinane lallai kuwa zan nuna miki cewa ni cikkake fitinane, ne ya mik'e tsaye saida ya yi mata kallon wulaqanci yace "Follow me
Haleesa tadafe k'irji ta zaro ido tace na'am"
Ko kallonta bai yi ba yanufi wata k'ofa ta glass cikin sassarfa ta bi bayanshi yana shiga tana shigowa batare da ya dube ta ba yanufi gym mat machine" yasoma motsa jikinshi sai uban gumi yake had'awa yayin da Haleesa tacigaba da tsayuwa jin ta yi k'afafuta sun fara d'auke wuta ta yi nufi ta zauna akan d'aya daga cikin chair's d'in wurin tun kafin d'uwawu ta su kai bisa kujerar yadaka mata tsawa ke! Wa ya baki izzini zama"?
```

A tsorace Haleesa ta mik'e chak ta yi narai-narai da ido hawaye suka tsiyayo mata wani irin dad'i ya lullu6e Habeeb Lamido sakamako hawaye da yagani sunanta fita daga idanuta, ya wani kada kai cikin d'agawa da nuna isa yace kad'an daga cikin k'anana wulaqanci da kika fara gani daga gareni kafin na fara baiyana miki manya-manya da ke jiranki amma in har kika dinga bin umurni na zan iya rankwata miki saboda ni mutum ne da bayaso shiga harka wani kamar yadda ni ma banaso a Shiga nawa yak'arasa yana Jan iska a zuciya Haleesa tace kai amma guy nan d'an air ne dube yadda yake ja iska kamar Wanda yaci yaji ta sauke numfashi muryarta na rawa tace zan kiyaye da duk wani umurni da za ka dinga ba ni.
Kamar bai ji abunda tafad'a ba ya yi switch off in machine d'in yasauko yadauki fari towel ya goge gumi fuskarshi har zuwa dokin wuyanshi yajuya yafice Daga room d'in da kyar Haleesa ta ja k'afutata kafin tak'ara sa tuni har Habeeb yarufo k'ofar ta tura k'ofa amma ta ji ta gam tacigaba da tura k'ofar iya k'arfinta har tagaji ta yi tsaye turus wani irin gumi ya tsiyayo mata me Habeeb yake nufi na rufe a cikin wad'annan k'arafe dole tanemi wurin ta zauna a hankali take rera kuka ga wani irin murd'awa da cikinta ya ke yi ta mik'e da kyar gaba d'aya jikinta ya jik'e da zufa tasoma dukan k'ofar da k'arfi had'e da kiran sunan Habeeb tsawon lokacin ta d'auka a haka daga karshe ta sulala k'asa tadafe kanta tasoma tambaya kanta, wannan wane irin aure ne rana farko na a gidan Habeeb na fara fuskantar k'alubali Habeeb yana sane yarufe Haleesa saboda yasan bara ta ta6a iya bud'e k'ofar domin k'ofar da code take using saida 6ata "long time a bathroom duk don ya wahalarda Haleesa ya shirya cikin brown Jean's da yellow t-shirt yasauko k'asa fuskarshi a murtuk'e ya bud'e ta Haleesa nagani K'ofa ta bud'e tak'ara fashewa da kuka Habeeb ya ja tsoki ya yi tafiyarshi tafito tana Jan k'afa ta hango shi a dining area peter yana saving in shi nan take yunwa da takeji tadawo sabuwa wata zuciya tace ki je Haleesa ki cika cikinki saboda bara ki iya cigaba da jure zama da yunwa "with full confidence tanufi table d'in a lokacin har Habeeb yafara cin abinci shi peter ya ja mata kujera ta zauna ya yi mata saving tsanani yunwa da takeji yasa tafara cin Chip's bata ko taunawa sosai take hadiyewa abunda ya yi mugun ba wa Habeeb haushi ya tsane ya ga ana cin abinci haka domin shi komai a yangance yake yi da k'arfi ya jefa  spoon in hannunshi cikin plate yature kujera ya yi tafiyashi Haleesa ta bi shi da kallo ta tabe baki saida ta yi narkat sannan ta tashi tanufi cikin "main parlour Habeeb na hakice akan two star fuskar nan a had'e kamar tsoho soja cikin sanyin jiki Haleesa ta zauna a k'asa "rugs carpet ta sunkuyar da kai a fakace Habeeb yake satar kallonta, Haleesa tad'ago da sunan ta sace kallonshi karaf suka had'a ido ya galla mata harara ya kuma k'ara  d'aure fuska da sauri ta d'auke idanuta phone in shi ta yi ringing ya yi picking _mtwww....ya ja tsoki look Mus'ab ni fa banaso iskanci in za ka shigo to bissmillah in kuma za ka tsaya munafuci ka ne ka kyalle khaleel ya shigo_ ya yi hanging up
A zuciya Haleesa tace kai wannan anyi masifafe, da kowa masifa ya ke"
Mus'ab da khaleel suka shigo sai fama kyalkyatar dariya suke kowanesu yanemi wurin zama Haleesa ta gaida su cikin tsokana Mus'ab yace Amarya bakya laifi ko kin kashe d'an masu gida murmushi yak'e Haleesa ta yi tak'ara sada kai k'asa Habeeb ya ja tsoki cike da takaici yace sanin kanka ne banida d'a a gidanan bansaniba sai in kai za ta kashe Mus'ab ya yi dariya yace to ae ni ba d'a ka bane a yatsine Habeeb yace wannan kuma matsalar ka ce "Haleesa ta mik'e tsam tanufi bedroom d'inta Mus'ab ya gyara zamanshi yace Habeeb yakamata ka sakawa zuciyarka salama ka, zauna lafiya da yarinya nan domin ni banga wata matsala a tare da ita, Habeeb ya yi tsoki had'e da mik'ewa khaleel tashi mu tafi banida "time in sauraro surutu

wannan duk yadda Mus'ab ya so ya lurar da Habeeb amma yak'i bashi had'in kai.
Bayan fitar Su Habeeb Haleesa tafito parlour bata jima da zama ba Hannah tashigo suka bud'e shafi na fira Hannah tarik'o Hannun Haleesa shawara zan baki Haleesa ba wai a matsayina na k'anwar mjinki ba matsayina na k'awarki kuma 'yar uwarki a musulunci Haleesa ki yi hankuri ki bi mijinki sau da k'afa domin samun aljannarki kada ki biyewa ta yaya Habeeb domin shi mutum ne mai wuyar sha'ani a wani gefe kuma yana da matuk'ar saukin kai, Haleesa ta yi murmushi na gode da wannan shawara ta ki Hannah zan yi k'okari na rinjaye zuciyata na bi yaya Habeeb insha Allah ba za'a ta6a samun matsala daga gareni zan bi shi ta yadda yakeso, sai misali k'arfe _2:30pm_ Hannah ta yi sallama da Haleesa.

_5:00Pm_
Haleesa na zaune a parlour har zuwa lokacin Habeeb bai dawo ba Maryam da zeely suka fad'o parlour ba ko sallama sai kace tumakai Haleesa tad'ago tana musu kallon mamaki daga bisani ta sauke idanuta akan wata kyakyawa yarinya da ke rik'e da hannun Maryam da shekaru ta basu haura 5-6 yrs nan take Haleesa tagano cewa ita ce imaan domin tana kama da Habeeb "sannu Ku da zuwa bissimillah ga wurin zama Haleesa tafad'a cikin 'yar gajeriya fara'a maryam ta yi mata kallon sama da k'asa ta yi tsoki tafinciko hannun zeely suka haura upstairs suka soma zagaya gidan kowane bedroom da parlour saida suka shiga part d'in Habeeb ne kadai basu samu damar shiga saboda yana rufe Haleesa ta juya wurin imaan da ke tsaye tana kallonta ta rik'e hannunta baby ya sunanki"?
Da k'arfi imaan ta fincike hannunta ta wani 6ata fuska cikin 'yar muryarta mai cike da yarinta tace "don't touch me ni bana sonki kuma aunty Maryam tace ke ba mommy na bane ke 'yar talakawa ce gidanku na jar k'asa ne irin gidansu hajjo mai aiki tak'arasa magana had'e da murguda d'an k'aramin bakinta Haleesa tasaki baki da hanci tana kallon Imaan a hankali ta dinga ja da baya tafad'a bisa kujera da6ass ta yi zaman 'yan bori cabdijam! Ana wata ga wata lallai ina da Jan aiki a gabana Maryam da zeely suka dawo cikin parlour Maryam tace, zeely yanzu kin gansu da abunda na ke Fad'a miki"?
"Kwarai kuwa k'awata ga zahiri nagani tajuya wurin Haleesa tace ke! Figa tsiyo kaza mayu wannan wane irin talauci da zallan kwad'ayi Ku ke da shi ke da iyayyenki"?
Ace ko allura ba su kawo ki da ita duk fad'in gidanan bakida tsinke naki na kanki Maryam ta kar6e zance ta hanya cewa wallahi, wallahi sai na yi nassara raba ki da yaya Habeeb domin bai dace da 'yar talakawa irinki mai k'ashin tsiya sai na sa kin yi kuka da hawayenki, masifa da bala'i da zan haddasa miki sai sun sanya ki fita gidanan da k'afarki haka su ka cigaba da yi wa Haleesa cin mutunci da yanka k'auna Haleesa na hakince tana kallonsu daga bisani ta yi murmushi tace kun gama"? Inaso ki bud'e kunnenki da kyau Maryam ki saurare ni kin riga kin tafka babban kuskure da ki ka yi sake na shigo gidan yaya Habeeb Wannan ne ya tabbata min da cewa ke d'in bakida Sa'a a rayuwa kuma da ki ke zance kayan d'aki tsabar na nunawa duniya ni nake juya yaya Habeeb yasa na zo ni kadai batare da ko tsinke, banda ke dak'ik'iya ce Maryam ae so ba ruwanshi da kyalekyale duniya ```NI DA YAYA HABEEB ``` nan gani nan bari dukiyar uban wani 'yar talakawa ta riga ta mallake zuciya abunda ki ke so.
Ran Maryam ya yi matuk'ar sosuwa da jin furuci Haleesa sai fama huci take kamar kubunbuwa motsin shigowar Habeeb ce ta janyo hankalinsu, da gudu Imaan tanufi wurinshi "Daddy oyoyo yad'aga ta chak had'e da mannata a k'irjinshi "how you my Angel"?

Am fine "Daddy
Ya yi pecking nata a cheek ya nufi kujera da Haleesa ta ke kai ya zauna daf da ita har jikinshi yana guga nata rass! Gaban Haleesa yafad'i ta wani d'id'ice Maryam ta mak'e murya tace "sannu da zuwa yaya Habeeb
Batare da ya dube ta yace sannu ya mayarda hankalinshi wurin Haleesa yarik'o hannunta "baby ba dai fushi ki ke yi da ni"?
Tsanani tsoro ya lullu6e Haleesa tad'ago had'e da tsura masa ido shin me Habeeb Lamido yake nufi da wad'annan kalamai nashi....??

Jeeddah Aliyu🌹

[04/11 7:06 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```®NWA```

°°°°```In Dedication```°°°
*To Shehu Aliyu family's*

```64```

Da sauri-sauri Haleesa ta sauke numfashi ta hadiye yawu Habeeb yak'ara dank'e yatsunta yana wani lumlumshe idanu "am sorry baby bara k'ara fita na barki ke kadai kinji"?
Kamar yadda Haleesa tasaba tashi da wuri  ta shiryawa Imaan zuwa school tana rik'e da hannunta suka nufi compound har wurin mota ta yi mata rakiya, da kanta ta bud'e k'ofa tashiga ta yi pecking  goshinta ta mik'awa sa'eed driver lunch box d'inta yayinda driver ya ja Motan zuwa gate Imaan tana d'aga mata hannun Haleesa ta mayar mata da cewa bye, babyn aunty ki yi karatu sosai Saida suka fice gate sannan Haleesa juya tana juyawa ta hango Habeeb tsaye da sauri yad'auke kai, kamar ba shi bane yake tsaye yana kallonsu, ta raba ta gefenshi dai-dai za ta shiga cikin gida tace _ina kwana yaya Habeeb"?_

"Saida zuciyarshi ta buga da k'arfi saboda baita6a tsanmani Haleesa za ta k'ara koda kallonshi ne ballanta magana ta fatar baki Tashiga tsakaninsu da kyar ya iya bud'e bakinshi ya amsa da _lafiya lau_

"Daga haka bata k'ara cewa da shi komai ba ta yi shigewarta cikin gida

"Habeeb ya yi ajiyar zuciya cike da mamakin Haleesa yafara zance zucin _ita wannan tana nufi har ta manta da abunda na yi mata jiya"?_

Wani 6angare na zuciyarshi yace da shi

In kuwa haka ne gaskiya tana da hank'uri da batada kyakyawar zuciya da 'yarka bara ta k'ara bata kulawa ba yanzu nan akan idonka ta wuce da Imaan da alama tana matuk'ar son Imaan kamar 'yarta ta cikinta, gaskiya Habeeb ka chanza tsari kadaina musgunawa yarinya nan tun kanada sauran daraja a wurinta kafin tadaina ganin darajarka ta rainaka.

Ya ja iska ya fesar a sanyaye yanufi bakin gate yana kwallawa Bala kira.

_11:00am_

Habeeb na zaune a office ga tarin aiyunka sunyi mishi yawa yarasa abunda ke masa dad'i da yarufe idanunshi Haleesa yake gani a nashi tunanin sai yadanganta hakan da abunda yafaru tsakaninsu jiya yana cikin wannan halin Mus'ab ya tura k'ofa yashigo har ya zauna Habeeb yana masa kallon k'asan idon.

"Mus'ab ya murtuk'e fuska had'e da mik'awa Habeeb hannu suyi musabaha bayan sun gama gaisawa Mus'ab ya gyara zamanshi yace ba sai gaya maka dalilin zuwa na office d'inka kwakwalwarka kadai ta isa ta zayyano maka dalilin zuwa na.

Yad'an numfasa yacigaba da cewa abunda ka aikata jiya Sam baiyi min dad'i ba jiya na kwana da takaicinka haba! Lamido da iliminka da komai za ka mayarda matarka abun
```

wulaqantawa Na fi kowa sanin yadda ka tsaneta amma bai kamata ka yi amfani da tsanar da ka ke yi mata ta zame maka hujja da za ka dinga wulaqantata ka ji tsoron "Allah ka tuna duk abunda ka ke aikatawa Allah yana ganinka in har ka 6oyewa mom irin mugun zaman da ka ke yi da Haleesa ka tuna ba ka isa ka 6oyewa ubangijinka ba.

"Har Mus'ab yadasa aya Habeeb yana kallonshi had'e da tsotsa baki wannan tsotsar bakin ya zame masa d'abi'a ya mik'e a hankali yataka zuwa wurin water disperser yadauki glass cup ya matsa ruwa mai sanyi ya kwarararawa mak'oshinsa ya lumshe idanu yana fesar da iska daga bisani ya koma mazauninshi.

"ya tabe baki ya dube Mus'ab a d'age yana wani cizo lips look Mus'ab karka shiga abunda ba ruwanka a ciki kafin kowa sanin halina, na tsani katsalanda a rayuwana bana shiga rayuwan kowa bai nima kanemi ka shiga rayuwana bansan menene b'acin rai ba sai da na had'u da yarinya nan ban ta6a d'aga hannun na  mari mace sai akanta, banta6a kwanciya na k'asa b'acin sai akanta a da ni mutum ne mai sanyi amma Shigowar yarinya nan a  rayuwata ya sauyani na dawo mutum mai tsananin zafin gaske na rok'e ka Mus'ab karka sake yi min maganarta saboda tun farko saida na gargad'enta akan ta bi dokoki na domin ta zauna lafiya da yake ita mai kunnen k'ashi ce sai ta yi fatali da doka ta ni kuwa me zai sa na d'aga mata k'afa"?

"Mus'ab ya girgiza kai yace Lamido  fahimce wani abu mana Haleesa fa k'aramar yarinya ce a hankali yakamata ka bi da ita har, ta fahimce tsarin rayuwarka ko wannan miskilancin naka kadai ya isa ya cutar da ita kuma ni ba zan fasa fad'a maka gaskiya ba saidai ka yi ta kallona a matsayin mai katsalanda a rayuwarka.

"Habeeb ya ja tsoki cike da takaicin Mus'ab ya koma jikin kujera ya lafe yayinda kujerar tadinga jujuya shi.

Mus'ab ya mik'e ranshi a b'ace yace tunda kai girman kanka bara bari ka bata hankuri ni zan je gidan naka na bata hankuri yana k'arasa magana bai jira jin ta bakin Habeeb ba ya yi ficewarsa.

"Habeeb ya bi shi da harara a baiyane yafara magana ba hankuri za ka bata ba in ka je ka goyata ka yawace garinan da ita ba abunda yadameni, ko angaya maka ni bawan mace ne irinka yak'ara Jan tsoki....

```HALEESA```

_Haleesa_ tana cikin kitchen sai ta ji ana sallama, da sauri ta fito ga mamakinta sai taci K'aro da Mus'ab zaune akan 1 sitter da murmushi tak'arasa shiga parlourn _sannu da zuwa Mus'ab_

"Yauwa Haleesa ya gida duk da naji gidan tsit yak'arasa magana yana 'yar dariya.

Haleesa ta yi murmushi ta koma kitchen tadauko masa kwalin fruitta mai sanyi had'e da glass cup ta tsiyaya ta mik'a masa tanemi kujerar da ke facing d'inshi ta zauna ta sada kai k'asa saboda tana mai jin kunyar abunda yafaru jiya.

"Mus'ab ya d'an yi slipping juice d'in ya ajiye cup bisa stool ya yi gyaran murya, yace Haleesa dama zuwa na yi na baki hankuri akan abunda yafaru shi kanshi lamid'o ya yi Nadama abunda ya yi miki kawai yana jin kunyar yadda zai yi facing d'inki yabaki hankuri amma yace nace da ke ki yi hankuri Sharrin shed'an ne.

"Haleesa ta yi murmushi domin tasan abunda Mus'ab yafad'a ba gaskiya bane  Habeeb Lamido ne zai ce a bata hankuri ae ba yau ya sa6a cin mata zarafi Wanda yafi wannan ya yi mata bai ce a bata hankuri ba sai wannan.
```

"Idanunta suka ciko da hawaye bata damu da ta goge su ba, tace ba zan 6oye maka ba Mus'ab a da ina da ra'ayi zama da yaya Habeeb koda ace zai dinga yanka naman jikina sai yagajin don kanshi ya saleme ni, amma a yanzu nayi nadamar aurenshi ba don komai sai don ya kasance mashayi ni kan bara iya rayuwa da mashayin giya tak'arasa magana cikin shasshek'a kuka.

"Mus'ab ya zaro idanu a rikice yace giya fa ki ka ce Haleesa"?

"Kwarai Mus'ab abokinka mashayi ne Sam babu tsoron Allah a tare da shi a cikin gidanan yake shan abarsa ya yi tatul.

"Da mugun mamaki Mus'ab yake kallon Haleesa daga bisani yace to ke Haleesa menene shedarki Lamido yana shan giya"?

Ni kuwa nakeda sheda mu je part d'inshi ka ganewa idanunka Haleesa tashige gaba Mus'ab yana biye da ita saboda iya zamanshi da Habeeb yasan ko cigarette ba yasha asalima ya tsanin duk wani abu da yake saka maye.

"Haleesa ta turo k'ofa suka shiga cikin parloun ta nunawa Mus'ab glassblower da ke d'auke da jerin white wine kala-kala Mus'ab ya yi ajiyar zuciya ya bud'e glassblower yaciro bottle gudu ya mik'awa Haleesa da sauri ta ja baya tana wani zare idon Mus'ab ya kyalkyale da dariya yace ki k'ar6a mana so nake ki karanta rubutu da ke jikin bottle d'in a sanyaye Haleesa ta k'ar6a ta karanta juice ne da aka sarafa da fruits sannan kuma an rubuta non alcoholic Haleesa tasauke ajiyar zuciya wani sanyi ya ziyarce zuciyata ta runtse idanu daga bisani ta ware su cikin jin kunya tace gaskiya na yarda da maganar yaya Habeeb da yake cewa ni villager ce amma kuma Mus'ab karka ga k'auyancin na saboda ban tashi a gidan da ake shan irin wad'annan abubuwan ba.

Mus'ab ya yi murmushi yace ki kyalle Lamido shima bak'auye ne sannan kuma ba ke kadai ki ke kallon wannan juice a matsayin giya mutane da dama Wanda ba su San juice bane a haka suke kallonsa.

"Haleesa ta yi dariya tajuya Mus'ab ya Mara mata baya suka koma parlournta, yacigaba da bata hank'uri saida ya tabbata da ta hank'ura sannan ya yi mata sallama.

_5:00pm_

Haleesa tana zaune a parlournta Imaan ta isheta da rigima a dole sai sunyi wasan 'yar 6oya Haleesa ta yatsine fuska ta ajiye phone d'inta bisa hannun kujera ta rik'on hannun Imaan suka nufi compound daga idan suke zuwa main gate akwai tazara sosai Haleesa taciro d'an kwalin kanta gashinta yasauka a gadon bayanta, tace da Imaan zo nan babyn aunty na daure miki idanunki

"Imaan tadaka tsalle cikin shagwa6a tace Allah aunty ke ce first ni kuma second Haleesa ta yi dariya tace kai....ka ji min yarinya da wayyo tana magana tana daure fuskarta idanunta na rufe tace 1.....2....3.... Start tasoma lallu6en Imaan tana jin dariyar Imaan amma takasa kamata, haka tacigaba da lullube.

"Bala yaddano hancin mota cikin compound Habeeb na owners corner a zaune tun kafin su k'arasa parkingc space ya hango Haleesa da Imaan suna wasa yaja tsoki a zuciyarshi yace k'aramar kawai Bala yana dariya ya bud'ewa Habeeb k'ofa yafito

"Boss yau amarya ta tuna da k'urciya wasan 'yar 6oya sukeyi yak'ara sa magana yana wani Sosa kai.

Harara Habeeb ya watsa masa yace kadauko briefcase ka shigar min da shi ciki Yajuya yanufi

cikin gida.
"Babyn aunty where are you I'm tight zan bud'e idanuna in bara ki bari na kama ki ba Imaan ta kyalkyale da dariya tace _yeee.... Aunty if you're can catch me_
Da sauri Haleesa tanufi idan takejin sautin muryarta dai-dai Habeeb yakawo da sauri Imaan ta boye bayanshi garin lallube Haleesa ta yi tuntube za ta fad'i da sauri Habeeb yatare ta tafad'o kan k'irjinshi..........

Jeeddah Aliyu🌹

[24/11 7:33 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```®NWA```

°°°°```In Dedication```°°°
*To Shehu Aliyu family's*

```77```

_this page dedicated to you *Ayshat D'ansabo lemu* thanks for the love & support it's means a lot_

~~k'amshin perfume da ta yi amfani da shi ya ratsa k'ofufi hancin Habeeb baisan lokacin da ya lumshe idanunshi yak'ara matso da ita zuwa k'irjinshi ya matse ta gam Tsigar jikinta ta tashi Yarr! Hancinshi yadaura a gefen wuyanta yana shak'ar k'amshinta tuni Habeeb ya manta suna tsaye ne a compound yafita haiyacinsa, numfashinsa yana fita da sauri-sauri ya kasa daurewa ya ziro hannunshi cikin rigarta da sauri Haleesa ta taka masa birki ta hanyar furta _please yaya Habeeb stopped Imaan is looking at us_
A rikice yadawo hayyacinsa ya tureta daga jikinsa dama hausawa sunce tabarma kunya da hauka ake nad'eta sai kawai ya gallawa Haleesa harara _wannan wane irin sakarcin ne huh"?_
_shine illah auren k'anana yara dube ki wai wasa 'yar 6oya ki ke yi danasani na barki ki fad'i ki karya k'afa ko hannunki naga d'an iska da zai yi jinyarki dallah! Bani wurin in wuce kin yi wani tsare ni da idanu_
A zafafe yak'arasa shiga gida Haleesa ta bi shi da kallon tasauke ajiyar zuciya, tajuya ta hango Imaan zaune cikin flowers tana wasa sai faman tsinko Flowers take tana tarawa a gefenta,

Haleesa tak'ara sauke ajiyar zuciya a cikin zuciyarta tace, _thank God_ ashe ba Wanda ya ganmu tanufi wurin Imaan tarik'on hannunta suka shiga cikin gida.
_9:00pm_
Haleesa na kwance a bedroom d'inta ta yi rub da ciki ta d'aga k'afafunta sama ta yi zurfi a tunanin rungumar da Habeeb Lamido ya yi mata d'azu da yamma abun yakasa fita daga zuciyarta duk lokacin da ta tuna da kyakyawar rungumar da tasamu a wurinshi sai ta yi murmushi ta kasa tantance wannan murmushin da take yi na menene ta yi wani juyi tadawo rigingine idanunta a lumshe tasoma fasalta kyakyawar Surar jikinsa ba abunda yafi burgeta a jikin Habeeb Lamido irin lallausar sumar kanshi koda yaushe idaunshi a lumshe suke kamar mai jin bacci da kyar Habeeb ya yi magana batare da ya ja iska ba kamar Wanda yacin yaji, yana yawan tsotsan bakinshi za ka yi tsanmani sweet yake sha in kuma yana magana d'aya-d'aya yake furta harafi sai kace mai bita, Haleesa ta yi murmushi  a zuciyata tace _Handsome_ kenan ga kyau saidai mugun hali da miskilancin tsiya, ta mik'e zaune ta k'urawa wall clock idanu _10:09pm_ ta d'an ja tsaki ko kad'an batajin bacci dama Imaan ce abokiyar firarta tun 8:00 o'clock ta yi bacci.

```HABEEB LAMID'O```

Habeeb na zaune a parlournshi yana tura bayanai a system yunwa yakeji kamar 'yan hanjinshi za su tsinke ya rasa dalilin da yasa tun jiya da yacin abincin Haleesa d'andanon abincin yakasa fita daga bakinshi duk abunda yacin sai yaji ba tested yature laptop a gefe yanufi part d'in Haleesa cikin sand'a kamar barawo yak'arasa wurin dining table ya bud'e warmers k'amshin Egusi soup ya buge hancinshi ya cigaba da bud'e warmers yana ganin abunda ke ciki a zuciyarshi yace ba shakka wannan abincin yarinya nan ce ta girka shi yadauki Ledar tuwo semo guda d'aya yasaka cikin plate ya zuba soup a d'an k'aramin plate d'ayan plate kuma zuba farfesun kifi da sauri yakoma parlournshi yana ci yana wani kad'a kai _ashe haka yarinya nan ta kware da girki"?_
_Gaskiya tafi Peter iya sarafa abincin nayi kuskure wulaqanta ta saboda banta6a cin abinci da ya yi min dad'i irin nata ba kuma har abada bara ta6a nuna mata ina jin dad'in girkinta duk ranar da tagano ina cin abincinta ajina da girmana za su zube a idonta ni kuma bara sake da abunda zai rage mini class_
Ya cinye tuwon tass! Har da su sud'e plate daga bisani yanufi bedroom ya zarce bathroom ya yi brush agajiye yafad'a kan bed cikin d'an k'ank'anin lokacin bacci yadauke shi a cikin baccin nashi yafara mafalkin leesa Zaune take a garden tana wasa da ja da farin fure tashagala da abunda take yi a hankali yake sand'a har yak'araso daf da ita ya zauna tana juyowa suka had'a ido tasake masa k'ayatace murmushi shima ya mayar mata da martanin murmushin nata kasa d'auke idanunshi ya yi akanta cikin sigar shagwa6a ta turo d'an k'aramin bakinta mai jefa Habeeb cikin tsantsar sha'awarta _yaya Habeeb wannan kallon fa"?_
  Cikin shauk'in so yarik'o hannunta ya jefa yatsanta a bakinshi yana tsotsa kamar yasami lollipop, da sauri leesa ta fisge hannunta ta wani yatsine fuska, Habeeb yadawo kalar tausayi chan k'asan mak'oshi ya furta _please leesa ki barni mana_
Shiru ta yi tana kallonshi da k'arfi yafisgota tafad'o kan k'irjinshi  ya matse ta gam ya lalla6o bakinta tsawon lokacin suka dauka a haka daga bisani ta ture shi ta mik'e da gudu tanufi cikin
```

yayinda shima ya mik'e ya Mara mata baya a parlour ya yi nasara kama ta ya d'auke ta chak! Yanufi bedroom da ita yadireta akan bed Daga nan komai yacigaba da wakana.
A firgici Habeeb ya falka daga mafalkin da ya zame masa, jiki gumi ya tsatsafo masa yadafe kanshi da hannayen, ya runtse idanunshi gam! Photon abunda yafaru tsakaninsa da Haleesa yadawo masa da sauri ya ware idanunshi ya ja tsaki cike da jin haushin kanshi ya mik'e yanufi bathroom.
Habeeb wanka ya ke yi yana zance zuci _me yasa duk lokacin da na kwanta bacci sai na yi mafalkin ina saduwa da yarinya nan"?_
_ina da wannan mafalkin nawa zai kasance gaskiya tabbas da ba k'aramin tafiyar da ruhina za ta yi ba_
Jiki ba lakka ya gama wanka yafito har aka yi kiran asuba yana fama da tunanin leesa da yarufe idanu kyakyawar fuskarta yake gani.
********************
_7:00am_
Haleesa na tsaye cikin kitchen tana had'awa Imaan abincin da za ta tafi da shi school tuni ta takatar da peter da Girka abinci da ita da kanta take shiga kitchen ta girka duk abunda ranta yakeso agurguje ta kamalla had'awa Imaan lunch box d'inta tanufi d'akin Imaan tayi mata wanka had'e da shirya ta cikin uniform ta zarce da ita dining area ta ja kujera ta zaunar da ita ta had'a mata tea had'e da chip's Imaan tana gama breakfast Haleesa tarik'on hannunta suka nufi compound suna, fita ta hango Habeeb da Bala a tsaye Habeeb na jefawa karnuka{ police dog's} nama suna Cin kasa k'arasawa parking space ta yi saboda tana jin kunyar had'a ido da Habeeb.
Imaan tadaka tsalle _yeee yau Daddy ya fiddo da Rahul da Rita bara naje mu yi wasa_
Da sauri Haleesa ta taka mata birki ta hanyar furta ke Imaan banaso shirme ke da za ki tafi school me ye gaminki da karnunka karki sake naga kin tsaya a wurinsu ko kinmanta yau za Ku fara test ne"?
Imaan ta girgiza kai Haleesa tace to kama hanya kitafi ga sa'eed driver yana jiranki ta mik'a mata lunch box d'inta Imaan tajuya tanufi wurin Daddynta _Good morning Daddy_
Morning my angel
Cikin shagwa6a Imaan tace Daddy shine saida kaga zan tafi school ka fiddo Rahul da Rita koh"?
Habeeb ya yi murmushi ya shafi kumatunta kin ga my angel banaso rigima kitafi school in kindawo auntynki ta fiddo miki su ku yi wasa.
"Imaan ta zaro ido kamar taga abun tsoro _Daddy aunty Haleesa tsoronsu fa take yi ranar ma mu je garden da ta gansu da gudu takoma cikin gida tadinga fad'a tana cewa shi wannan yaya Habeeb komai so yake yi yanzu yarasa abunda zai yi kiwo sai bak'ak'en karnunka sai nace da ita aunty ba fa sunansu karnunka ba sunansu R........_Imaan ta hadiye raguwar kalamanta sakamako katsinta da Habeeb ya yi my angel wannan labarin naki basan tsawon lokacin da zai d'auka kafin naji karshensa ki bari sai kindawo daga school ki k'arasa mun kinji"?
Imaan tad'aga kai sa'eed driver yarik'o hannunta suka nufi parking space
"Bala ya kyalkyale da dariya Habeeb ya galla masa harara Bala ya hadiye dariyarshi yace "Boss Imaan tana mugun burgeni saboda surutun nan nata.
Habeeb ya tabe baki yace ae dole ta burge ka saboda halinku d'aya

Bala washe hak'ora yace ni fa boss mamaki nake yi kai ga  magana wuya take maka kuma ka tsanin yawan surutu sai gashi Allah yabaka 'ya mai bala'e surutu kamar Aku{parrot}
Habeeb ya ja tsaki yace _"Allah ya shiryeka Bala_
Bala yace ameen boss yau za'ayi ruwan sama har da k'ank'ara saboda ka yi min fata nagari da alama amarya tafara canza ka yak'arasa magana yana dariya
"Tsawon lokacin Habeeb yad'auka yana kallon Bala daga bisani ya girgiza kai, yace tun da kagama surutun naka daga ciki har da yi mun sharri sai ka tattara rahul da Rita ka mayarda su d'akinsu karka d'aure su kabarsu a sake kuma ka tabbata ka rufe musu k'ofa.
"Bala yace angama boss ae tun da na fahimcin amarya tana tsoronsu bara yi sake da za su fito su tsorata maka ita.
Habeeb ya yi murmushin takaicin  yajuya yasan muddin yacigaba da tsayuwa Bala zai iya haddasa masa bugawar zuciya direct parlourn Haleesa yadosa bata ciki tana bedroom ya yi tsaye a tsakiyar falon yana k'are masa kallo _very neat_ sai k'amashin turaren wuta ke tashi karaf idanunshi suka hasko masa dining table da sauri yanufi wurin ya yi serving d'in chip's had'e da sauce na cabbage da carrot ya ji anta da k'oda dai-dai lokacin da Haleesa taddano kai parlourn ta hango abunda Habeeb
Yake yi da sauri ta la6e tana lek'onshi tana kallonshi har yashige part d'inshi Haleesa ta yi murmushi ta kad'a eye's ball d'inta lallai Habeeb lamid'o d'an rainin hankali ne ko ya manta da kirarin da ya yi kada na kuskure na dafa ko da noodles da sunanshi sai gashi na kama shi yana satar mun abinci daga yau bara ka k'ara ganin abincin ballantana har ka sata
"ta yi murmushin mugunta tun daga ranar Haleesa da tayi girki take zube abinta cikin warmers takai bedroom da, Habeeb yasud'ad'o yacin mai dad'i yatarar da dining table wayam!
Duk lokacin da Habeeb Lamido ya zauna bashida aiki sai tunanin Haleesa kuma baya iya cin abincin kowa sai nata yadda peter ya jera masa abincin haka zai dawo yadauke saboda ko kallon bai ishe ba cikin d'an k'ank'ani lokacin Habeeb yafara fita hayyacinsa, ganin yadda sha'awar Haleesa na neman kassara shi ya tattara kayansa ya haura Germany a tunaninshi in ya nisanta da ita zai manta da duk wani abu da yashafe ta baisan cewa hakan ba abunda zai k'ara masa sai  d'inbin damuwa, da tunani kuma yak'i ya amince da soyayya Haleesa ce ta kama shi ba sha'awa ba.
*****************
```GERMANY```
Habeeb yana zaune a wani had'ad'en wurin  hutawa kallon d'aya za ka yi masa kagano yana cikin damuwa yadda zuciyarsa ke azalzalarsa akan ya kira Haleesa ko muryarta za ta rage masa damuwar da yake ciki zuciyarsa na bugawa Ya yi dialling number ta.
Haleesa na zaune Imaan tayi pillow da cinyoyinta kiran Habeeb yashigo wayarta ta zaro idanu gabanta na fad'uwa ta yi picking................

Jeeddah Aliyu🌹

[25/11 4:57 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```
```

_❣ the sweetest love_❣

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```®NWA```

°°°°```In Dedication```°°°
*To Shehu Aliyu family's*

```78```

~~cikin muryarta mai sanyi da zak'i ta furta _hello_ Wani irin sanyi ya ziyarce zuciyar Habeeb har ya yi nasara saukar masa da natsuwa, ya sauke ajiyar had'e da lumsashe idanu tsabar miskilancin irin na Habeeb Lamido a maimakon ya furta abunda ke neman raba shi da jin dad'insa sai kawai ya yi shiru yayinda katin wayarshi{recharge card} ke tafiya a banza jin shiru nashi ya yi yawa yasa Haleesa tak'ara cewa _hello_ ya ja iska ya fesar adak'ile yace ki ba wa Imaan waya zan yi magana da ita, jiki a sa6ule Haleesa taciro wayar daga kunnenta ta d'anko hannun Imaan ta daurawa mata ranta a b'ace tace ki yi magana da Daddynki, ta rafka tagumi tunanin hali irin na Habeeb shin ko ya manta da matsayinta na matarshi da bara iya tambaya ko da lafiyar jikinta ne ta ja d'an siririn tsaki ta mayarda hankalinta wurin Imaan tana sauraro yadda ta ke zuba masa surutu, mai d'auke da tambayoyin _Daddy ina ka tafi ne na daina ganinka in na tambayin aunty Haleesa ina ka ke sai tace batasaniba"?_

"A hankali Habeeb ya bud'e idanunshi ya cize lips d'inshi na k'asa kenan yarinya nan bata ma damu da ni ba ni kadai nake fama da sha'awa da tunaninta.....cike da jin haushin Haleesa yaja tsaki yace my angel na yi tafiya shiyasa ki ka daina ganina.

" Daddy Ya sunan garin da ka je"?
Ya yi murmushi a kasalance ya furta Germany
"Daddy yaushe za ka dawo"?
Dafe goshi ya yi saboda yafara gajiya da tambayoyin Imaan da kyar ya furta very soon my angel
Daddy me za ka siyo mun"?
_Anything you wants my Angel_
Imaan ta yi shiru tana tunanin abunda za ta fad'a kamar daga sama tace Daddy ka siyo min monkey da snake da lizard da......cikin zafin rai Haleesa ta kwace wayarta ta yi hanging up ta gallawa Imaan harara ke wace irin yarinya ce Imaan"?
Duk lokacin da Daddynki ya yi tafiya bara ki lissafa masa abun Kirki da zai siyo miki sai na banza da wofi ko angaya miki nan gidan zoo ne da zai kwaso wad'anan tarkace ya kawo miki. Imaan ta kwa6e fuska kamar zai ta yi kuka cikin shagwa6a tace aunty ban gama magana da Daddyna ba kin kar6e waya

"Haleesa ta tabe baki ta shafi sumar kan Imaan tace ae kin gama magana Imaan fatana d'aya kada Allah yasa wannan Daddy naki 0ne & d half ya biye wa shirmenki ya kwaso miki wad'annan masifun da ki ka lissafa saboda, shima irinki ne bai ji sauki ba ta k'arasa magana

had'e da kya6e baki.
"Imaan ta zaro idanu tace aunty dama Daddy bashida lafiya"?
Haleesa ta yi murmushi a zuciya ta tace kai wannan yarinya akwai 'yar jarida da alama uwarta ta biyo da wannan d'an banzan surutu saboda ubanta kurma ne a baiyane kuma sai tace _Eh bashida lafiya amma ya ji sauki_
Aunty me ke damunshi"?
Haleesa ta girgiza kai tace Imaan tashi ki je kitchen akwai ice cream a fridge ki dauko ki sha kinji"?
Da sauri Imaan ta tashi cikin zumud'i tanufi kitchen Haleesa tana murmushi ta bi ta da kallo.
Ta 6angare Habeeb kuma yana jin kiran ya yanke sai kawai ya tabe baki yadanganta, hakan da matsalar network d'in Nigeria ya dukufa tunanin Haleesa iya saninshi ba son yarinyar yake yi ba matsananciyar sha'awarce take wahalarda shi, duk ranar da ya kusance ta zai manta da ita ya ja tsaki had'e da shafi sumar kanshi yana mamakin yadda yake ware lokacin mai matuk'ar mahimanci agareshi ya zauna yana tunaninta a da shi mutum ne Wanda bai San tunani ba sai akan Haleesa tun farkon had'uwarshi da ita har yau ita kadai ce take haddasa masa shiga yanayin na tunani.
***********************
```2 DAY'S LATER```
Habeeb na kwance a room d'in da ya yi booking a Alexander Hotel da ke Germany ya yi pillow da hannayenshi ya zurfafa a tunanin, Haleesa duk yarame sai wani farin da ya yi ga wata 'yar uban k'asumba da yatara akan fuskarshi kamar Wanda aka mintsina ya mik'e zaune yadauki phone d'inshi da ke ajiye akan bedside ya yi dialling number Haleesa a maimakon ya jin 'yar muryarta mai sanyaya masa zuciya sai kawai ya tsince muryar Imaan tana zuba masa surutu, ba d'ad'aukawa bai San lokacin da ya katsin kirar{hanging up} ya jefar da wayar bisa bed yarik'en kanshi da ke barazanar fita daga gangar jikinsa, ga matsananciyar yunwa yana ji tun zuwanshi Germany daga coffee sai soft drink su kadai yake daurawa cikinsa cikin d'an k'ank'ani lokacin zazza6i mai zafin gaske ya lullu6e shi.

```HALEESA```
Haleesa na zaune bisa farar kujera roba a compound Imaan na wasa akan 'yar motarta ta wasan yara wance ake sakawa a charging sai kai da kawo take yi Haleesa kuma ta duk'ufa tunanin rayuwarta Ita kanta in aka tambayeta bara ta iya cewa ga asalin abunda ke damunta lokacin sallah magarib yak'arato ta tattara Imaan da motarta suka shiga gida.
A daddafe Habeeb Lamido ya yi 2 weeks a Germany yajuyo gida Nigeria around _10:30pm_ flight d'in da yad'auko su ya yi landing a hankali yake taka stairs d'in jirgi yana saukowa ya hango Bala.
"Tun akan hanya Bala yafara aika masa tambayoyi "Boss ka yi rashin lafiya ne"?
Habeeb ya yi ignoring nashi, da sauri yadafe kanshi tun a flight yake jin ciwon kai had'e da sanyi duk surutun da Bala yake zuba masa ya yi shiru bai tanka masa ba suna isa gida tun kafin Bala ya bud'e masa k'ofa ya bud'ewa kansa yana gaba Bala na biye da shi janye da luggage d'inshi direct yawuce bedroom yafad'a bisa bed ko takalmin k'afarsa bai cire ba ya lullu6e cikin blanket a rikice ya yaye blanket yashiga bathroom yadinga kwara amai Kore shar abun gwanin ban tausayi, jiri na d'ibarsa yafito daga bathroom yak'ara kwanciya, sai faman rawar sanyi yake yi

hak'ora shi na had'ewa ya k'undundune cikin blanket gaba d'aya Daren rana Habeeb bai runtsa ba kwana ya yi yana kwara amai a zaune ya yi sallah asuba har 10:00am ya yi yana kwance bai San idan kanshi yake ba
"Da kyar ya lalla6o phone d'inshi ya yi dialling number Bala cikin sark'ewar halshe yace _Bala ka zo banida lafiya_ yana k'arasa magana ya jefar da waya a rud'e Bala yashigo bedroom d'in
"Sannu Boss
Muryarshi a dusashe yace please Bala kira Dr saleem.
Bayan kamar _10 minutes_ sai ga Dr saleem ya zo bayan yagama duba shi ya debi jininsa zai yi masa blood test domin ya tantance musanbabin ciwonsa, yadaura masa drip had'e da allurai bacci ya yi awon gaba da Habeeb Dr saleem kuma Yakama gabansa, Bala ya na tare da Habeeb drip yak'are ya zare masa, sai misalin k'arfe _2:00pm_ Habeeb yafalka ya yi wanka had'e da sallah duk wannan budirin da ake yi Haleesa batasaniba, Bala kuma yana mamakin ina tashiga saboda sau biyu yana shiga part d'inta bai ganta ba, Habeeb ya ji sauki sosai yau kwanansa biyu dawowa ko compound bai lek'a ba yana kwance a d'akin Bala ke kula da shi matsalar Habeeb bayason magani ga kuma rashin cin abincin tsakiyar dare ciwonsa yadawo sabo dal, a wannan karon har da stomachache sai amai yake kwarawa kamar zai amayar da 'yan hanjinshi, a wahalce ya kira phone d'in Bala koda Bala ya zo yatarar da shi duk yajigata, yafita a hayyacinshi a tsorace Bala ya yi kanshi, yad'ago shi sai kawai Habeeb yafara wani irin nishi yana rik'en cikinshi haka bacci yadauke shi, Bala ya rafka tagumi yana kallonshi kamar daga sama Habeeb ya zabura ya mik'e yanufi bathroom, ya yi amai yana fitowa ya yanke jiki yafad'i k'asa, da gudu Bala ya yi kanshi yana girgiza shi had'e da kiran sunanshi duk girgizar da yake masa ko d'an yatsanshi bai motsa ba, Bala yarud'e iya rud'ewa babu shiri ya yi dialling number madam Hindu.
"Madam na kwance akan katafaren bed d'inta kirar Royal bed tana sharar bacci ta ji ringing d'in wayarta, a tsorace ta falka saida ta yadda ganinta akan wall clock ta ga time _3:45am_ ta zaro ido gabanta ya yi mummuna fad'uwa hannunta na rawa ta d'auki wayar tun kafin ta yi picking, zuciyarta ta ba ta cewa wannan kiran ba na lafiya bane sakamako ganin kiran daga Bala ne.
"Muryarta na rawa ta furta _hello Bala lafiya kuwa ka kira ni a wannan lokacin"?_
_madam ki taimake ni ki zo wallahi boss yana cikin matsanancin hali gashinan kwance ko numfashi ba ya yi_
Bala yak'arasa magana kamar zai rushe da kuka
"Numfashin madam yadinga fita da sauri gaba d'aya ta rud'e kanta ya kwance jikinta yad'auki rawa takasa furta uffan, jin shiru nata ya yi yawa yasa Bala ya katsi kiran da kyar madam Hindu tasauko bisa bed ta bud'e wardrobe taciro wrapper{zani} ta daura bisa night gown d'in jikinta, ta zira hijabinta na sallah tun kafin tak'arasa compound ta dannawa drivernta kira da sauri driven yafito da mota a rud'e madam tashiga motar suka d'auki hanyar gidan Habeeb suna isa direban yadanna horn security's d'in gidan suka fito ta k'aramar k'ofa suna ganin motar madam Hindu da gudu d'aya daga cikinsu yajuya domin ya bud'e mata gate tun kafin ya bud'e gate madam ta balle k'ofa tafito, tafiya take yi batare da tasan inda take jefa k'afarta ba part d'in Haleesa tafara dosa taji k'ofa a rufe dole tajuya tanufi part d'in Habeeb direct ta wuce bedroom d'inshi a rikice ta yi kanshi tana kiran sunanshi...........

Jeeddah Aliyu🌹

[27/11 4:59 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```®NWA```

°°°°```In Dedication```°°°
*To Shehu Aliyu family's*

```79```

~~Son, son please wake up don't leave your mother I really need you, please Habeeb wake up, gaba d'aya lissafin brain d'in madam Hindu ya kwance tarasa inda za ta jefa kanta batasan lokacin da tafashe da matsanancin kuka tana girgiza Habeeb da k'arfi ganin take yi kamar Habeeb ya mutu ita kuka Bala kuka ba mai rarrashin wani sai lokacin tunani ya zo wa Bala da hamzari yanufi d'an k'aramin fridge da ke ajiye a d'akin ya bud'e yadauko robar ruwa mai sanyi, ya shafawa Habeeb kamar _5 second's_ da Shafa mishi ruwan yasaki ajiyar zuciya mai k'arfi a hankali ya ke bud'ewa idanu har ya ware su gaba d'aya akan fuskar madam Hindu ya k'ank'ame ta cikin dashashshiyar murya, yace _sweetheart cikina kaina, ki rik'e min kaina zai cire_ Madam Hindu tak'ara rud'ewa ta juya wurin Bala cikin shouting tace _please Bala call doctor saleem immediately_

Jikin Bala na rawa ya yi dialling number Dr saleem daf da asuba Dr saleem ya iso cikin muryar kuka madam Hindu tafara rok'onshi _please Doctor do something to save my son life I don't wants to loose him'!_

"Dr saleem yace calm down madam insha Allah ba abunda zai faru da d'anki batare da 6ata lokacin ba Dr saleem yafara treatment d'inshi ta hanyar daura mishi drip da injections cikin d'an k'ank'ani lokacin bacci ya yi awon gaba da shi madam na zaune a gefenshi tana Shafa sumar kanshi ta mayarda ganinta wurin Dr saleem tace _what's wrong with my son Doctor"?_

Dr saleem ya share zufa da handkerchief ya d'an numfasa daga bisani yace na yi matuk'ar mamaki lokacin da nagano ainihin abunda yake damunshi da farko akwai tsananin tunanin da yake yi Wanda yana daf da jininsa ya hau sai kuma rashin cin abincin Wanda ya janyo masa kamuwa da cutar ulcer.

"Madam Hindu ta zaro ido da alama firgicin a tare da ita ga kuma d'inbin mamakin furucin Dr saleem muryarta na rawa ta maimaita abunda Dr saleem yafad'a _tunani da ulcer_

"With full confidence Dr saleem ya gyad'a kai yacigaba da cewa dole sai ana bashi,

kyakyawar kulawa musanman cin abincinsa idan ya falka ki yi k'ok'ari a matsayinki na mahaifiyasa ki titsi shi domin ya sanar da ke abunda yake damu shi a matsayinki na uwa bara ki rasa taimakon da za ki ba shi, ba kuma ki tabbata yana taking medicine d'inshi in time domin na fahimce duka magunguna da na kawo mishi ba Wanda ya yi amfani da shi.

"Madam ta goge hawayen fuskarta, tace na gode Dr saleem.

"You're welcome madam Dr saleem yafad'a yatattara tarkace shi, ya kama gabansa yabar madam Hindu cikin jimami da fargaba.

"Madam tasauke ajiyar zuciya ta juya wurin Bala cike da son jin k'arin haske dangane da ciwon d'anta Bala har tsawon wane lokacin Habeeb yadauka bashida lafiya sannan kuma ina matarshi da ta barka kana jinyarsa"?

"Domin ita ce ta dace ta kula da shi ba kai ba tun zuwa na gidanan duk, da bana cikin natsuwa ta zuciya ta take bani akwai abunda ke faruwa a tsakaninsu.

"Bala ya numfasa ya karkace baki yasoma kwararo wa madam Hindu zance tun kafin boss ya yi tafiya na fahimce akwai abunda ke damunshi, kwata-kwata yadaina cin abincin ranar da yadawo yafad'i cikin yanayi na rashin lafiya sau biyu ina zuwa part d'in Haleesa bana tararda ita rabona da in sakata a idanunna tun washe garin ranar da Imaan tasami hutun makaranta, lokacin da Hannah ta zo za ta tafi da ita na had'u da su a parking space Haleesa ta yi musu rakiya mu ka gaisa to fa tun daga ranar ban k'ara ganinta ba abun ya yi matuk'ar d'aure mini kai ina tashiga ne tsawon wannan lokacin da Boss yake fama da rashin lafiya yak'arasa magana cikin yanayi da ke nuna alhininsa.

"Madam ta mik'e tsanm..... Batare da tace da Bala komai ba tanufi part d'in Haleesa cikin Sa'a tana murd'a handle k'ofar ta bud'e ta kutsa kai tun kafin tak'arasa shiga parlourn, ta hango Haleesa zaune akan _2 seater_ k'afutata na zube akan kujerar tana yanke farce jin k'arar bud'e k'ofa yasa Haleesa ta d'ago _4 eye's_ tayi da madam Hindu rass!....gabanta yafad'i da sauri ta mik'e tsaye ta d'an sace kallon wall clock da ke manne a falon _9:07am_ jikinta yafara rawa tsoro ya baiyana k'arara akan fuskarta da kyar ta furta _sannu da zuwa mom_
Saida madam Hindu takai zaune sannan ta amsa mata ba yabo ba fallasa.

"Tun daga nan Jikin Haleesa ya yi sanyi nan take zuciyarta yaba ta cewa akwai abunda yake faruwa a sanyaye ta duk'a cikin girmamawa tace _ina kwana mom"?_

_lafiya amma ba qalau ba_
furucin madam Hindu yak'ara tsorata Haleesa cikin sark'ewar halshe tace me ke faruwa mom"?

"Wannan tambaya ta Haleesa tak'ara harzuk'a madam Hindu har takasa controlling temper ta cikin zafin rai ta rufe Haleesa da fad'a _ke wance irin mutum ce Haleesa mijinki bashida lafiya tsawon kwanaki uku kuna gida d'aya ace baki saniba wannan wane irin sakarcin ne"?_

"Wannan ya tabbata mun da cewa baki Masan menene Kalmar miji take nufi ba, ballatana ki San yadda ake kula da shi, dalilin wannan sakacin naki gashinan d'ana ya kamu da cutar yunwa, wallahi idan wani abu yasame d'ana Haleesa har abada bara taba daina ganin sakaci da laifinki ba koda ace Habeeb ya yi miki wani laifi bai kamata ki yi masa horo da yunwa ba tak'arasa magana tana huci.

"Tun lokacin da madam Hindu tafara wankewa Haleesa allonta Haleesa take wuk'i-wuk'i da idanu tsananin mamakin zafafa kalaman madam Hindu suka hanata tabuk'a komai.

Shiru Haleesa ta yi tarasa abun fad'a sai kawai tafashe da kuka madam Hindu ta girgiza kai ta mik'e a zafafe tace wannan kukan da ki ke yi bashida amfani zan iya danganta shi da kukan

dad'i domin in Habeeb ya mutu bakida asara nice da asara domin ni ce narasa d'a madam Hindu na k'arasa magana tafice daga falon tabar Haleesa na kuka kamar ranta zai fita, haushi da tsanar Habeeb Lamido suka cukuikuye mata zuciya a yadda takejin zafi na kwarara a zuciyata Kamar ta had'a kayanta tabar mishi gida dama yasha fad'a mata saboda mom ya aureta a halin yanzu mom ta tsaneta, har tana danganta da laifin da batada masaniya akai tana cikin wannan halin Hannah tashigo
ta zauna a gefenta cikin sanyin murya tafara magana, Haleesa yanzu nan mom ta kira ni a waya ta zayyane mun abunda yafaru nayi matuk'ar mamaki yadda mom takasa gano laifin yaya Habeeb, jira nake yaya Habeeb yafarfad'o na fallasa shi a gabanta in yaso ta tantance tsakani ke da shi waye mai laifi.

"Haleesa ta share hawaye fuskarta tace Hannah banaso, ki sanarda mom komai dangane da zaman mu da yaya Habeeb, a hali yanzu zuciyata tariga ta bushe na dau alwashi sai na azantarda ruhin d'an uwanki da soyayya ta mai tsananin zafin gaske na yi amfani da ita na rama duk wani cin kashi da ya yi min sai na nunasa masa cewa ba kowace Mace ake wulaqantawa ba sai gwanmace kid'a da karatu.

Cikin tsananin farin ciki Hannah tarik'o hannun Haleesa tace tun farko abunda nake nuna miki kenan Haleesa ki ka k'i bani had'in kai da yanzu zance yasha banban, yanzu tashi mu tafi ki ba wa mom hak'uri nasan yadda mom takesonki bara ta iya cigaba da fushi da ke kuma duk bak'ak'en maganganu da mom ta zuba miki ki rubuta su tass....ki yi wa d'anta tanadin su Haleesa ta zaro ido tace Hannah bakida kirki yayanki ne fa

"So what's Hannah tafad'a had'e da kad'a eye's ball d'inta karki manta Haleesa ciwon 'ya mace na 'ya mace ne don haka duk lokacin da yaya Habeeb yashiga hannunki karki raga masa ki tabbata kin sauke masa wannan miskilancin da yake tak'ama da shi.

Haleesa ta cize lips d'inta na k'asa ta kad'a kai tace bari kawai Hannah Allah yakai damo ga harawa.

Ameen 'yar uwa zo mu tafi kada mom tak'ara hayewa.

"Direct bedroom d'in Habeeb suka wuce mom na zaune kusa da shi ta rafka tagumi yayinda Habeeb ke ta sharar bacci, Hannah ta zunguri kafad'ar Haleesa nan take Haleesa ta yi pity face ta zube gaban mom tarik'e hannun mom ta marairace murya _Dan Allah mom ki yi hak'uri nasan na yi kuskure amma insha Allah bara ki sake kamani da koda kwatankwacin irin wannan laifi_

tak'arasa magana cikin muryar kuka madam Hindu tasauke ajiyar zuciya tad'ago Haleesa suka nufi parlour tasoma yi mata nasiha daga yau Haleesa karki sake sakacin sake ragama abincin mijinki a wurin ku-ku lokacin da peter yake yi min bayani tun zuwanki gidanan shi yake yi wa Habeeb girki ba ki ji yadda raina ya6acin ba amma yanzu komai yawuce ki tashi ki Shiga kitchen ki Samar mishi abunda zai cin domin Dr saleem yace da ya falka abashi abinci

"Da hamzari Haleesa ta mik'e tanufi part d'inta Hannah ta Mara mata baya.

_15 minutes later_

A hankali Habeeb yake bud'e idanunshi har ya ware su gaba d'aya, k'ok'ari yake ya mik'e zauna da sauri mom ta taimaka masa, ya zauna tasaka masa pillow a baya ya jingina jikinsa, duk ya rame ya yi k'ashin wuya.

"Sannu son ya ka ke jin jikin naka"?

Da sauki mom yanzu dai ina son na yi wanka na rama sallah da ke kaina.

Da sauri mom ta mik'e bara na kira Haleesa ta taimaka ma, batare da ta jira jin ta bakinshi ba tafice, Wani irin dad'i ya ratsa sassan jikin Habeeb ya kwarara a zuciyarsa, ya lumshe idanu, jin karar bud'e k'ofa yasa da sauri ya bud'e idanunshi yasauke su akan fuskar Haleesa, tasake masa k'ayatace murmushi, sannu yaya Habeeb ya jikin naka"?
"Saida ya ja iska yafesar sannan yace da sauki ki taimaka ki had'a min ruwa zan yi wanka
Batare da tace komai ba tashiga bathroom ta cika masa bathtub da ruwa masu d'an d'umi-d'umi har tafito yana nan yadda ta barshi muryarta tace tadawo da shi daga tunanin da ya afka _yaya Habeeb na had'a ruwan_
"Chan k'asan mak'oshi ya furta na gode yana bin bango yashiga bathroom Haleesa ta bi shi da kallo ya yi matuk'ar bata tausayi ashe akwai abunda zai sa yaya Habeeb ya yi laushi, ta yi murmushin mugunta ta gyara masa bed ta feshe d'akin da freshener tana tsaye har yafito daga wanka ya zauna a gefen bed yana mata kallon k'asan ido wani irin abu yakeji yana ratsa jinin jikinsa can! Ya yi gyaran murya daga bisani yace........

Note:- _I'm sorry readers nasan za Ku ce page d'inan yayi kad'an wallahi yau nayi typing mai yawan gaske basan ya akayi ya fita gaba d'aya, ba da kyar na yi wannan a halin yanzu kaina yadau zafi ina cikin yanayi na jiyar zuciya_

Jeeddah Aliyu🌹

[28/11 6:20 pm] Jeeddah Aliyu🌹: ```💝NI DA YAYA HABEEB💝```

_❣ the sweetest love_❣

Na Hauwa Shehu Aliyu🌹

```®NWA```

°°°°```In Dedication```°°°
*To Shehu Aliyu family's*

```80```

~~ke! Bud'e wardrobe ki dauko min fari jallabiya{white colour} yak'arasa magana had'e da lumsashe idanu.
Haleesa ta tabe baki a zuciyarta tace huh...daga farfad'owarsa yafara kirana da suna nan da na tsana, a maimakon ta dauko white colour kamar yadda ya umurceta sai kawai ta dauko mishi black colour, k'i kar6a ya yi yabarta tsaye rik'e da rigar, Haleesa tasake mik'a masa rigar tace yaya Habeeb gashi katashi ka yi sallah lokacin yana k'urewa.
"Ya yi kici-kici da fuska very slowly yafara magana Fari nace ki dauko ba black ba.

"Umhh....fari kace na dauko ni kuma a ganina white da black duk d'aya ne muradi kawai ka suturta jikinka ko...ya kace"?
Tak'ara sa magana tana kallon fuskarsa, saida ya tsotsi bakinshi sannan yafisge rigar daga hannunta daga zaune ya zura rigar yayinda Haleesa ta shinfid'a masa pray mat yana fara sallah tafice daga d'akin a parlour ta tararda madam Hindu da Hannah suna breakfast mom tace kin had'a masa ruwan wanka ne"?
"Eh mom har yafito daga wanka yanzu ma na barshi yana sallah abincinsa zan dauko masa.
Da kyau 'yar albarka haka akeso mace tagari ta kasance, murmushi Haleesa ta yi tanufi kitchen hannunta d'auke da k'aton tray ta tura k'ofa tashiga, yana zauna inda ya yi sallah da sauri yad'ago yarame sosai idanunshi sun k'ara girma fuskarshi ta yi wani fiyau ga wata irin k'asumba da yacika masa fuska.
Tadire tray hannunta ta zauna a gabanshi tana magana tana zuba masa kunun gyad'a kafara da wannan saboda hanjinka ya warware tak'arasa magana had'e da mik'a masa cup ya kafe ta da idanu ko kintawa ba bu Haleesa ta kad'a eye's ball d'inta ta marairaice murya ka daure kasha koda d'an kad'an ne.
Idaunshi a lumshe ya mik'a hannu ya kar6i cup d'in daga hannunta a hankali, yake kur6a kunun har ya shanye  tass...ta kar6i cup ta bud'e food flask k'amshin faten dankalin turawa ya daki hancin Habeeb ya hadiye yawu, ta yi masa serving sai ga gogan naku ya lamshe fate tass....ya ajiye plate yana wani yatsinar fuska Haleesa tace uhmm....ciwonka yana burgeni yaya Habeeb saboda bai hanaka cin jagwalgwalen Haleesa ba tak'arasa magana tana murmushin tsokana.
Habeeb ya daure fuska kema kinsan saboda mom tana gidanan yasa naci abunda ki ka sarafa da hannunki.
"Haleesa ta tabe baki tace uhmm.....yaya Habeeb kenan a wasu lokuta in kana magana kamar da gaske sau ina kama ka kana satar jagwalgwale tak'arasa magana tana dariya.
"Da k'arfi yafisgota tafad'a kansa ya yi mata bak'ar matsa tasaki 'yar k'ara, yadaura bakinshi dai-dai k'ofar kunnenta yace ke! Waye barawo"?
"Ni fa bance maka barawo ba tafad'a cikin rawar murya d'ago fuskarta ya yi yana mata kallon ido cikin ido kasa jurewa ta yi ta sunne fuskarta a k'irjinshi, jikin Habeeb Lamido na 6ari yak'ara rungume ta tsanm....ya daura kanshi bisa wuyanta yana sauke numfashi can! K'asan mak'oshi Haleesa tace ka sakeni kada su mom su shigo su ganmu a haka Allah kunya zan ji tak'arasa magana cikin sigar shagwa6a.
'Maganar tace ta katsiwa Habeeb hamzari da sauri ya yakice ta daga k'irjinshi a kunya ce ya mik'e yanufi gefen gado ya zauna, Haleesa bata k'ara kallonshi ba ta tattrara food flask tafita da su.
Koda ta koma d'akin ta tarar da mom da Hannah na ciki Habeeb ya daura kanshi, akan cinyoyin mom tana shafar gashin kanshi Haleesa tabe baki tanemi kujera da ke cikin d'akin ta zauna cikin sigar rarrashi mom take masa magana _please son ka sanarda ni ainihin abunda yake damunka sanin kanka ne bara ta6a samu peace of mind matuk'ar kana cikin damuwa_
"Idanun Habeeb suna lumshe yace c'mon sweetheart I told you hundred time's ba abunda ke damuna so stop worry yourself.
Madam Hindu ta girgiza kai tace shikenan son, amma Dan Allah ka dinga cin abinci, kuma daga yau na hana peter ya girka abinci da kai ga matarka nan duk abunda ka ke so kafad'a

mata za ta girka ma.
"Sai lokacin ya bud'e idanunshi ya mik'ewa zaune madam Hindu ta juya wurin da Haleesa take zaune tace ni zan tafi Haleesa ki tabbata yana cin abinci sosai ya kuma dinga shan maganinsa in time.
"Haleesa ta gyad'a kai a zuciyarta tace kai wannan matar akwai iya yi hatta da magani tace sai na bashi sai kace k'aramin yaro ae kuwa overdose zan dinga d'irka masa.
Madam Hindu tariga Hannah fita daga d'akin Hannah ta matsa daf da kunnen Haleesa ta rad'a, _yar uwa karki sake ki yi wasa da wannan damar da ki ka samu ba Dr saleem yace cutar ulcer da hawan jini yake damunsa ba ke Kuma ki yi k'ok'ari ki k'ara masa da cutar so_
"A lokacin d'aya suka kyalkyale da dariya had'e da tafawa Habeeb Lamido ya zaro ido a zuciyarsa kai lallai yara nan sun rainani da alama gulma ta ce suke yi ya murtuk'e fuska ya gallawa Hannah harara yace ke wai uban me ki ke jira ne da ba ki tafi ba kin bar mom tana jiranki"?
Hannah ta turo baki tace mom tare take da direbanta, ni kuma da motana nazo.
"Whatever! Habeeb yafad'a a harzuk'a.
Tsabar tsokana irin na Hannah saida tak'ara rad'awa Haleesa _yar uwa kada wannan muzurai da yake yi yabaki tsoro domin hakan zai iya rusa miki plan_
Haleesa ta yi murmushi ita ma ta rad'awa Hannah _don't worry 'yar uwa ke dai ki zuba ido ki sha kallo_
Suka k'ara kwashewa da dariya Hannah tajuya wurin Habeeb tana dariya tace bros ni zan ware sai gobe in nazo shan farfesu.
Tsaki Habeeb ya ja yace wannan kuma matsalarki ce munafuka kawai.
Hannah ta dube Haleesa ta yi mata signal karaf akan idon Habeeb, sai kawai ya ga Haleesa ta tintsire da dariya Hannah ta bud'e k'ofa tafice.
"Habeeb ya d'aure fuska yana kallon Haleesa a d'age yayinda ita kuma ta sadda kanta k'asa, tsawon dak'ik'a uku ta dauka kanta na sunkuye daga bisani tad'ago ta sace kallon Habeeb idanunshi na kafe akanta, batasan lokacin da tasake masa murmushi ba. harara ya galla mata yace ke zo nan
Saida anta cikinta ta kad'a ta dake kamar bata tsorata ba ta mik'e a sanyaye tanufi wurinshi Saida yak'are mata kallon wulaqancin yace jikina yabani cewa wannan rad'e-rade da Ku ke yi da ni Ku ke don haka fad'a min abunda Ku ke cewa"?
"Haleesa ta rusa yar da kai ya za'ayi yaya Habeeb kana zaune mu yi gulmarka"?
Karaf yarik'en mata hannu ya shiga murza yatsunta da k'arfi, Haleesa tafasa ihu _wayyo yatsuna Yaya Habeeb karka yi min targad'e_
Saida yagaji don kanshi yasaketa, ta koma gefe tana 'yarfe hannu a zuciyarta tace mugu kawai nan take ta tuna da bai sha maganinsa ba ta yi murmushin muguntа tace nima anan zan rama yanzu nan za ka ga kalar nawa mugunta.
Tajuya ta dube shi ta ga har yanzu ita yake kallo ta turo baki tanufi bedside tadauko ledar magunguna sa, robar ruwa da cup tadauko ta ajiye bisa dressing mirror tasoma 6alle tablets saida ta cika hannunta duk abunda ta ke yi Habeeb ya kafenta da ido murgud'a masa baki ta yi ta mik'a masa hannunta karaf ya d'anke hannunta tace kai bawan Allah magani za ka kar6a ba hannuna ba.
"Yatsine fuska ya yi Can! K'asan mak'oshi ya furta kina nufi ni zan sha wannan tulin

magani"?
Kwarai kuwa ko bara ka sha bane na kira mom a waya
Tsaki ya ja yace amma dai kinsan banason magani koh"?
Ta tabe baki tace oho...ni bansaniba cike da jin haushi ya mik'a mata hannu ta bashi maganin kamar zai fashe da kuka yace duk tulin magani nan ace ni kadai zan shanye shi, sai kace d'an kwaya.
Saura kiris Haleesa ta tintsire dariya sai kawai ta hadiye abarta Habeeb ya runtsi idanunshi da kyar ya shanye maganin yayinda Haleesa take aikin kallonshi saboda yatuna mata da marigayi yaya Habeeb shima haka yake Sam bayason magani duk lokacin da bashida lafiya sai tasha artabo da shi kafin yasha magani.
"A zuciyarta tace huh....kenan duk mai suna Habeeb bayaso magani batasan cewa maganar da tayi yafito fili ba.
Tsananin kishinta ya lullu6e Habeeb cikin zafin rai ya wanka mata raguwar ruwan da yasha magani.
A tsorace Haleesa tad'ago tana kallonshi yayinda shima ya kafenta da idanunshi da ke baiyanar da b'acin ranshi a fili.
Nan take wani tunani yafad'owa haleesa sai kawai ta hadiye b'acin ranta, ta mik'a hannunta ta d'auki robar ruwa kamar za ta sha ta balle murfi ta kwara masa a jiki ta balla da gudu ta nufi k'ofar fita har tafita ta d'an lek'o kanta ta yi masa gwalo tasaki k'ofa ta kwasa da gudu tashige part d'inta direct ta wuce bedroom tafad'a bisa bed tad'auki pillow ta manna a k'irjinta wani irin nishad'i, takeji Wanda rabonta da ta tsince kanta cikinsa tun yaya Habeeb d'inta yana raye ta runtse idanuta fuskar Habeeb Lamido ke mata gizo.
Ta6angare Habeeb kuma Haleesa na ficewa ya tsurawa k'ofa ido daga bisani ya sulale ya kwanta rabin jikinsa na bisa bed yayinda k'afafunsa ke k'asa wani irin tafiyar tsotsa yakeji a jininsa, sai kawai ya afka tunani yafara aikawa kansa tambaya batada amsa.
_me yasa lokacin da yarinya nan ta yi zancen marigayin sarauyinta naji mashahurin kishinta ya turnuke ni"?_
Ya mik'e zauna wani 6angare na zuciyarsa yace hakan yana da nasaba da tsananin sha'awarta da ka ke yi ya tabe baki had'e da mik'ewa yacire rigar jikinsa Yana tunanin in ya kama Haleesa irin hukuncin da zai yi mata.
*************************
_8:30pm_
Habeeb yana zaune a falonshi ya kafe akwatin talabijin da ido Haleesa ta yi sallama sai kawai ta ja ta yi tsaye cikin tsokana tace _yaya Habeeb in shigo ko in koma inda na fito"?_
Murmushi Habeeb ya yi had'e da shafa sajen shi, ya ja iska wani irin dad'i ya ziyarcenshi jin yake yi tamkar yana yawo a sararin samaniya, amma tsabar zafin kanshi ba zai barshi ya baiyanar da jin dad'i nasa ba.
"Ya yatsine fuska yace duk yadda ki ka za6a.
Haleesa ta mak'e kafad'a tak'arasa shiga falon a fakace yak'are mata sanya take cikin lemon green colour gown iya guiwanta ta yane kanta da d'an k'aramin white colour veil fuskarta tasha light make-up matsananciyar sha'awarta ta lullu6enshi har ta haddasa masa kasala yasauke zazzafar ajiyar.
Kaitsaye ta zauna bisa hannun kujerar da yake zaune, k'amshin turarenta ya baibaye shi ya

tsincin kanshi cikin wani hali Wanda a tarihin rayuwarsa bai ta6a riskar kansa a ciki ba.
Kafin yadawo daga duniyar tunani muryar Haleesa ta daki dodon kunnenshi _yaya Habeeb your food is ready_
Habeeb ya tabe baki yana mamaki me Haleesa take nufi da wannan sabon salo da ta zo mishi da shi ta na nufi za ta ja ra'ayinsa ne yafara sonta"?
Ya yi murmushi yad'ago kanshi sama yadda zai hango fuskarta yana mata duba mai cike da sha'awa, yace ki je ki juyewa Rahul da Rita ni na k'oshi.
Haleesa batasan time d'in da ta galla masa harara ba ta murgud'a baki.
yadda ta murgud'a baki ta yi mugun bashi dariya sai kawai ya basar, yad'age gira sama yana mai cigaba da kallonta.
"Haleesa ta narke murya tace haba! Yaya Habeeb karka yi mun haka mana karka manta mom tace na kula da cin abincinka yanzu dai ka yi hak'uri katashi mu je ka cin abinci kaji"?
